KWAMACALA A RUBUTUN HAUSA: NAZARI A KAN RUBUTUN LITTATTAFAI DA JARIDU DA MUJALLU DA ALLUNAN TALLA DA ABUBUWAN HAWA

NA

HASSAN RABEH

MA/ARTS/2536/2009-2010

A THESIS SUBMITTED TO THE POSTGRADUATE SCHOOL, AHMADU BELLO UNIVERSITY, ZARIA – NIGERIA

IN PARTIAL FULFILMENT OF THE REQUIREMENT FOR THE AWARD OF MASTER OF ARTS DEGREE IN AFRICAN LANGUAGES (HAUSA)

DEPARTMENT OF AFRICAN LANGUAGES AND CULTURES AHMADU BELLO UNIVERSITY, ZARIA-NIGERIA

FEBRUARY, 2014

DEDICATION

This research is dedicated to my late mother, my father, family, tutors and to humanity.

DECLARATION

I hereby declare that this Thesis entitled “Kwamacala A Rubutun Hausa: Nazari A Kan Rubutun Littattafai da Jaridu da Mujallu da Allunan Talla da Abubuwan Hawa ” is written by me and it is a record of my own research work and that it has not been presented in any previous application for a higher degree. All quotations and sources are dully referenced and specifically acknowledged.

_____ _____

HASSAN RABEH DATE

CERTIFICATION

This Thesis entitled "Kwamacala A Rubutun Hausa: Nazari A Kan Rubutun Littattafai da Jaridu da Mujallu da Allunan Talla da Abubuwan Hawa " by Hassan Rabeh, meets the regulation governing the award of the degree of Master of Arts (M.A.) in African Language (Hausa) of Ahmadu Bello University, Zaria – Nigeria and is approved for its contribution to knowledge and literature.

_____ _____

Dr. Magaji Tsoho Yakawada Date
Chairman Supervisory Committee

_____ _____

Prof. Munnir Mamman Date
Member Supervisory Committee

_____ _____

Dr. Balarabe Abdullahi Date
Head of Department

_____ _____

Prof. A. A. Joshua Date
Dean School of Postgraduate Studies

GODIYA

Godiya ta tabbata ga Allah (maxaukakin sarki) wanda ya fifita xan'adam da ilimi, da hikima da basira. Allah ya qara yin salati ga fiyayyen halitta, Annabi Muhammad (S.A.W.) wanda Allah ya aiko da addini na gaskiya,

Ina miqa godiya ta musamman ga jagororin wannan aiki wato Dr Magaji Tsoho Yakawada da Professor Munnir Mamman waxanda da taimakonsu da kuma shawarwarinsu ne wannan aiki ya kawo matsayin da yake a yanzu. Ina qara jinjina masu da irin haquri da juriya da suka yi da ni, duk kuwa da irin raunina.

Haka nan ina miqa godiya ga Shugaban Sashen Nazarin Harsuna da Al'adun Afirka na wannan jami'a wato Dr. Balarabe Abdullahi, da shugaban Tsangayar Fasaha na wannan jami'a wato Professor Muhammad Lawal Amin, da Professor M.A.Z. Sani na Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya na Jami'ar Bayero da ke Kano da kuma Professor Xalhatu Muhammad.

Bayan waxannan, akwai shahararrun masana da suka taimaka qwarai kamar Professor Halliru Amfani da Dr. Bello S.Y. Al-Hassan da Professor M.A. Umar da Malam Adamu Ibrahim Malumfashi da Malam Abubakar Sarki Muhammad da Malam Sani Usman da Malam Shu'aibu Abdulmumin da Dr. Salisu Garba Kargi da Malam Rabi'u Tahir da Dr. Aliyu Busa da Malama Halima Kabir Daura. Haka nan ban manta da irin gudummuwar da na samu daga abokan karatuna ba irinsu Abubakar Ayuba da Suleman Ladan da Abdulqadir Abubakar Zailani da Rabi'u Bashir da Musa Tela da Maikudi Umar.

Godiya ta musamman ga Malam Ibrahim Ammani Baban Yara na Asibitin Qwararri ta Jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya da Malam Sani Hassan da Malam A.Y. Darma da Malam B.M. Gafai da Malam Babangida Hamza dukkansu a

Sashen Nazarin Harshen Hausa na Kwalejin Ilimi ta Isa Kaita da ke Dutsin-ma don irin gudummuwarsu. Haka kuma ban manta da gudummuwar da Malam Yusuf Mu'azu Ibrahim and Malam Yakubu Muhammed Saulawa da Munnir Garba da Mahmud Garba suka bayar ba ta shawarwari da kalamai masu qara qwarin gwiwa.

Dole ne in miqa godiya maras adadi ga iyayena waxanda suka yi xawainiya da ni tun ina qarami har na zama mutum. Haka nan godiya ta musamman ga dukkan 'yan'uwana da iyalina. Musamman maixakina don irin haquri da juriya da gagarumar gudummuwar da suka ba ni a lokacin da nike wannan karatu. Allah ya saka wa kowa da alherinsa.

QUNSHIYA

Title Page		i
Dedication		ii
Declaration		iii
Certification		iv
Acknowledgement		v
Qunshiya		vii
Tsakure		x
	BABI NA XAYA: GABATARWA	
1.0	Gabatarwa	1
1.2	Manufar Bincike	1
1.3	Dalilin Bincike	1
1.4	Muhimmancin Bincike	2
1.5	Hanyoyin Gudanar da Bincike	2
1.6	Farfajiyar Bincike	3
1.7	Hasashen Bincike	4
1.8	Naxewa	4
	BABI NA BIYU: BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA	
2.0	Gabatarwa	5
2.1	Bitar Ayyukan da Suka Gabata	5
	2.1.1 Litattafai	5
	2.1.2 Kundayen Bincike	10
	2.1.3 Muqalu	14
2.2	Naxewa	24
	BABI NA UKU: SAMUWAR RUBUTUN HAUSA	
3.0	Gabatarwa	25
3.1	Rubutun Boko	26

3.1.1 Nasarar da Rubutun Boko ya Samu 29
3.1.2 Daidaita Qa'idojin Rubutu na Hausa 30
3.2 Samuwar Qa'idojin Rubutun Hausa 36
3.3 Ci gaban da Rubutun Hausa ya Samu 37
3.4 Ma'anar Rubutu 39
3.5 Muhimmancin Rubutu 40
3.6 Ma'anar Qa'idojin Rubutu 41
3.7 Muhimmancin Qa'dojin Rubutun Hausa 41
3.8 Samuwar Jaridu da Mujallu a Qasar Hausa 43
3.8.1 Jaridu 43
3.8.2 Bunqasar Jaridu da Mujallu a Arewacin Nijeriya 46
3.8.3 Mujallu 46
3.9 Allunan Tallace-tallace (Billboards) 48
3.9.1 Ire-Iren Allunan Tallace-tallace 49
3.9.2 Muhimmancin Allunan Tallace-tallace 50
3.10 Naxewa 51

BABI NA HUXU: YANAYIN KWAMACALA A RUBUTUN HAUSA

4.0 Gabatarwa 52
4.1 Littattafai 55
4.2 Jaridu da Mujallu 61
4.2.1 Haxa Kalmomi 61
4.2.2 Raba Kalmomi 70
4.2.3 Rubuta Kalmomi 89
4.2.4 Alamomin da Ake Amfani da su a Rubutu 94
4.3 Allunan Talla 105
4.4 Abubuwan Hawa 108
4.5 Sauran Rubuce-rubuce 109

4.6 Naxewa 109

BABI NA BIYAR: DALILAN KWAMACALA DA MATAKAN GYARA

5.0 Gabatarwa 110

5.1 Abubuwan da Bincike ya Gano 110

5.2 Matakan Gyara 113

5.3 Matsalolin da Rubutun Hausa Yake Fuskanta 114

5.4 Matakan Inganta Rubutun Hausa 116

5.5 Naxewa 118

BABI NA SHIDA: KAMMALAWA DA SHAWARWARI

6.0 Gabatarwa 119

6.1 Kammalawa 120

6.2 Naxewa 121

6.3 Shawarwari 121

Manazarta 124

Tsakure

Ganin halin da rubutun Hausa yake ciki na ci gaba da qara bunqasa a wannan lokaci da kuma irin kwamacalar da ake samu wajen amfani da shi, musamman a jaridu da mujallu da allunan talla da ma littattafai da sauran fannoni na rayuwa, ya sanya wannan bincike ya yi nazarin wannan al'amari da nufin fito da irin matsalolin da ake fuskanta a yayin gudanar da rubutuun Hausa.

Su kuwa waxancan hanyoyin samar da bayanai da aka yi nazarin su, sun zama abubuwa ne da ake amfani da su a yau da kullum, musamman ga waxanda suka samu damar yin ilimin karatu da rubutu na boko. Don haka ne wannan bincike ya waiwayi yadda ake amfani da rubutun Hausa a cikinsu da irin kurakuran da ake samu a yayin yin rubutu.

BABI NA XAYA

GABATARWA

1.0 Gabatarwa

An daxe ana gabatar da nazari a kan jaridu da mujallun Hausa kama tun daga tarihin samuwarsu da yadda suke amfani da harshe a fagen sadarwa da irin salon da suke amfani da shi da muhimmancinsu ga al'umma da ire-irensu ta fuskar bayanan da suke qunshe da su,

Dalilin gudanar da wannan bincike shi ne domin sanin halin da rubutun Hausa yake a cikin littattafai da jaridu da mujallu da allunan talla da jikin abubuwan hawa da ma sauran wurare da ake amfani da shi, tare da yin nazarin irin matsalolin da ake fuskanta a fagen rubutu a waxannan kafafen ilmantarwa da wayar da kan al'umma.

1.2 Manufar Bincike

Manufar wannan bincike ita ce, yin zuzzurfan bincike a kan yadda jaridu da mujallu da allunan talla suke gudanar da rubutun Hausa, musamman ta amfani da qa'idojinsa, kuma an yi nazarin irin kurakuran da ake samu a yayin rubuce-rubucen tare kuma da gano hanyoyin da za a kauce musu da kuma bayar da shawarwarin yadda za a inganta rubutun Hausa.

1.3 Dalilin Bincike

Ganin irin muhimmancin da rubutu yake da shi da kuma dangantakar da ke tsakanin rubutu da kafafen isar da saqo na jaridu da mujallu da allunan talla ya sa wannan bincike ya yi nazarin irin yadda ake gabatar da rubutuna waxannan kafafe da nufin gano ire-iren matsalolin da ake samu.

1.4 Muhimmancin Bincike

Babban muhimmancin wannan bincike shi ne taimaka wa masu amfani da rubutun Hausa domin samun isar da saqo cikin sauqi ba tare da sauyawa ko salwantar ma'ana ba. Akwai fannoni da dama da ake amfani da rubutun Hausa; ta fuskar ilimi zai taimaka wajen fahimtar irin kurakuran da ake samu a yayin gudanar da rubutun Hausa. Haka nan zai taimaka wajen fahimtar da al'uma cewar ba duk mai iya karatu da rubutu ba ne zai iya rubutu da Hausa a bias qa'idojinta, don haka akwai buqatar samun ilimin qa'idojin rubutu na Hausa. Haka nan zai taimaka wa kamfanoni masu yin tallace-tallace a rubuce su fahimci cewar suna kasha maqudan guxaxe ta wannan fuskar, amma kwalliya bat a biyan kuxin sabulu domin kuwa a mafi yawanci lokuta ba saqon da suke son a isar ake isarwa ba, a wani lokaci ma babu ma'ana ga abin da ake rubutawar. Irin wannan matsala tana faruwa a tallar da ake yi a jaridu da mujallu da kuma allunan talla.

1.5 Hanyoyin Gudanar da Bincike

Yayin gudanar da wannan bincike an karanta jaridu da mujallu da nazarin allunan talla da rubuce-rubuce a jikin abubuwan hawa, musamman motocin haya da nufin zaqulo kurakuran da ake samu. Don haka akwai buqatar a kalle su, a xaixaikunsu. Saboda haka hanyoyin da aka bi wajen gudanar da wannan bincike sun haxa da:

Karanta littattafai, musamman masu magana a kan qa'idojin rubutu na Hausa da jaridu da mujallu, don yin nazarin yadda ake gudanar da rubutun Hausa a cikinsu. An kuma yi nazarin kundayen binciken digiri na biyu da na uku da aka gudanar a kan rubutun Hausa ko a kan littattafai da jaridu da mujallun Hausa don samun qarin haske a kan hanyoyin da aka gudanar da wannan bincike. An kuma gana da masana da editoci da 'yan jarida da masu karanta jarida da karanta littattafai da suka danganci rubutun Hausa da masu bayanai a kan jaridu da

mujallu. Sannan kuma an karanta kuma aka juyi wuraren da aka yi kurakurai don nazartar su.

Haka kuma an ziyarci xakunan karatu na jami'o'i, musamman na jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya da jami'ar Bayero da ke Kano da jami'ar Usmanu Xanfodiyo da ke Sakkwato da kuma jami'ar Umaru Musa 'Yar'aduwa da ke Katsina domin yin nazarin bayanai da suka shafi qa'idojin rubutu na Hausa da kuma yadda ake amfani da su a rubuce-rubuce na yau da kullum.

1.6 Farfajiyar Bincike

Wannan bincike ya gano ire-iren matsalolin da ake samu a rubuce-rubucen da ake yi a cikin littattafai da jaridu da mujallu da allunan talla da jikin abubuwan hawa da sauran hanyoyin sanarwa a rubuce. Ta vangaren jaridu aikin ya yi nazarin Jaridar Gamzaki da Jaridar Leadership Hausa da At-tatbiq da Aminiya da Gaskiya Ta Fi Kwabo da kuma Jaridar Rariya. A vangaren mujallu an yi nazarin Mujallar Fim da Xakin Kara da Mujallar Gani da Ido (Maganin Tambaya) da Mujallar Kulawa da Mujallar Magama da Kunnen Gari, (in ka ji, kowa ya ji) da Mujallar Sautus Sunnah da kuma Muryar Arewa,

Haka nan binciken ya yi nazari a kan rubutu na Hausa a yau; yadda suke da yadda ake gabatar da su. Haka nan wannan aiki bai taqaita ga wani vangare na qasar Hausa ba, musamman ganin abubuwan hawan da aka yi nazari suna yin zurga-zurgarsu ne a duk faxin garuruwan qasar Hausa.

Aikin kuma ya yi nazarin rubutun Hausa a kan tituna, wato yadda ake amfani da shi don yin sanarwa ko gargaxi ko tallace-tallace a jikin bangaye ko qananan allunan talla ko na sanarwa (sign boards)

1.7 Hasashen Bincike

Hasashen wannan bincike dai shi ne dalilan da suke haddasa kwamacala a rubutun Hausa guda biyu ne; na farko shi ne take sani, musamman inda ake samun masu ilimi suna yin rubutun Hausa ba bisa qa'ida ba. Wannan ba ya rasa nasaba da halin Bahaushe na 'shakulatin vangaro' wato ko in kula ga abin da ya wajaba a yi wato dai an wallafa littafi don wata manufa, amma an qi kulawa tare da tabbatar da an cim ma wannan manufar. Wannan ne yakan sanya a samu kura-kurai a cikin litattafai da aka wallafa su don su zama jagora ga mai rubutun Hausa, watoya zama mai dokar barci yana gyangyaxi.

Dalili na biyu kuwa shi ne na rashin sani a game da rubutun Hausa bare kuma qa'idojinsa. Irin wannan matsala ita ce ta fi shafar masu rubuce-rubuce a jikin abubuwan hawa da katin gayyata da sanarwa ko gargaxi da ake samu a wurare daban-daban. Buqatar irin waxannan marubuta dai ita ce ta isar da saqon da ake tunanin an isar ko ta halin qaqa.

1.8 Naxewa

Wannan bincike ya mayar da hankali ne a kan kwamacalar da ake samu a rubutun Hausa a littattafai, musamman masu bayani a kan qa'idojin rubutu da jaridu da mujallu da jikin abubuwan hawa, musamman motocin haya da allunan talla da sauransu da nufin zaqulo irin kurakuran da ake samu da kuma yin cikakken tsokaci a kan kowace qa'ida aka kawo da abin da ya faru har ake ganin an sava wa waxannan qa'idoji.

BABI NA BIYU

BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA

2.0 Gabatarwa

Wannan babi ya yi bitar ayyukan da suka gabata ne a fagen nazarin qa'idojin rubutu na Hausa dangane da abin da ya shafi jaridu da mujallu da allunan talla da kuma abubuwan hawa, domin kuwa masana da dama sun gudanar da bincike da rubuce-rubuce a fagen nazarin qa'idojin rubutun Hausa da kuma abin da ya shafi jaridu da mujallun Hausa da sauran fannoni daban-daban na rayuwar al'umma.

2.1 Bitar Ayyukan da Suka Gabata

A nan an yi bitar ayyukan da suka gabata inda aka rarraba su zuwa littattafai da kundayen bincike da kuma muqalu.

2.1.1 Litattafai

Bargery (1934) ya yi taqaitaccen bayani ne a kan wani cigaba da aka samu a wancan lokacin wanda a kansa ne ya gina littafin nasa. Daga ciki akwai daina yin xigo a qarqashin haruffan **b** da **d** da **k** za a riqa yin waqafi a saman waxannan haruffa (**d' d'** da **k'**) da daina amfani da **ch** sai **c**, sannan **ts** da **sh** za a bar su haka nan, amma a wajen maimaicin su za su zamo **tts** da **ssh.**

Haka nan babu nuna tsawon wasali ko hawa da saukar murya, sannan kuma babu bambance **r** (ra-gare da ra buge) wato r ta kalmar ga**r**dama da ta cikin **r**aqumi. Babu bambancin **n** ta hanqa da ta ganxa da ta hanxa a yayin rubutu na yau da kullum, misali ga**n**ya da ha**n**ta da ga**n**ga. Wannan ya taimaka wajen bin diddigin tarihin rubutun Hausa da irin ci gaban da aka samu tun a wancan lokacin, duk da yake dai aikin bai tavo wani abu game da rubutun Hausa a jarida ko mujalla ba..

Galadanci (1976) ya bayyana wasu daga cikin qa'idojin rubutu na Hausa. Marubucin ya fara bayaninsa tun daga yadda ake rubuta manya da qananan baqaqen Hausa da yadda harafin **p** kan kasance da muhallin harafin **m** da **n** a tsakiyar kalmomin Hausa da yadda ake rubuta maimaicin tagwayen haruffa.

Ya kuma kalli yadda ake rarraba kalmomi a rubutu, musamman kalmomi masu gava xaixai. Haka ma ya bayyana yadda ake rubuta mallaka da wakilan sunaye. A babi na goma ya tavo qa'idojin rubutun Hausa, a sauran babin littafin ya fi mayar da hankali ne a kan nahawun Hausa. Littafin nasa ya zama ma'aunin da aka yi amfani da shi a yayin nazarin rubutu a jaridu da mujallu da allunan talla da ma abubuwan hawa, musamman motoci wanda shi ne maqasudin wannan aiki. Galadanci (1976) bai yi wani tsokaci a kan jaridu ko mujallu ba bare ma ya danganta yadda suke amfani da qa'idojin rubutu ba kamar yadda wannan aiki ya yi.

Shi kuwa Yahaya (1988) ya yi cikakken bayanin tarihin samuwar rubutu a harshen Hausa ne tun daga samuwar rubutun ajami har zuwa rubutun boko. Ya kasa aikin nasa zuwa kashi 12.

A kashi na 9 da na 10 ne marubucin ya tavo abin da ya shafi wannan aikin kai tsaye inda a kashi na 9 ya kawo bayani a kan daidaita qa'idojin rubutun boko, sannan ya yi bayanin Hausar cikin littattafai kafin qarni na 20 da kuma bayan nan. Haka ma ya bayyana kafa Hukumar Hausa da taron daidaita qa'idojin rubutun Hausa. A kashi na 10 kuma ya bayyana samuwar jaridun Hausa na farko da na lokacin NORLA da kuma bayan NORLA har zuwa yau. A dukkan qoqarin da wannan aiki ya yi bai kalli kwamacala a wata jarida ko mujalla ba kamar yadda wannan aiki ya yi.

Bunza (1990) kuwa ya mayar da hankali ne a kan qa'idojin rubutun Hausa. Ya kawo muhallin baqaqe da wasulla a rubutun Hausa. Kuma sai ya yi bayanin

raba kalma a cikin rubutu da muhallan da ake raba kalma a yayin rubutu. Ya bayyana muhallan da ake haxa kalma, sai ya yi bayanin dangantakar nahawu da rubutu tare da bayanin muhimmancin qa'idojin rubutu ga ma'anar kalmomi da kuma muhimmancinsa ga li'irabin Hausa. Babban bambancin da ke akwai a tsakanin wannan aiki da na Bunza shi ne wannan aikin yana qoqarin bin waxancan qa'idojin rubutu ne tare da nuna yadda ake sava masu a jaridu da kuma mujallu da allunann talla.

Daga cikin batutuwan da Newman (2000) ya gabatar akwai bayanin rubutun boko da yadda ake raba kalmomi da ma yadda ake rubuta su (spelling rules) da muhallan da ake amfani da manyan haruffa. Haka kuma ya yi bayani kan rubutun ajami da haruffansa, sannan ya kawo wasu rubuce-rubuce da aka samu a cikin ajami tare kuma da juye su zuwa rubutun boko. Marubucin bai yi wani tsokaci kan kwamacala a rubutun Hausa ba.

Jaggar (2001) ya kawo bayani a kan tsarin rubutun Hausa inda ya fara kawo tarihin samuwar rubutun jami tun a cikin qarni na sha huxu. Sannan ya kawo bayanin samuwar rubutun boko a farkon shekarun alif xari tara (1900s), tare da kawo abjadin rubutun boko da kuma bayanin haruffa masu qugiya (v,x,q). Shi ma dai kamar Newman ya kawo wasu rubuce-rubuce da aka samu a cikin ajami tare kuma da fassara su da rubutun boko. Jaggar bai kalli sauran qa'idojin rubutu ba bare ma ya danganta yadda ake amfani da su a wasu littattafai ko jaridu ko mujallu ba.

Bunza (2002) ya kawo asalin rubutu ne tun daga Mesopotamia da Misira da cewa rubutu ya samo asali ne daga zane-zane da alamomi da aka yi domin bayar da bayani a kan wani abu da ake son a sanar ga al'umma. A qasar Hausa kuwa Bunza ya yi qoqarin danganta asalin rubutu tun daga tsaga da tun fil'azal aka san al'ummar Hausawa da ita domin kuwa ita ma zane ce da akan yi wa mutum don nuna asali ko dangin da ya fito daga ciki. Haka nan ya qara qarfafa bayaninsa da

irin zane-zane da ake yi a jikin layu da kambu ko qiri. Haka nan ya bayyana wani abin dubawa a nazarin asalin rubutu a qasar Hausa inda ya bayyana yadda ake zanen suna a qasar Hausa, ya ce akan taru a muhallin zanen sunan bayan an yi shaye-shaye da raye-raye sai dattijai su zo da kararen rama vararru guda bakwai. Za a yi zane-zane da tsinke na wuta a kan kowanen su don ya fito sosai. Waxannan karare ne za a kai wa mai jego ta zavi guda. Akan mayar wa da tsofaffi karan da ta xauka su kuma su yi la'akari da shi ta lura da zanen da yake a jikinsa domin faxar sunan abin da aka haifa. Wannan shi ne asalin abin da ake ce wa zanen suna a qasar Hausa.

Akwai ma zane-zane irin na masu sana'o'in gargajiya kamar masassaqa da maqera da 'yan qorai (masu sana'ar qwarya), waxanda ya nuna cewa bisa ga asali waxannan zane-zane ba wai don kwalliya kawai ake yin su ba, su ma suna da ma'anoninsu, don haka su ma abin la'akari ne a wajen nazarin asalin rubutu a qasar Hausa, domin kuwa sauran al'ummomin da suka gabata da ire-iren waxannan zane-zane ake danganta asalin rubutunsu.

Amma rubutu kamar yadda aka san shi a yau bai samu a qasar Hausa ba sai bayan zuwan Musulunci daga baya kuma Turawan mulki, inda aka samu asalin rubutun ajami da kuma rubutun boko, waxanda suka samu ta dalilin salailan rubutun Larabci da kuma na Romawa. Duk da wannan qoqari na bin asalin rubutu da Bunza ya yi bai kalli wani abu da ya shafi irin kwamacalar da ake samu a rubutun Hausa ba.

Sa'id (2004) ya kalli wasu muhimman vangarori ne na qa'idojin rubutun Hausa inda ya yi waiwaye a kan lokacin da aka fara yunqurin samun ingantacciyar hanyar rubuta Hausa, saboda muhimmancinta a wajen wallafe-wallafe. Marubucin ya yi waiwayen shekarar 1932 wato lokacin da Bergery yake qoqarin rubuta qamusun farko na Hausa.

Haka nan, ya yi bayani kan kwamitin da aka kafa a shekarar 1951 don inganta rubutun Hausa. Kwamitin ya duqufa wajen ganin an samu amintacciyar hanyar rubuta Hausa, inda ya yi bitar qa'idojin rubutu, sannan aka kuma cim ma matsaya gamsasshiya a game da su. An sake zaunawa don duba qa'idojin rubutun Hausa a shekarar 1972, a nan ne aka sake daidaita wasu matsalolin da suka taso. A shekarar 1980 ma an yi wani zama a wurare biyu, wato a Jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya da kuma a Yamai ta Jamhuriyar Nijar, duka dai da nufin samun sahihiyar kuma amintacciyar hanyar rubuta Hausa. Babbar nasarar da wannan zama ya samu ita ce ba a samu wani savani ba.

Ya yi bayani a kan baqaqen Hausa da yadda ake sarrafa su da kuma yadda ake rubuta wasu kalmomi na musamman da wurin da aka fi samun matsala a rubutun Hausa wato wurin da ake raba kalamomi da wurin da ake haxe su. Sannan kuma sai aka yi bayanin muhallin manyan baqaqe. A qarshe ya yi bayani kan alamomin ajiye magana, wato alamomin da ake amfani da su a yayin rubutu. Irin waxancan qa'idoji da alamomi ne wannan aiki yake qoqarin ganin yadda ake amfani da su a jarida ko wata mujalla ko allunan talla.

Wurma (2005) ya kawo muhimmancin harshen Hausa da cigabansa da ma'anar daidaitacciyar Hausa da wuraren da ake amfani da ita waxanda suka haxa da kafofin watsa labarai irin su radiyo da talabijin da jaridu da mujallu da sauran hanyoyin sadarwa (da suka haxa da allunan tallace-tallace da na sanarwa)

Ya yi tsokaci a kan karin harshe da daidaitacciyar Hausa da bambancin daidaitacciyar Hausa da sauran kare-karen Hausa. Ya kuma yi bayanin abubuwan da suka shafi qa'idojin rubutun Hausa tun daga baqaqen Hausa da yadda ake amfani da su a daidaitacciyar Hausa da wasullan Hausa da kalmomin jama'u da alamomin da ake amfani da su a rubutun Hausa waxanda suka haxa da aya da tagwayen aya da alamar motsin rai.

Haka nan ya tavo muhallan da ake amfani da manyan baqaqe da yadda ake rubuta kanun magana da yadda ake rubuta kalmomin bayanau da zagi da mahaxi da na motsin rai. Ya kuma riqa yin bayaninsa tare da kawo misalan wuraren da aka samu matsalar rubutu a wasu daga cikin littattafan Hausa kamar su Magana Jari Ce. Abin sha'awa a game da littafin na Wurma shi ne ya tavo vangarori da dama na qa'idojin rubutun Hausa. Duk da faxin da'irar da wannan littafi ya tavo, bai tavo kwamacalar rubutun Hausa a jaridu ko mujallun Hausa ba. Sai dai an yi qoqarin danganta abubuwan da Wurma ya bayyana a littafinsa da yadda ake amfani da su a jaridu da mujallu na Hausa.

Ado da Rabeh (2008) sun kawo kaxan daga cikin tarihin samuwar rubutun Hausa tun daga na ajami har zuwa na boko. Kashi na farko na littafin ya qunshi qa'idojin rubutun Hausa ne da suka shafi yadda ake rubuta kalmomi, wato wuraren da ake haxe kalmomi da inda ake raba su da amfani da manyan haruffa da haruffan da ba a amfani da su a rubutun Hausa da tagwayen haruffa da dai sauran hanyoyin da ake rubuta kalmomin Hausa.

Kashi na biyu kuwa yana xauke ne da alamomin da ake amfani da su a rubutu waxanda suka haxa da aya da waqafi da waqafi mai ruwa da sauran alamomin rubutu. Haka nan sun yi bayanin sakin layi da yadda ake yin shi a cikin rubutu. Shi ma wannan aiki bai danganta qa'idojin rubutu da wata kafa ta isar da saqo irin su jaridu da mujallu ba. Haka nan aikin bai kalli yadda ake kwamacala a rubutun Hausa a wata kafar isar da saqo a rubuce ba kamar yadda ake son yi a wannan aiki. Sai dai aikin nasu zai iya zama madogara da za a yi amfani da ita don nazarin qa'idojin rubutu a waxanan kafafen sadarwa.

2.1.2 Kundayen Bincike

Dyson (1973) ya bayyana babban dalilin gudanar da bincikensa da cewar shi ne gano dangantakar da ke tsakanin furucin kalmomin Hausa da yadda ake rubuta

su. Binciken nasa ya mayar da hankali ne a kan yadda kalmomin Hausa a rubuce suke wakiltar abin da aka furta. Wannan aiki dai bai da alaqa da wasu qa'dojin rubutu bare ma har ya kalle su ta fuskar rubutu a jaridu ko mujallu.

Zahra (1986) ta yi nazarin Jaridun Hausa Havakarsu da Gudunmawarsu Kan Harshe da Al'adun Hausawa. Ta yi bayani a kan hanyoyin sadarwa na gargajiya da na zamani da kuma ire-iren sadarwa kamar ta magana da isharori. A babi na biyu ne ta yi bayani a kan tarihin rubutun Hausa da ajami da kuma samuwar rubutun boko. Babi na uku yana bayani ne kan dalilin samuwar jaridun Hausa, sai babi na huxu da ke bayani a kan tsarin jaridun Hausa.

Babi na biyar na bayani ne a kan salon sarrafa Hausa a jaridu, babi na shida na bayani kan gudummawar jaridun wajen havaka tarihi da inganta addinin Musulunci da havaka siyasa da kasuwanci. Babi na bakwai na bayani ne a kan ra'ayoyin mutane game da jaridu, sai kuma qarshen babi na takwas wadda yana bayanin kammalawa.

Babban dalilin da ya sa aka yi wannan bincike shi ne ganin yadda Hausawa suka karvi jaridun Hausa hannu bibbiyu, kullum suna rububin su saye su. Sai dai Zahra ba ta yi wani nazari a game da halin da rubutun Hausa yake ciki a jaridu da mujallun Hausa ba.

Musa (1988) ya bayyana samuwar radiyo da talabijin a qasar Hausa. Aikin ya yi qoqarin yin bincike kan tarihin samuwar kowanne xaya daga cikinsu, tare da yin nazari kan ire-iren shirye-shiryen da suke tsarawa kuma su gabatar kan al'adun gargajiya na Hausawa. Binciken ya cigaba da bayyana yadda kafofin watsa labarai na zamani sukan taimaka wajen fito da al'adun gargajiya.

Wannan aiki nasa ba wai ya kalli kafofin watsa labarai ba ne ta fuskar rubutu, kamar yadda wannan aiki yake qoqarin yi, kuma aikin ya haxa har da

radiyo da talabiji ba kawai jaridu da mujallu ba, amma aikin zai taimaka ta fuskar yadda kafofin watsa labarai suke gudunar da aikinsu a rubuce.

Haka nan ma Maryam (2006) ta yi nazarin mujallun finafinan Hausa da samuwarsu da kuma havakar su. Sannan ta bayyana ma'anar mujallun Finafinai da cewar su ne mujallun da ke xauke da labaru da bayanai game da finafinan Hausa, sannan ta kawo ire-iren abubuwan da suka qunsa. Maryam ta kawo tarihin samuwar mujallun finafinan Hausa daga 1994 zuwa 2006. Daga nan ta zayyano muhimmancin su da suka haxa da bunqasar harshen Hausa da ilimantarwa da wayar da kan jama'a da xebe kewa ko sanya nishaxi da havaka kasuwanci da kuma samar da ayyukan yi.

Ta fuskar matsalolin da suke fuskanta kuwa da yadda za a havaka su ta kawo bayani a kan zuba jari da masu zuba jari da gwamnatoci da masu tsarawa da bugawa da sauran al'umma a matsayin abubuwan da suke taka muhimmiyar rawa a wajen havaka irin waxannan mujallu. Maryam ba ta kalli rashin bin qa'idojin rubutu a matsayin wata matsala da ake fuskanta a jaridu ko mujallu ba.

Guibi (2006) ya yi bayani kan jaridu da maqalu da mujallu da ake wallafawa a yanar sadarwa ta internet. Daga ciki ya kawo adireshin wasu daga cikin shafukan da ake wallafa jaridu da mujallun Hausa a cikinsu waxanda suka haxa da mujallun Fim __www.fim. "http://www.fim.tvheaven.com ko _www.kanoonline.com_) da kuma mujallar Gidauniya www.gidauniya.4t.com_). Haka nan ya kawo adireshin jaridar Almizan www.almizan.faithweb.com_). Sannan ya kawo irin rawar da irin waxannan jaridu da mujallu suke takawa. Sai dai nazarin nasa bai tavo yadda ake gudanar da rubutu a waxannan kafafe ba, amma aikin na Gurbi zai taimaka gaya a wajen samar da sahihan bayanan da za a yi amfani da su a yayin nazarin jaridu da mujallun da ake wallafawa a yanar sadarwa.

Halima (2008) ta kawo bayani a kan jaridun Amana da A Yau da Gaskiya Ta Fi Kwabo, tare da tarihinsu da yadda suke gabatar da rahotanni. Haka nan ma ta

yi bayani kan yadda editocin waxannan jaridu suke gudanar da aikinsu. Sannan ta yi nazarin yadda kare-karen harsunan editocin kan yi tasiri a kan yadda suke gudanar da rubuce-rubucensu. Amma ba ta kalli matsalar bin qa'idojin rubutu a waxannan kafafen isar da saqonni ba.

Rabi'u (2009) ya yi nazarin yadda editan jaridar Gaskiya Ta Fi Kwabo ya yi amfani da adon harshe daga shekarar 1939 zuwa 1945. A babi na uku ne ya kalli yadda edita ya yi amfani da salon sarrafa harshe. Abubuwa da Rabi'u ya yi bayani sun haxa da karin magana da siffantawa da kwalliya da abuntawa da dabbantawa da mutuntawa. Duk a cikin nazarinsa bai kalli yadda editan jaridar ya yi amfani da qa'idojin rubutu ba. Don haka wannan nazari zai cike wancan givi na bin qa'idojin rubutu amma a jaridu da mujallu da allunan talla da abubuwan hawa.

Muhammad (2009) ya kawo irin cigaba da kuma matsalolin da rubutun Hausa ya fuskanta. Tarihin nasa ya faro ne tun daga lokacin da aka yi yunqurin samar da qamusun nan na Bergery.

Haka nan ya tavo maganar jaridu a inda ya yi bayanin su tare da kawo jerin sunayensu da kuma lardin da ake wallafa kowace da kawo bayanin irin matsalolin da wallafe-wallafen Hausa suka shiga tun daga lokacin da aka rushe kamfanin NORLA har zuwa 1966. Koda yake aikin na Muhammad bai tavo matsalolin rashin bin qa'idojin rubutu a waxancan jaridu kamar yadda wannan aikin yake qoqarin bincikowa ba, amma ya kawo matsalolin da wallafar jaridu da littattafai suka shiga saboda wasu dalilai na gwamnati. Daga nan ne marubucin ya duqufa wajen bayanin yadda wasu daga cikin qa'idojin rubutun Hausa suke wanda nan ne babbar alqiblar da littafin ya fuskanta. Sai dai aikin nasa bai kalli wasu jaridu da mujallu ba da nufin bin diddigin yadda ake amfani da qa'idojin rubutu a cikinsu kamar yadda wannan aiki ya fuskanta.

2.1.3 Muqalu

Zarruq (1982) ya yi bayani dalla-dalla a game da dangantakar da ke akwai a tsakanin rubutu da maganar baka inda ya bayyana yadda ake samun bambance-bambance a tsakanin furucin kalmomi da kuma yadda ake rubuta su, musamman a harsunan Ingilishi da Larabci da Faransanci. Ya kawo misalan yadda furucin harafi yake sauyawa a cikin wasu kalmomi na Ingilishi inda ya bayar da misalan kalmomin ‘chortle’ da ‘chorus’ da ‘cache’ da ‘give’ da ‘gist’ da ‘gnat’ da sauransu. Ya bayyana dalilan da sukan sanya a samu irin wannan bambanci, daga ciki akwai daxewa ana rubuta su a bisa qa’idoji kafaffu, alhali kuwa lafazin masu magana da harshen yana sauyawa da kaxan-kaxan.

Takardar ta bayyana cewar saboda harshen yana canzawa a koyaushe, musamman saboda hulxa da sauran harsuna, ba abin mamaki ba ne bayan ‘yan shekaru rubutu ya bar lafazi a baya har ma a rasa dalilin da ya sa ake rubuta haruffan wasu kalmomin Ingilishi, misali ‘psychology ’da ‘pneumonia’ da ‘droughtsman’ da sauran makamantansu.

Haka nan takardar ta tavo matsalolin rubutun Hausa inda ta yi bayanin cewar a Hausa ba wai rubutu ba ne ya tafi ya bar lafazi ba, a’a, rubutun ne bai samu zama da gindinsa sosai ba. Ya qara bayyana cewa Hausa dai tana da hanyoyin rubutu uku ne; ajami da bokon Nijeriya da bokon Nijar, to amma an zavi bokon Nijeriya saboda ana jin ya fi sauran yaxuwa a littattafan da ake karantawa a makarantun zamani da na nishaxi da jaridu da mujallu (da ma yanar sadarwa). Bayan haka, ana ganin hanyar ta fi sauqi wajen karantawa da rubutawa, duk da yake rubutun ajami shi ne ya fi daxewa ga al’ummar Hausawa.

Duk da wannan fifiko da bokon Nijeriya ya samu a bisa sauran hanyoyin, Zarruq ya kawo raunin dukkan waxancan hanyoyin rubutun da aka ambata domin kuwa duka hanyoyin uku babu wadda take iya ganar da mai karatu game da irin

bambancin karin amon da ke tsakanin kalmar “masaqa” ta sunan muhalli da “masaqa” ta sunan mutane, sai dai abin da ba a rasawa, cewa ajami da bokon Nijer suna bambance, tsawon wasali da gajeren wasali. Sannan da bokon Nijar da na Nijeriya duka babu mai rarrabe tsakanin ‘r’ iri biyu da ke cikin kalmar “ragama” da “rahama”. Bambancin aikin na Zarruq da wannan aiki shi ne wannan aikin yana qoqari binciko irin kwamacalar da ake samu ta fuskar rubutun Hausa.

Zahra (1984) ta yi bayanin furuci a matsayin babbar hanyar sadarwa. Daga nan sai ta kawo wasu hanyoyin sadarwa da suka haxa da shela ko yekuwa da bayar da saqo ta hannun al’umma da kuma sauran hanyoyi na gargajiya irin su hura hayaqi da kaxa ganga ko kuge ko wani abin kixa ko busa abin busa kamar qaho.

Daga baya ne aka fara amfani da rubutun Larabci ana rubuta Hausa, wato tsarin rubutu na ajami, sannan bayan zuwan Turawa ne aka fara amfani da rubutun boko ana rubuta Hausa. Ta cigaba da bayar da tarihin samuwar rubutun ajami da na boko a qasar Hausa. Haka nan ta karkata akalar takardarta zuwa dalilan samuwar jaridu a qasar Hausa inda ta fi mayar da hankali a kan jaridar Gaskiya Ta Fi Kwabo duk da yake ba ita ce jaridar da aka fara bugawa a Nijeriya ba. Daga cikin dalilan da ta bayar na kafa wannan jarida akwai wayar da kan jama’a, musamman a lokacin da yaqin Hitler ya varke, aka fara yaxa jita-jitar cewa Ingila za ta bayar da qasar Nijeriya ga qasar Jamus don ita ma ta samu qasar da za ta mulka. Wani dalilin kuma shi ne bayan qare yaqin Hitler sai aka qara faxaxa yawan jaridun da ake wallafawa zuwa kowane lardi ya riqa wallafa tasa jaridar, musamman don yaqar jahilci.

Daga nan sai ta mayar da hankali kan fuskantar abin da takardar take magana a kai wato salo da sarrafa harshe a jaridun Hausa. Ta fara ne da bayar da ma’anar salo da salon sarrafa harshe da yadda ake amfani da kalmomi da jimloli a wajen isar da saqonni a jaridun Hausa. Haka nan ta kalli yadda ake amfani da zane-zane a jaridun duk dai a qoqarin isar da saqonni ga al’umma. Sai dai Zahra ba ta yi

nazarin rubutun Hausa a cikin irin waxannan jaridu ba kamar yadda wannan bincike yake qoqarin yi.

Shi ma Xangambo (1985) ya gabatar da muqala a kan qa'idojin rubutun Hausa mai manufofi guda biyu; manufa ta farko ita ce fito da qa'idojin rubutun Hausa don yaxawa kowa ya sani. Ta fuskar wannan manufa ya mayar da hankali ne ga irin matsalolin da xalibai suke fuskanta a fagen rubutun Hausa da irin mahawarar da malamai suke yi domin rashin amincewa da juna a kan wata qa'idar rubutu.

Manufar wannan muqala ta biyu ita ce fito da matsayin da Hausa take da shi domin nuna cancantarta na zama harshen qasa. Xangambo ya fito da matsalar tsayar da qa'idar rubutu da zaven harshen qasa. Daga nan ya mayar da hankali a kan irin kurakuran da aka fi yi a rubutun Hausa inda ya kalli matsalar haxe kalma da kuma rabe ta da kuma irin tasirin da karin harshe yake yi a yayin da marubuci yake yin rubutunsa. Har dai Xangambo ya kammala muqalarsa bai yi bayanin irin matsalar da ake fuskanta a rubutun jaridu ko mujallu ba kamar yadda wannan aiki ya yi.

Sa'id (2002) ya yi waiwaye a kan qa'idojin rubutun Hausa inda ya yi nazarin abubuwan da suke haddasa matsaloli a rubutun Hausa. Da farko ya yi tsokaci a game da qirqiro qa'idojin rubutun Hausa da yadda ake sarrafa wasu baqaqe a yayin rubutu, inda ya kalli harafin **m** da **n** a tsakiyar kalmomi da kuma **n** da **r** a muhallin mallaka da yadda ake rubuta ninkin tagwayen haruffa irin su **ts** da **sh** da **ky** da sauransu. Haka nan ya kalli wasu kalmomi na musamman inda ya yi nazarin harxaxxun sunaye da mataimakan fi'ilai da kalmomin sadarwa.

Sa'id ya cigaba da bayyana yadda ake bambance jakada **wa** da xafa qeya **wa**. A qarshe ne ya yi bayanin inda ake amfani da manyan haruffa da alamomin ajiye magana da suka haxa da aya da alamar tambaya da alamar motsin rai. Haka

nan ma ya kalli sauran alamomi irin su waqafi da waqafi mai xigo da karan-xori da baka biyu da kuma alamar zarcewa.

Duk da wannan qoqari na Sa'id bai kalli wata kwamacala da ta shafi rubutun Hausa ba. Sai dai wannan aiki ya haskaka qwarai wajen fahimtar qa'idojin rubutu da kuma yadda ake amfani da su a yayin rubutu.

Bayan waxannan akwai wasu shafuka da suke koyar da wasu vangarori na nazarin Hausa da suka haxa da nahawu da adabi, waxanda mallakar wasu jami'o'i ne, daga ciki akwai Jami'ar Califonia da ke Los Angeles, musamman don masu sha'awar sanin ko nazarin wani abu game da Hausa. Sauran shafuka da aka bayar da misalan su sun haxa da waxanda wasu al'umma sukan buxe don tallata hajarsu kamar www.dantatafamily.com da www.hausanet.com da www.kanoonline.com. Akwai kum shafuka irin su http//mujahidah.htmlplanet.com da ake amfani da ita don yaxa wa mata Musulmi labaru daga sauran vangarori na duniya.

A yanzu dai kaxan ne daga cikin wallafe-wallafen 'yan qasa suke a shafukan yanar sadarwa. Misali qungiyar tunawa da Abubakar Imam ta Zariya (Abubakar Imam Foundation) suka buxe shafin www.abubakarimam.com wadda take xauke da dukkan littattafan da Abubakar Imam ya rubuta. Haka nan akwai littattafai da akan samar kyauta irin su fassarar R. Sutherland Rattray na Hausa Folk-Lore Custom, Proverbs da sauran makamantan su. Wani muhimmin shafi da za a iya samu shi ne shafin samar da bayanai na Wikipedia Encyclopedia da Hausa, wato http//ha.wikipedia.org/wiki/main page. Ire-iren waxannan aikace-aikace ne wannan aikin yake son ya kalla ta fuskar rubutun Hausa a jaridu ko mujallu ko allunan talla.

Adamu (2004) kuwa ya bayyana irin cigaban da harshen Hausa ya samu ta fuskar xab'i, musamman a fagen kwamfuta. Bayaninsa ya faro ne tun daga lokacin da aka fara qoqarin rubuta Hausa a kwamfuta ta hanyar amfani da haruffan Hausa,

musamman haruffa masu qugiya (v, x, q) da irin qoqarin da aka yi na samar wa Hausa haruffanta (fonts) a kwamfuta.

Yunqurin bai tsaya a rubutun Hausa ta amfani da haruffan boko kawai ba, har ma da yadda aka yi qoqarin samar da haruffan Hausa ta ajami tun da yake ana rubuta Hausa ta hanya biyu ne; Hausar boko da Hausar ajami. Daga cikin qoqarin da aka yi akwai samar da haruffa na 'Rabiat' da 'Daneji' da 'Abdalla' waxanda marubuta Hausa suka riqa amfani da su a wajen buga littattafai da wallafe-wallafe ta amfani da kwamfuta.

Wani vangaren kuma da wannan takarda ta mayar da hankali a kai shi ne amfani da rubutun Hausa a 'yanar sadarwa' (Hausa website). Adamu ya bayyana cewar duk da ximbin rubuce-rubuce da ake da su a Hausa, qalilan ne daga cikin su suka sami shiga yanar sadarwa. Daga cikin shafukan da suka fara buga Hausa a yanar sadarwa akwai www.gumel.com da www.bisharat.com.

Amfani (2004) ya yi bayyanin irin ci gaban da aka samu ta fuskar nazarin harshen Hausa a cikin shekara arba'in. Daga cikin fannonin da ya tavo kuwa har da tarihin ci gaban da aka samu ta fuskar qa'idojin rubutun Hausa tun daga lokacin Hanns Vischer a shekarar 1912 da amfani da haruffa masu qugiya wato **v** da **x** da **q** da kafa Hukumar Kula da Harshen Hausa a shekarar 1955 da Taron Qa'idojin Rubutu na Bamako a 1966 da na Jami'ar Ahmadu Bello a 1970 da na Jami'ar Bayero a 1972. Haka nan ya kalli vangaren wallafe-wallafen littattafai da mujallu da vangaren nazarin tsarin sauti da na ginin kalma da kuma na ginin jimlolin Hausa, sannan ya kalli kundayen bincike na digiri na farko zuwa na uku. Amma duk da wannan qoqari bai danganta yadda ake samun kwamacala a jaridu ko mujallun Hausa ba.

Shi kuwa Gidan Dabino (2004) bayyana ma'anar jarida da mujalla ya yi waxanda ya ce asalinsu kalmomin Larabci ne da suke nufin labarai ko bayanai da

ake rubutawa ko bugawa a cikin warqoqin takardu, su kuma fito da wani suna da aka bai wa jaridun ko mujallun a wani qayyadajjen lokaci.

Ya danganta asalin aikin jarida a qasar Hausa (da ma sauran qasashen Afirika) da irin saqonnin da sarakuna sukan aika zuwa ga takwarorinsu ko ta hanyar shela ko yekuwa da wasiqu da kundaye da sauran hanyoyin isar da saqonni a gargajiyance. A Nijeriya kuwa, ya kawo asalin jarida (irin wacce ake da ita a yau) ta farko ita ce wadda Rev. Henry Townseed ya fara bugawa a shekarar 1859 mai suna Iwe Irohin mai fitowa a harshen Yarabanci da Turanci. Jaridar Hausa ta farko kuwa ita ce jaridar Nijeriya ta Arewa a 1932 mai shafi 22, wadda Maxaba'ar Gwamnati da ke Kaduna take bugawa. Jaridar tana fitowa a cikin harsunan Hausa da Turanci da Larabci.

Daga nan ya ci gaba da bin diddigin samuwar jaridu har zuwa lokacin da aka qago jaridu na lardi-lardi da kafa hukumar NORLA da yadda jaridu da mujallu suka samu bunqasa a arewacin Nijeriya. Haka nan ya yi bayanin mujallun 'yan fim da na marubuta littattafai da na masu waqoqin yabon Annabi (SAW) da na harkokin mata tare da kawo jerin sunayen wasu daga cikin jaridu da mujallun Hausa rayayyu da matattu. A qarshe ya kawo matsalolin da jaridu da mujallun Hausa suke fuskanta, sai dai kuma bai kawo wani bayani dangane da rubutu ba da yadda ake gabatar da rubutu a jaridu da mujallun na Hausa ba kamar yadda wannan aiki yake qoqarin yi.

Almu (2004) ya bayyana muhimmancin hanyoyin sadarwa na zamani da yadda za a iya amfani da su a fagen nazarin Hausa. Xaya daga cikin muhimman tambayoyin da aikin nasa ya yi qoqarin amsawa ita ce ta yaya harshen Hausa zai iya cin gajiyar waxannan hanyoyi ta fuskar adabi da al'adu da siyasa da tattalin arziki da kuma sauran harkokin rayuwa?

Almu ya yi qoqarin bayyana wani shiri na kwamfuta (Hausa Word Processor) wanda zai iya bayar da damar sarrafa kwamfuta da harshen Hausa.

Wannan shiri kuma zai bayar da damar yin zane-zane da yin rubutu na qawa da launi iri daban-daban (da za a iya amfani da su a wajen wallafe-wallafen littattafai da jaridu da mujallu da allunan talla da abubuwan hawa, musamman na haya). Bayan nan shirin zai riqa gyara kalmomin da ba a rubuta su daidai ba (spell-check) da bayar da ma'anonin kalmomi (kamar yadda qamusun Thesaurus yake yi) wanda zai rage yawan kurakuran da ake samu a harkokin wallafe-wallafe da na xab'i da sauqaqa ayyukan editoci da kuma ciyar da rubutun Hausa zuwa wani mataki na zamani. Almu bai bayyana irin kwamacalar da ake samu a rubutun Hausa ba.

Shi kuwa Vatagarawa (2005) ya kawo irin matsalar da rubutun Hausa ba ya iya warwarewa. Daga cikin matsalolin akwai kasa bambance furucin kalmomin da ke da kama guda, abin da kawai ya bambanta su shi ne tsawon wasali ko karin sauti wato hawa ko saukar murya. Ya kawo misalan kalmomi irin su tafi (tafi) da tafi (taafii).

Haka nan ya kawo muhimmancin hawa ko saukar murya da kuma nuna tsawo ko gajartar wasali a rubutu domin kuwa za su iya bambance kalmomi biyu ko ma fiye tare da rubuta kalma kamar yadda ake furtawa, kamar dai yadda rubutun ajami da rubutun bokon Jamhuriyar Nijar suke yi.

Saboda wannan dalili ne Vatagarawa yake bayar da shawara ga masana da su riqa amfani da nunin tsawon wasali da kuma hawa ko saukar murya a cikin rubutun Hausa domin bayar da damar bambancewa a tsakanin kalmomi masu siga iri xaya ta fuskar rubutu wanda rubutun Hausar bokon Nijeriya a yanzu ba ya iya bambancewa. Duk da wannan qoqari Vatagarawa bai kalli halin da rubutun Hausa yake ciki a wata jarida ko mujalla ba kamar dai yadda wannan aiki yake qoqarin nazari halin da rubutun yake a jaridu da mujallu da allunan talla da sauran abubuwan hawa, musamman na haya.

Bunza (2009) ya yi bayani ne na tarihin jaridu da mujallu a qasar Hausa inda ya bayyana ma'anar kalmomin biyu wato jarida da mujalla tare da nuna tarihin

cuxanya tsakanin al'ummar Hausawa da Larabawa wadda ita ce ta haifar da tsarin rubutun Hausa na farko wato ajami. A cikin bayanin nasa ya kawo jaridar Hausa ta farko da aka fara wallafawa wadda ita ce jaridar Nijeriya ta Arewa a shekarar 1932. Daga nan sai jaridu irin su Daily Comet da Daily Mail (waxanda ba na Hausa ba ne amma suna qunshe da labarai da Hausa a wasu daga cikin shafukansu)

Ta fuskar mujalla kuwa Bunza ya bayyana cewa mujallar Alfijir ita ce mujallar Hausa ta farko da ake bugawa a qarqashin Hukumar Yaqi da Jahilci Ta Arewacin Nijeriya (NORLA) a shekarar 1953. Daga nan ya kawo bayanin bunqasar jaridu da mujallu a lokacin rayuwar hukumar NORLA har zuwa shekarun 2006. Sannan ya kawo irin gudummuwar da qungiyoyi daban-daban, musamman masu zaman kansu, suka bayar wajen havaka da bunqasar jaridu da mujallun Hausa a Nijeriya. Duk da bayanin havakar jaridu da mujallu Bunza bai yi nazarin irin matsalar da ake samu ta fuskar rubutun Hausa a jaridu da mujallu da allunan talla da abubuwan hawa da sauran fannoni na rayuwa ba.

Abubakar (2010) ya bayyana irin rawar da jaridu da mujallu za su taka a fagen sauqaqa samuwar fannonin ilimi, musamman waxanda ba kowa ne zai iya zuwa ya koyi yadda ake nazarinsu a makarantu ko a gaban masana ba. Ya kawo misalin a wasu qasashe da suka ci gaba jaridu da mujallu ba su taqaita a samar da labarun siyasa da tattalin arziki da adabi da zamantakewa kaxai ba. Suna samar da bayanai da suka shafi fasahohin zamani da na qere-qere da ilimin sararin samaniya da na qarqashin qasa da kimiyyar halitta da kimiyyar sadarwar zamani da ta inganta muhalli da sakamakon binciken da qwararru suka gudanar a fanni daban-daban

Marubucin ya qara kawo misalin jaridar Science da Scientific American da New Scientist da mujallar Physics da National Geographic da PC World da suke samar da irin waxannan bayanai a qasar Amurika. Haka nan ya kawo misalan wasu a qasashen Larabawa kamar jaridun Okaz a qasar Saudiyya da Al-Jamhuriyya a

qasar Misira. Irin wannan aiki da jaridu da mujallu suke yi yana matuqar taimakawa, musamman ga xalibai wajen qara masu qwazo da kuma cusa masu kwaxayin abin a zukatansu.

Abubakar ya kawo shawarar samar da irin waxannan jaridu da mujallu a wannan qasa ta Nijeriya don ganin iri taimakon da za su bayar ta fuskar ilimantar da al'umma tare da samar da sahihan bayanai a kan fannoni daban-daban na ilimi, musamman ma dai ilimin kimiyya da na kimiyyar sadarwa irin su kwamfuta da fasahohin qere-qere na zamani. Ya kuma nuna cewar abu ne mai kyau idan jaridu da mujallu, musammn na Hausa, za su rage yawan shafukan da suke sadaukarwa wajen yin hira da cuku-cukun siyasa ko kuma su qara ko da shafi guda ne don gabatar da wasu nau'o'in bayanai masu alaqa da fannin kimiyya a cikin harshen Hausa. Sai dai Abubakar bai mayar da hankalinsa a kan irin matsalar da ake samu ta rashin bin qa'idojin rubutu a wata jarida ko mujalla ba.

Yakasai da Mu'azu (2010)***** sun yi qoqarin fito da dabaru ko hanyoyin koyar da qa'idojin rubutun Hausa. Takrdar ba ta yarda da hanyar koyarwa da wasu malaman Hausa suke bi wajen koyar da qa'idojin rubutu ba, wato hanyar a haxa wani vangare na kalma da wani (a samu kalma guda) ko a raba wata kalma guda ta zama kalma biyu. An daxe ana bin wannan hanya wajen koyar da qa'idojin rubutn Hausa, maimakon kwalliya ta biya kuxin sabulu kullum sai koma-baya ake samu. Wato xalibai da marubuta da 'yan jarida sun kasa fahimtar zubi da tsarin yadda ya kamata a yi rubutun Hausa.

Wannan takarda an gabatar da ita a Taron Qara wa Juna Sani wanda Qungiyar Malaman Harsunan Nijeriya ta Qasa ta shirya a Kwalejin Ilimi ta Tarayya da ke Kwantagora a jihar Neja. Sannan daga baya aka yi mata kwaskarima aka sake gabatar da ita ga maáikatan jaridar Aminiya a shekarar 2011. Haka nan an sake yi mata gyaran fuska aka sake gabatar da ita ga maáikatan Sashen Hausa na BBC a ofishinsu da ke Abuja a shekarar 2012.

Wannan takarda ta yi nuni da cewa a halin da rubutun Hausa yake ciki a yanzu akwai buqatar a yi waiwaye a kan yadda za a koyar das hi. Takardar ta fito da dabarun koyar da qa'idojin rubutun Hausa waxanda suka haxa da sanin baqaqe da wasula da tsarin gavar kalmomin Hausa da sanin rukunan nahawun Hausa da iya rarrabe su da kuma sanin wasu dokokin rubutun Hausa ta fuskar tsarin sauti da qira da ma'anar kalmomin Hausa.

Takardar ta yi nuni da cewar idan aka bi waxannan dabaru za a iya fahimtar cewar akwai qa'idojin rubutun Hausa kuma bah aka nan suke kara-zube ba; tattare suke da ilimin kimiyyar harshe na Hausa. Manifofin wannan takarda sun haxa da fahimtar halayen rubutacciyar magana da iya amfani da ita yadda ya kamata, da iyakance haruffan da ake rubutu da su da iya karanta Hausa cikin sauqi da isar da saqo daidai.

Adamu (2012) ya kawo asalin rubutun Hausa a ra'ayin Malam Aminu Kano. Ya nuna cewar an fara samun rubutu a garin Kano a jikin wata tsohuwar rijiya a wata unguwa. Ya bayyana cewa Hausawa ba su da wani tsarin rubutu gabanin rubutun ajami da na boko. Ya qarfafa cewar bayan rushewar daular Romawa sun bazu a cikin duniya, musamman duniyar baqar fata ta Afirika. Wasu daga cikin su sun zauna a wata unguwa a garin Kano. A kusa da inda suka zauna akwai wata rijiya da ake kira 'Akwa' wadda take nufin ruwa a harshen Girkanci. Tun da yake wannan tsohuwar daula tana da tsarin rubutu tun a wancan lokaci zai yi wuya a ce waxannan mutane ba su yi wasu rubuce-rubuce ba a lokacin da suka zauna a wannan unguwa, sai dai a ce ba a samu kaiwa gare su ba. Haka nan Adamu ya yi nazarin waxansu ra'ayoyi game da samuwar rubutu a qasar Hausa. Ya kalli samuwar rubutun ajami da na boko.

Wannan muqala ta kuma yi nazarin yadda aka Hausantar da haruffan Larabci kamar su anbakiwofi da alubaqi da alu ja da lamjaye da ha babba da kuri

da sauran haruffan da ake amfani da su a rubutun Ajami. Haka nan ma ya yi nazarin matakan samuwar rubutu a qasar Hausa tun kafin samuwar rubutun Ajami har ya zuwa samuwar rubutun boko. Duk da wannan qoqari da Adamu ya yi bai yi nazarin yadda ake gudanar da rubutun Hausa a jaridu ko mujallu ba. Don haka wannan aiki zai yi qoqarin yin nazari a kan yadda ake gudanar da rubutu a waxancan kafafen isar da saqo. Aikin Adamu zai taimaka qwarai wajen qoqarin gano asalin rubutun Hausa da kuma yadda ya havaka ko bunqasa a yau.

2.2 Naxewa

An yi bitar ayyukan da masana da manazarta suka gabatar masu alaqa da wannan aiki ta fuskar rubutun Hausa ko waxanda suka shafi jaridu ko mujallu. Waxannan ayyuka da aka duba sun haxa da littattafai da muqalu da kundayen bincike na neman digiri na biyu da na uku don tabbatar da samun sahihan bayanai a kan abin da ya shafi rubutun Hausa ko jaridu ko mujallu.

Wannan aiki yana qoqarin gano irin matsalolin da ake samu a jaridu da mujallu da allunan talla da abubuwan hawa da sauran fannoni na rayuwa. Wannan bincike ya bambanta da dukkan waxanda suka gabace shi domin kuwa sun kalli wasu matsalolin da kai tsaye ba su yi daidai da wannan aikin ba, amma babu wanda ya kalli jaridu ko mujallu ta fuskar kwatanta qa’idojin rubutun Hausa.

BABI NA UKU

SAMUWAR RUBUTUN HAUSA

3.0 Gabatarwa

Xaya daga cikin hanyoyin bayyana harshe a kan takarda ita ce, hanyar amfani da haruffa domin su wakilci muryoyin harshe, a bisa wasu hanyoyin rubutu. Hausa na da hanyoyin rubutu iri biyu, ajami (rubuta Hausa cikin haruffan Larabci) da rubutun book (rubuta Hausa cikin haruffan boko).

Rubutu shi ne zayyana wasu alamomi a kan takarda ko a kan wani abu mai bigire don sadar da magana wadda xan'adam ya fi faxar ta da fatar baki, a ji da kunne. Rubutu dai ya samu ga xan'adam tun lokaci mai tsawo da ya shuxe, kuma ana amfani da alamomin rubutu iri-iri a sassa daban-daban na duniya (Yahaya 1988:1). Yana da wuya a iya cewa ga wanda ya fara yin rubutu a duniya illa dai kawai masana tarihi sun gano cewa Mesapatomia ce al'ummar da ta fara amfani da rubutu. Kafin fara rubutun boko a qasar Hausa ana amfani ne da rubutun ajami, wato salon rubutun Hausa ta amfani da haruffan Larabci tare da yi wa wasu gyare-gyare don su dace da wasu saututtukan da babu kwatankwacin su a harshen Larabci.

Sanarwar farko ta sauya amfani da rubutun ajami zuwa rubutun boko ta fito ne daga ofishin sakataren Lugard ranar 29 ga watan Oktoba na shekarar 1902. Sanarwar ta bayyana cewar za a riqa amfani da tsarin rubutun boko a maimakon na Larabci ko ajami da tun fil'azal Turawan mulkin mallaka suka tarar ana amfani da su. Turawan mulkin sun qara bayar da fifiko ga duk wanda yake son ya yi aiki da gwamnati dole sai ya iya amfani da tsarin rubutu na boko wajen rubuta Hausa ko da kuwa bai iya amfani da Ingilishi ba. (Phillips 2004:63)

A wannan babi za a yi qoqarin bin tarihin rubutun Hausa da yadda ya samu bunqasa har zuwa yau. Haka nan za a kalli matsalolin da rubutun Hausa ya fuskanta tun daga samuwar sa har zuwa matakin da yake ciki a yau. Sannan kuma za a bayyana matakai da qa'idojin rubutu ya hau har zuwa matakin da yake a yanzu.

3.1 Rubutun Boko

Tsarin rubutun boko dai kamar yadda aka sani, tsari ne na amfani da haruffan abacada, inda ake gwama baqi da wasali a jere domin tayar da zance. Rubutun boko ya samo asali ne daga rubutun Latin na harshen Romawa tun kimanin shekara 3,100 da suka wuce. Irin wannan tsarin rubutu ne qasashen Turai kamar su Ingila da Faranshi da Jamus da sauran makamantan su suke amfani da shi yayin rubuta harsunansu.

An fara rubuta Hausa a cikin rubutun boko a qasar Turai tun kafin boko ya fara wanzuwa a qasar Hausa. A wajen shekarar 1535 aka sami wani Balarabe haifaffen Afirka ta Arewa mai suna Al-Hassan Ibn Muhammad Al-Wizas wanda ya yi zaman kaso (kurkuku) a qasar Italiya kuma wanda aka fi sani da Leo Africanus ya rubuta wasu littattafai guda bakwai a cikin harshen Larabci, waxanda suke xauke da labarai a kan tafiye-tafiyen da ya yi a cikin qasashen Afirka. Daga baya ne aka fassara waxannan littattafai zuwa harshen Ingilishi (da ma wasu daga cikin harsunan Turai). A xaya daga cikin litattafan ne ya bayar da labarin zuwan da ya yi qasar Borno da wasu daga cikin daulolin qasar Hausa a tsakanin shekarar 1513-1515 waxanda ya rubuta sunayensu kamar haka:

Gubir (Gobir)
Cano (Kano)
Casena (Katsina)
Zegzeg (Zazzau) (Yahaya 1988: 73)

Irin waxannan labarai da Turawa suke samu a game da sabuwar duniyar Afirka ne ya kwaxaitar da su, musamman na qasar Portugal da na Jamus da na Faranshi da ma na Ingila, suka duqufa wajen binciko yadda wannan sabuwar duniya take da yanaye-yanayenta. A shekarar 1788 an kafa wata qungiya mai suna African Association mai manufar gano farkon Kogin Neja da qarshensa da kuma yiwuwar qulla hulxar ciniki a tsakanin qasar Ingila da mazauna gavar kogin. Daga cikin fitattun mutanen da wannan qungiya ta aiko akwai Mango Park (Mabuxin Kwara) da Clapperton da Denham da Landers daga 1795-1830. Waxannan mutane sun yi wa kogin da garuruwan da suke a kewayensa ganin qwaf. A cikin wannan tafiya ne wasu daga cikinsu suka ziyarci qasashen Sakkwato da Kano suka kuma yi rubutu a kan rayuwar mutanen waxannan garuruwa. (Yahaya 1988:73)

A qasar Denmark ne aka fara samun kalmomin Hausa a cikin rubuce-rubucen Turawa a lokacin da sarkin Denmark ya tura wakilansa zuwa qasar Arabiya a shekarar 1773 don gudanar da bincike na kimiyya. Daga cikin waxannan wakilai har da wani mai suna B.G Niebuhr, wanda shi kaxai ya rayu ya kuma sami damar komawa qasar ta Denmark. A cikin wannan shekara ne wani Balarabe mutumin Tunis mai suna Abdurrahman tare da wani bawansa wanda yake fahimtar harsunan Larabci da Barbarci da kuma Hausa suka kai ziyara a qasar ta Denmark. Saboda Neibuhr yana jin harshen Larabci a sanadiyyar zaman da ya yi a qasar Yemen sai sarkin Denmark ya sa aka kira shi domin ya yi masa tafinta a tsakinsa da wannan jekada na Tunis. Daga nan sai abota ta qullu a tsakanin Neibuhr da Abdurrahman har Neibuhr ya yi sha’awar koyon harsunan da bawan Abdurrahman yake ji. Neibuhr ya duqufa wajen koyon harshen Hausa, inda bawan Abdurrahman ya riqa faxa masa sunayen abubuwa da harshen Hausa shi kuma yana qoqarin rubutawa kamar yadda ya ji muryarsu tare da fassararsu kamar haka:

dudsji	dutsi	hill
ghaui	gari	town

koroma	qorama	stream
dsjenari	zinari	gold
ghurass	gurasa	wheaten food
sinkaffer	shinkafa	rice
bavia	baiwa	female slave
crua	ruwa	water (Yahaya 1988: 74)

A shekarar 1791 ne aka wallafa waxannan kalmomi a cikin wani littafi mai suna Life of Neibuhr. Baya ga wannan a qasar Ingila akwai wani xan kasuwa Balarabe mutumin qasar Moroko mai suna El-Hajj Abd Salam Shebeni wanda yakan je qasar Ingila domin yin fatauci. El-Hajj Abd Salam ya sheda wa sakataren Qungiyar Afirka da ke London cewa akwai wata qasa da ake kira Houssa a Afirka ta Yamma, kuma mutanen wannan qasa suna da ilimin karatu da rubutu da haruffan Larabci (ajami). Wannan bayani nasa ya sanya gwamnatin Ingila da Qungiyar Gano Afirka da wasu qungiyoyi na addinin Kirista na qasashen Turai suka qara qaimi wajen turo masu binciken al'adu da harsuna da labarin qasa da masu yaxa addinin Kirista da masu mulki suka yi ta sintiri a Afirka ta yamma a cikin qarni na sha takwas da na sha tara (Yahaya 1988:72-74).

Tun kafin Turawan mulki su karvi iko daga hannun sarakuna ne wasu Turawan Mishan masu bincike suka fara zuwa qasar Hausa suna nazarin al'adun Hausawa suna komawa qasashensu suna rubutawa a cikin harsunan Turawa (Ingilishi da Jamusanci da Faransanci da sauran su). A tsakanin shekarun 1800 da 1890 wasu Turawan Jamus guda biyu, Dr H. Barth (1821-1865) da Dr. James Fredrick Schon (1803-1889) suka kawo ziyara a qasar Hausa domin yin bincike na sanin qasar Hausa da yaxa addinin Kiristanci. A wannan tafiya tasu ce suka sayi wasu bayi guda biyu wato Durugu (mutumin Damagaran) da Abbega (mutumin qasar Borno). Bayan komawar Dr. Schon gida sai ya yi ta qoqarin rubuta labaru da tatsuniyoyin da Durugu yake faxa masa masu nasaba da qasar Hausa. Dr. Schon ya

samu wasu matsaloli a rubutun nasa da farko dai ya rasa yadda za ya yi da furucin **v** da **q** da **x** da **ts** da sauran makamantansu (Yahaya 1988: 76)).

3.1.1 Nasarar da Rubutun Boko ya Samu

Babbar nasarar da rubutun boko ya samu ita ce bunqasa a cikin xan qanqanen lokaci. Wannan kuwa ya faru ne ta dalilin sanya hannun Turawan mulki da kuma gwamnatocin da suka biyo baya. Turawan mulki sun kakkafa makarantun boko a yankuna daban-daban na qasar Hausa. Da farko dai sun yi qoqarin horar da malamai waxanda za su koyar a makarantun da aka buxe a larduna, sannan sun kawo tsarin iya rubutun boko a matsayin ma'aunin xaukar wanda duk yake so ya yi aiki da gwamnati.

A shekarar 1905 ne aka buxe makarantar boko ta farko a Sakkwato a qarqashin Mr. Burden da kuma mataimakinsa Malam Ibrahim. Sai dai a wannan lokaci iyayen yara sun qi yarda 'ya'yansu su shiga wannan makaranta don gudun kada a mayar da su Kiristoci. Saboda haka wannan makaranta ba ta xore ba sai aka rufe ta. An sake buxe wata makarantar zamani a Kano a shekarar 1909 a qarqashin shugabancin Hans Vischer (Xan Hausa). Daga baya kuma aka ci gaba da buxe irin waxannan makaranru a sauran larduna na arewacin wannan qasa.

A cikin shekarar 1924 kuma gwamnatin jihar Arewa ta kafa Hukumar Fassara. Wannan hukuma ta taimaka wajen havaka da bunqasa rubutun boko domin kuwa ta wallafa littattafai da dama, ta kuma fassara wasu zuwa harshen Hausa. Daga cikin littattafan da ta fassara akwai littafin Dare Dubu Da Xaya wanda aka fassara daga harshen Larabci zuwa Hausa. Haka nan ta wallafa littattafan Hausawa Da Maqwabtansu da kuma Labaru Na Da Da Na Yanzu. A shekarar 1933 gwamnati ta canza Hukumar Fassara zuwa Hukumar Adabi. Wannan hukuma ita ce take da alhakin wallafa littattafai. Daga cikin ayyukan da wannan hukuma ta yi har da sanya gasar wallafa littattafai na qagaggun labarai ga 'yan qasa inda aka samar da littattafai da har yanzu ake amfani da su. Haka zalika

wannan hukuma ta wallafa wata jarida da ake bugawa a cikin harsunan Ingilishi da Hausa mai suna Nijeriya ta Arewa (Yahaya 1988:23).

Gwamnatin jihar Arewa ta yi yunqurin havaka sha'anin yaqi da jahilci a shekarar 1953 saboda haka ne ta kafa hukumar NORLA (Northern Region Literature Agency) a qarqashin shugabancin M.W.F. Jeffries aka kuma miqa mata alhakin shirya azuzuwan yaqi da jahilci da kuma samar da littattafan da za a yi amfani da su. Mr. Skinner ne aka miqa wa alhakin kula da harkar littattafai. Wannan hukuma ta wallafa littattafai masu tarin yawa kuma ita ce ta shirya jaridu na larduna. Daga cikin littattafan da ta wallafa akwai na zube irin su Hali Zanen Dutse da na waqoqi kamar Waqar Mu'amare da Waqar Zuwa Ingila da littafatan wasan kwaikwayo kamar Wasan Marafa da Malam Inkuntum da Zamanin Nan Namu. (Yahaya 1988: 99)

Dukkan waxannan rubuce-rubuce da waxannan hukumomi suka aiwatar suna fa aiwatar da su ne da tsarin rubutun boko ba da na ajami ba, sun ma juyar da waxanda aka yi da ajamin zuwa na boko. Don haka su ma sun taimaka gaya a wajen qara bunqasa da havaka rubutun boko da kuma dakushe rubutun ajami domin kuwa hankalin al'umma ya karkata ga fahimtar rubutun boko don samun damar cin gajiyar ayyukan waxannan hukumomi.

Daina amfani da rubutun ajami, sai dai na boko, ya qara dakushe tagomashin rubutun ajami, ya kuma qara bunqasa rubutun boko inda a yanzu ma samun wanda ya iya amfani da rubutun ajami kamar yadda ake amfani da na boko sai an bincika qwarai da gaske.

3.1.2 Daidaita Qa'idojin Rubutu na Hausa

Duk da daxewar da aka yi ana rubuta Hausa da ajami ba a tava yin wani yunquri domin daidaita masa qa'idojin rubutu ba. Wannan ne ma ya sanya ake samun bambanci daga wani wuri zuwa wani. Babban yunqurin da malamai suka yi kawai shi ne na samun haruffa da za su yi amfani da su waxanda babu su a harshen

Larabci, misali irin su haruffan x da v da q da ts da kuma ‘y, ko su ma dai ana samun bambanci a tsakanin malamai. Shi kuwa rubutun boko kusan a ce tun lokacin da aka fara rubuta Hausa da shi ana tafiya ne ana daidaita masa qa’idojin rubutu. Tun a shekarar 1788 mutanen Ingila suka kawo shawarar yin amfani da wasula irin na Italiyawa da baqaqen Ingilishi a wajen rubuta harsunan duniya, daga baya a shekarar 1836 qungiyar labarin qasa ta Ingila ta zartar da wannan shawarar don ma’aikatanta su sami hanyar da za su riqa bi domin rubuta duk wani harshe da suka sadu da shi.

A shekar 1848 Qungiyar Cocin Mishan (C.M.S) ta buga wani littafi da ta yi wa laqabi da Dokokin Kafa Abjadin Romawa Don Harsunan Da Ba a Rubuta Ba, musamman Na Afirka. Wannan shi ne ya zama babban harsashen da mishan suka kafa wajen rubuta harsunan Afirka cikin haruffan Latin. A cikin wannan littafi ne, qungiyar ta umurci ma’aikatanta da su riqa yin xigo a qarqashin haruffa **b** da **d** da **k** na Hausa a madadin **v** da **x** da **q**.

A shekarar 1850 Lapsius, wani masanin tarihin harsuna, ya tsara wata hanya wadda ya kira Daidaitaccen Abjadi. Daga baya wasu mutane watoNoinhof da Peter Schmidt, suka yi wa abjadin kwaskwarima suka kira shi da Abjadin Bil’adama. Daga nan a shekarar 1891 aka kafa Qungiyar Hausa a birnin London don tunawa da ayyukan da Mr. John Alfred ya yi da kuma ci gaba da bincike a kan harshen Hausa a bisa tafarkin kimiyya. Da kuma ba ma’aikatan mishan damar iya fassara abubuwa zuwa harshen Hausa.

Mutum na farko wanda ya yi rubuce-rubuce da dama a Hausa shi ne James Friedrick Schon, wanda aikin mishan ya kawo shi Saliyo (Sierra Leone) a wajen shekarar 1840. Abjadin da Frederick ya yi amfani da shi, shi ne ya qirqiro abinsa, har ma ya ambaci haka, cewa: “Na riya waxannan qa’idojin rubutu a raina ne, bayan na yi shekaru ina lura da abubuwa. Saboda haka na yi amanna da dacewarsu”. Amma daga baya Schon ya karvi shawarwari daga wajen Lapsius, duk

da haka abjadinsa ya bambanta da sauran waxanda suka biyo bayansa. Daga wannan lokaci sai qa'idojin rubutun Hausa ya rabu; akwai na Frederick da sauran waxanda suka kwaikwaye shi irinsu Prietzer a 1904 da Adam Mischlich a 1906 da Westermann a 1911 da sauransu (Zarruq 1980:4-5).

A xaya vangaren kuma akwai waxanda suka xauki ajami suka juye shi zuwa boko ba tare da sun tace haruffan Hausa daban da na Larabci ba, misali Charles H. Robinson da Alder Burton da sauransu. A wajen rubutun boko suna bin waccan qa'ida ta Qungiyar Afirka ne wato wasula irin na Italiyanci da baqaqe irin na Ingilishi, sannan dole ne a faxi duk baqin da aka rubuta. A sakamakon haka Robinson da sauran masu irin salonsa suna sanya xigagga a qarqashin hamzatattun haruffa wato **v** da **x** da **q**, sannan kuma Robinson yana sanya xigagga a qarqashin duk baqaqen Larabci masu taukidin lafazi, misali **s**, **d**, **t**, **z**. Saboda haka sai a rasa waxanne ne hamzatattu, waxanne ne ba hamzatattu ba.

A shekarar 1879 wani bature mai suna Sir George Goldie ya kafa wani kamfani mai suna U.A.C (United African Company) don qarfafa ciniki a tsakanin mutanen Ingila da na qasar Nijeriya. Daga baya Ingila ta aminta da wannan kamfani har ma ta sauya masa suna zuwa Royal Niger Company ta kuma ba kamfanin izinin yin ciniki da gudanar da mulki a garuruwan kewayen kogin Neja (Sashen jihohin Arewa). Sannan a shekarar 1897 gwamnatin Ingila ta naxa Lord Lugard (wani babban jami'in soja) a matsayin kwamishina mai kula da harkokin tsaron wuraren da kamfanin Royal Niger Company yake iko da su aka ba shi ikon kafa rundunar sojoji mai suna 'Niger Constabulary' don kare jihohin arewa daga cin iyakar da sojojin Faranshi suke qoqarin yi. Wannan runduna ta haxe har da Ilori da Bida da Lakwaja. Turawa sun qulla yarjejeniyar mulki da ciniki da qasar Ingila (Yahaya 1988:79).

A ranar Litinin, 1 ga watan Janairun shekarar 1900, gwamnatin Ingila ta miqa ragamar mulkin jihohin arewa a hannun Lord Lugard, sai ya tafi garin

Lakwaja ya tumvuke tutar Royal Niger Company, ya kafa tutar mulkin Ingila. Lugga ya tayar da hedikwatar mulki daga Lakwaja ya mayar da ita Zungeru a tsakanin 1901-1903. A wannan tsakani ne Lugga ya riqa aika takardu zuwa ga sarakuna yana neman su miqa kai. Wasu daga cikinsu suka bi waxansu kuwa suka qi. Daga nan sai ya aika sojojin Niger Constabulary zuwa Zariya da Yola da Bauchi da Borno da Katsina da Daura da Kano da kuma Sakkwato inda aka sha xauki-ba-daxi daga qarshe dai aka qulla yarjejeniya da su a ranar 15 ga watan Maris na 1903. Sarkin Musulmi Attahiru 1 ya qi amincewa da Turawa da aqidarsu, sai ya janye magoya bayansa masu yawa suka baro Sakkwato, suka bi ta Gusau zuwa Burmi. (Yahaya 1988:88).

A shekarar 1910 ne aka fara rubuta Hausa a Nijeriya a qarqashin Hukumar Mulkin Mallaka. A wannan lokaci ne Hanns Vischer ya tsara wa bokon Hausa qa'idoji. Shi ma ya riqa sanya xigagga a qarqashin hamzatattun haruffa (b,d,k) da kuma amfani da ch a maimakon c, daga baya a lokacin da G.P. Bargery (1876-1966) ya tsara nasa abjadin sai ya riqa sanya waqafi a gaban b da d da kuma bayan k kamar haka 'b, 'd da kuma k'. Bergery ya gina abjadinsa a bisa tsarin Mahaxar Harsuna da Al'adun Afirka ne, xigagga ne kawai bai yarda da su ba. (Zarruq 1980:6).

A shekarar 1932 sai Ofishin Fassara ya zartar da shawarar yi wa hamzatattun haruffa qugiya kamar yadda suke a yanzu wato v da x da q. Kafin a daidaita qa'idojin rubutu kamar yadda suke a yanzu sai da aka xauki tsawon lokaci ana rubuta Hausar boko ta hanyoyi daban-daban. Manyan bambance-bambancen da aka riqa samu su ne:

i Yadda ake haxe kalmomi ko raba su a rubuce. Misali

sukan	su kan
za mu	zamu
koyaushe	ko yaushe da sauransu

ii Hanyoyin sarrafa waxansu sautuka na Hausa a rubutun boko, wato samar da irin sautukan da babu su a abjadin boko. Misali ts da v da x da q da ‘y da sauransu.

iii Matsalar amfani da wani karin harshe a cikin rubutu.

Mafi yawan littattafan da aka rubuta da Hausa kafin qarni na 20, za a tarar da irin waxannan bambance-bambance na hanyoyin rubuta sautukan Hausa a rubutun boko. Wannan kuwa ya faru ne domin a lokacin Turawa ba su gane yadda za su sarrafa sautukan **ts** da **v** da **x** da **q** da ‘**y** a rubutun Hausa ba. Misali a littafin da James Frederick Schon (1803-1889) ya rubuta a shekarar 1885 a game da labarin tafiyar da Durugu ya ba shi da suka yi da Henrich Barth zuwa Sakkwato, ya rubuta kalmomi kamar haka:

tasi	maimakon	tashi
sida	maimakon	shida
bersi	maimakon	barci
kasua	maimakon	kasuwa
Sokotu	maimakon	Sakkwato (Sokoto)

Kamar yadda (Yahaya 1988:126) ya bayyana farkon qarni na 20 ne aka fahimci cewar akwai sautuka na musamman a harshen Hausa, sai aka qago hanyar da za a riqa rubuta waxannan haruffa a cikin rubutu. Marubuta irin su Chales H. Robinson (1861-1925) da Frank Edger sun yi amfani da xigo a qarqashin wasu baqaqe don wakiltar wasu sautuka. Misali,

b	maimakon	v
d	maimakon	x
k	maimakon	q

A haka aka ci gaba da amfani da wannan hanya har zuwa wajen shekarar 1912 lokacin da Hans Vischer (Xan Hausa) ya rubuta wani littafi mai suna Rules For Hausa Spelling inda ya zayyano qa’idojin rubutun Hausa. A ciki ya yi bayanin

kalmomin da ya kamata a haxe da waxanda ya kamata a raba, sannan kuma ya sauya tsarin rubuta wasu daga cikin haruffan Hausa inda aka riqa rubuta waqafi a saman wasu haruffa a maimakon yin xigo a qasansu, misali:

‘b maimakon v

‘d maimakon x

‘k maimakon q

Da waxannan qa’idoji ne Rev. G.P. Bergery ya rubuta qamusunsa mai suna Hausa-English Dictionary and English-Hausa Vocabulary. A shekarar 1932 kuwa sai aka kafa wani kwamiti don daidaita qa’idojin rubutun Hausa. Xaya daga cikin ‘yan kwamitin wato Dr. R.M. East ya tattauna da wani farfesa a kan nazarin Harsuna da Al’adun Afirka mai suna D. Westermann, suka kuma yanke shawarar yi wa b da d da k lanqwasa don nuna sautukan v da x da q, an buga sanarwar amincewa da wannan tsari a Nigeria Gazette, Government Notice No. 396, ta ranar 24 ga watan Maris 1938. R. C Abrahan ya yi amfani da waxannan haruffa a qamusunsa mai suna Dictionary of the Hausa Language wanda aka buga a shekarar 1946. (Sa’id 2004:1).

Tsohuwar gwamnatin jihar Arewa ta kafa Hukumar Hausa a shekara 1955 bayan da wani xan majilisa mai wakiltar Bauchi mai suna Malam Bawa Balkacuwa ya bayar da shawarar yin haka. Dalilin kafa wannan hukuma shi ne domin ta daidaita yadda za a riqa rubuta daidaitacciyar Hausa (don kauce wa amfani da kare-kare a cikin rubutu) tare da daidaita yadda ake rubuta wasu kalmomi a harshen Hausa da kuma tace kalmomin da Hausa takan aro daga wasu harsuna, musamman harshen Larabci da na Ingilishi, da dukkan wasu ayyuka waxanda za su kyautata Hausa a rubuce, saboda ana yawan samun baddale-baddale a rubuce-rubucen da ake gabatar wa majalisa. Daga cikin wakilan wannan hukuma akwai Alhaji Isa Kaita da Alhaji Aliyu Makaman Bidda, waxanda ministoci ne a wancan lokaci. Ayyukan da wannan hukuma ta yi sun haxa da,

- Tabbatar da qa'idojin rubutun Hausa waxanda aka kawo a cikin littafin Rules For Hausa Spelling bayan ta yi gyare-gyare a cikinsa. An wallafa waxannan gyare-gyaren a mujallar Gwamnatin jihar Arewa (Norther Nigeria Gazette) mai lamba Northern Regional Notice no. 31, wanda aka buga a ranar 22 ga watan Janairu na shekara 1957.
- Cim ma yarjejeniya game da wasu kalmomi na nahawun Hausa. Misali suna a maimakon isimi da abin da za a yi a maimakon fi'ili.
- Tsara wani littafi mai xauke da jerin ararrun kalmomi cikin Hausa mai suna Alphabetical List of Words Imported into Hausa.
- Tsara wani littafi na kevavvun kalmomi mai suna Glosseries of Technical Terms. Wannan littafi yana xauke da kalmomi kimanin dubu na wasu kevavvun wurare kamar ma'aikatar gona da ma'aikatar lafiya da sauran makamantan su (Yahaya 1988:129).

Duk da wannan qoqari an ci gaba da rubuta kalmomi barkatai kamar haxe kalmomi ko raba su a wuraren da ba su dace ba. Wannan ne ya jaza yin tarurruka guda uku a wurare da lokuta daban-daban. Taro na farko an yi shi ne a garin Bamako na qasar Mali daga 28 ga watan Fabrairu zuwa 5 ga watan Maris na shekarar 1966.

3.2 Samuwar Qa'idojin Rubutun Hausa

Yunqurin qa'idojin rubutun Hausa ya faro ne tun wajen qarni na 19. Lokacin da Schon (1885) da Robinson (1896) da sauransu suka fara neman hanyar bambanta baqaqen Hausa masu lanqwasa v x q da takwarorinsu na Ingilishi marasa lanqwasa b d k. Sai dai a wancan lokacin, rubutun Hausa bai sami sahihan qa'idojin rubutu ba, saboda a wancan lokaci rubutun yana xanye ne.

Bayan Turawan Ingila sun shimfixa mulkinsu a qasar Hausa, sai gwamnati ta rungumi al'amarin raya harshen Hausa da hannu bibiyu. Da farko ta mai da hankali ga sama wa harshen Hausa hanyar rubutu. Qa'idojin rubutun Hausa na

farko an rubuta su a shekarar 1910. Bayan haka, an sake bitar waxannan qa'idojin har sau biyu; a shekarar 1932 da shekarar 1958.

Bayan samun mulkin kan Nijeriya, sai al'amarin daidaita qa'idojin rubutun Hausa ya koma ga hannun jami'o'i da qungiyoyi masu zaman kansu, kamarsu O.A.U. da UNESCO. Saboda haka, bitar qa'idojin rubutun Hausa ta ci gaba a qarqashin waxannan shika-shikai. An yi tarurrukan daidaita qa'idojin rubutun Hausa har sau huxu, a lokuta daban-daban, kamar haka:

i Taron BAMAKO, 28 ga watan Fabrairu, zuwa 5 ga watan Maris, 1966. An yi shi a qarshin inuwar UNESCO.

ii Taron Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya, 21 ga watan Yuni 1970.

iii Taron Kwalejin Abdullahi Bayero Kano, watan Satumba, 1972. wadda daga baya ta zama cikakkiyar Jami'a wajen 1975 – 6.

iv. Taron jami'ar Yamai, 7–12 ga watan Janairu, 1980, wanda aka yi qarqashin inuwar O.A.U. (Yahaya 1988:124-140),

Taro na qarshe, an yi shi da nufin kusantar da rubutun Hausa a Jamhuriyar Nijar ga rubutun Hausa a Nijeriya. Qa'idojin da aka yi matsaya a kan su a wannan taro, su ne qa'idojin rubutun Hausa a yau.

Qa'idojin rubutun Hausa sun daxe qunshe a cikin qamusoshi da mujallu, lokaci mai tsawo. Ba su fara bayyana ba don karantarwa a makarantu, sai lokacin da Galadanci (1976) ya wallafa littafin An Introduction to Hausa Grammar wanda ya qunshi wani babi a kan qa'idojin rubutun Hausa. Daga nan aka ci gaba da samun babobi game da qa'idojin rubutun Hausa a cikin littattafan nahawu; misali, Yahaya (1992) da Newman (2000) da Jaggar (2001) da sauransu.

3.3 Ci gaban da Rubutun Hausa ya Samu

Bayan wannan gwagwarmaya da rubutun Hausa ya sha a kan hanyarsa ta samuwa da daidaituwa, rubutun ya samu havaka da bunqasa a ciki da wajen qasar Hausa. Xaya daga ciki manyan ci gaban da rubutun Hausa ya samu shi ne na

amfani da shi a harkokin gwamnati kamar rubuta kundin tsarin mulkin Nijeriya da rubuta hukunce-hukuncen da alqalai suka zartar, musamman ma a Arewacin Nijeriya da sauran makamantansu. Ashe amintar da hukuma ta yi a yi amfani da rubutun Hausa ba qaramin ci gaba ba ne ga rubutun Hausa.

Rubutun Hausa ya samu damar kutsawa cikin al'amuran ilimi a duniya, domin kuwa ba a jami'o'in qasar Hausa kawai ba kusan a duk jami'o'in da ake nazarin harshen Hausa a duniya ana amfani da rubutun Hausa wajen gabatar da muqalu har ma da kundayen bincike.

Haka nan rubutun Hausa ya samu shiga kafofin yaxa labarai na duniya domin kuwa akwai kafofin yaxa labarai na qasashen duniya da suke amfani da harshen Hausa don yaxa labaransu. Bayan haka akwai ma jaridu da mujallu na sauran qasashen duniya da suke rubuta labaransu ta amfani da rubutun Hausa domin yaxawa ga al'umar qasashensu masu amfani da harshen Hausa da ma sauran al'umar duniya. Misali akwai jaridar Ad-da'awa al-Islamiyya wadda jam'iyyar da'awa ta duniya take bugawa a cikin wasu manyan harsuna na duniya ciki kuwa har da harshen Hausa. Kuma gidan radiyon Misira (Egypt) da suke gabatar da wani shiri na koyon harshen Larabci (Arabic By Radio) su ma suna fassara littattafan da suke amfani da su da harshen Hausa.

Rubutun Hausa ya samu karvuwa ga mawallafa na duniya baki xaya domin kuwa akwai abubuwa da dama a fannonin rayuwa, kamar allunan tallace-tallace (Billboards) da fasta-fasta ta siyasa da tallace-tallace da wayar da kan jama'a da fannonin kiwon lafiya duk ana amfani da rubutun Hausa wajen wallafa su. Ba kawai ma sauran vangarorin rayuwa ba hatta manyan litattafai na addinin Musulunci da na addinin Kirista, kamar Alqura'ani mai girma da Attaura da Zabura duk an fassara su zuwa harshen Hausa ta amfani da rubutun harshen. Sannan ga 'yan takardu da ake bugawa don yin nasiha da yaxa addinai ana rubutu su ta amfani da rubutun Hausa.

Wani abin ban sha'awa akwai wayar hannu (salula) da kamfanin Nokia ya yi mai xauke da bayanan sarrafawa da rubutun Hausa. Haka nan ma qasar Saudiyya tana amfani da rubutun Hausa wajen faxakar da mahajjata da yi masu maraba a yayin aikin hajji, misali a wurin jifar Jamori an rubuta

Shaixan Qarami Shaixan Na Tsakiya Shaixan Babba

(Bunza 2002:206).

Rubutun Hausa ya samu shiga cikin duniyar intaneti inda akan samu shafuka da suke bayar da bayanai da Hausa, don haka dukkan bayanan da irin waxannan shafuka suke samarwa suna samar da su ne a cikin rubutun Hausa. Baya ga wannan an samu ci gaban samar da rubutun Hausa a kwanfuta. Wannan namijin qoqari da Uba Abdalla ya yi ya samar da tsarin rubutu har iri biyu; wato Rabi'at Muhammad da Uba Abdalla. Aikin na Abdalla ya qara sanya rubutun Hausa shiga a dama da shi cikin harkoki na zamani domin a yanzu ana iya rubutun Hausa ta amfani da waxannan tsarin rubutu (fonts) da dukkan haruffan da ke a cikin abjadinta.

3.4 Ma'anar Rubutu

Kamar yadda aka yi bayani a (Greenberg 1960:208-208) da kuma (Abubakar 1972:424-426) asalin kalmar karatu daga harshen Kanuri, wato Barbarci take (Zarruq – babu ranar bugawa). Rubutu dai wata dabara ce ta yin amfani da wasu alamomi da za su wakilci magana. (Bunza 2002:1). Qamusun Hausa (2006:347) ya bayya rubutu da "Zanen magana a kan takarda ko allo ko wani bigire". Shi kuwa Mukhtar (2010:1) cewa ya yi:

> *Wata hanya ce da al'umma masu amfani da harshe xaya da al'adu kusan irin xaya takan ware da nufin amfani da ita a matsayin wakiliyar magana ta fatar baki. Wannan hanya, ta qunshi wasu alamu waxanda za a gani kuma a yi amfani da su a madadin magana ta fatar baki domin isar da saqo.*

Haka nan kalmar rubutu tana nufin dukkan wani abu da aka yi amfani da alqalami, ko da yatsa ko wani abin rubutu aka zana ko aka rubuta a bisa takarda ko

qasa ko wani abu wanda zai iya xaukar rubutu kuma za a iya gani a zahiri wanda kuma yake xauke da ma’anar da za a iya fahimta idan an karanta shi. A taqaice dai rubutu qoqari ne na wakilta magana ta fatar baki ta amfani da wasu alamomi.

3.5 Muhimmancin Rubutu

Rubutu a kowane harshe yana da matuqar muhimmanci. Baya ga kasancewarsa abin tinqaho ga harshen, domin kuwa ba kowane harshe ba ne yake da hanyar rubutu. Sauran muhimmancin rubutu sun haxa da:

Wakiltar Zance

Rabutu dai yana wakiltar zance ne ma’ana za a iya alamta abin da ake furtawa da baka ta hanyar rubutu. Dukkan abin da wani ya faxa ana iya wakilta shi a rubuce domin isar da saqo ga wanda ba ya kusa da mai zancen.

Xaukaka Harshe

Dukkan harshen da yake da tsarin rubutu yakan samu xaukaka fiye da takwarorinsa waxanda ba su da tsari ko hanyar rubutu. Da rubutu ne manyan harsuna irinsu Ingilishi da Larabci suka samu xaukaka a duniya. Ba sai an je da nisa ba, samun tsarin rubutu ne ya xaukaka harshen Hausa a kan sauran harsuna a wannan qasa.

Haka kuma da tsarin rubutu ne ake iya nazarin harshe ta hanyar sama masa nahawu da kuma rubutaccen adabi

Isar da Saqo Cikin Sauqi

Ana iya isar da saqo ga wanda ba ya kusa ta hanyar rubutu. Wannan yana nufin ana iya samun sadarwa a tsakanin al’umma ba tare da sun haxu da juna ba ta hanyar rubutu. Haka nan akan iya barin saqo na lokaci mai tsawo a tsakanin wanda ya shuxe da wanda ma bai zo duniya ba. Ta hanyar rubutu ne saqonnin manzannin da suka gabata suka samu isowa wannan zamani da muke ciki bayan dubunnan shekaru da shuxewar su. Ta hanyar rubutu ne za a iya qulla yarjejeniya tare da

adana ta na lokaci mai tsawo. Haka nan ana iya adana muhimman bayanai da suka haxa da tarihi ta hanyar rubutu.

Bunqasa Adabi

Rubutu yana taimakawa wajen bunqasa da yaxa adabi, musamman ma a wannan zamani da ake iya samar da bayanai a yanar intanet. Dukkan ire-iren bayanan da ake samarwa ana samar da su ne a rubuce. Haka nan ma littattafai na zube da wasan kwaikwayo da rubutttun waqoqi na samar da su ne ta hanyar rubutu. Ke nan rubutu ya zama wata muhimmiyar hanya ta yaxa al'adu da buqasa su.

3.6 Ma'anar Qa'idojin Rubutu

Ita kuwa kalmar 'qa'ida' na nufin tsararriya ko amintacciyar hanyar gudanar da wani abu. Don haka qa'idar rubutu ita ce wata tsararriyar hanyar gudanar da rubutu wadda aka aminta da ita wajen rubutu a harshe. Ana bukatar qa'idar rubutu ta kasance akwai daidaito a cikinta, ma'ana kowane mai rubutu a cikin wannan harshe yana amfani da ita.

3.7 Muhimmancin Qa'dojin Rubutun Hausa

Qa'idojin rubutu suna da matuqar muhimmanci ga rubutun Hausa, domin kuwa idan da babu su babu wani ma'auni da za a iya auna rubutun Hausa da shi bare ma a iya gane cewa daidai ne ko akwai kuskure. Ashe su ne ma'aunin gane kurakurai a cikin rubutu da hanyoyin da za a iya yin gyara. Sauran muhimmancin qa'idojin rubutu sun haxa da:

Fito da Ma'anar Kalmomi

Samuwar qa'idojin rubutun Hausa ya warware wasu daga cikin matsalolin yadda ya kamata a rubuta wasu kalmomi. Irin waxannan qa'idoji ne suka warware matsalar bambancin da ake samu a rubuta wasu kalmomi da suke xauke da haruffa masu qugiya da takwarorinsu masara qugiya. Ya kamata mai rubutu ya yi la'akari da baqaqe masu lanqwasa, ya kuma ba su haqqinsu a yayin rubutu. Rashin yin

lamqwasa a kan v da x da q yana iya canza ma'anar kalmar da aka rubuta (Sa'id 2004:4), misali, baki da baqi.

Fito da Ma'anar Jimloli.

Haka nan ma samar da qa'idojin rubutu ya bambance muhallan da ake haxe kalmomi da inda ake rabewa. Don haka an sauqaqe matsalar samun jimloli masu kama da juna, misali;

a Ko yi da mutum yana da kyau?

Koyi da mutum yana da kyau.

b Itace ta kwaso.

Ita ce ta kwaso.

c An sa mu hanya.

An samu hanya.

Haka nan an warware matsalar kalma ko jimla, wato dai kalma xaya ce ko biyu ko kuma jimla ce aka rubuta, misali

Abarshi ya saki matarsa.

A bar shi ya saki matarsa.

Kyautata/ Inganta Sadarwa

Samuwar qa'idojin rubutu ne ya sanya har ake iya gane kuskure ko rashin sa a cikin rubutu, da babu qa'idar rubutu to da kome aka rubuta daidai ne. Samuwar qa'idojin rubutu ne ya haddasa wannan bincike da aka gudanar, kuma shi ne ya bambanta masanin qa'idojin da akasinsa. Ashe samuwar qa'idojin ce take iya sanyawa a ce wannan rubutun ya yi daidai wancan kuwa bai yi ba, kenan tana kyautata rubutun harshe. Haka nan rubutun da aka yi a bisa qa'ida ya fi sauqin karantawa da fahimta fiye da wanda aka sava qa'ida a cikinsa.

Xaukaka Harshe

Samuwar qa'idojin rubutu yana qara xaukaka harshe. Xaya daga cikin manyan dalilan da suka sanya harshen Hausa ya samu bunqasa ita ce ta samuwar

rubutu da kuma qa'idojinsa. Wannan ne ya bayar da damar yin nazarin harshen da kuma ba harshen damar yin gogayya da sauran harsuna na duniya waxanda suke iya tinqaho da wata hanya ta rubutu.

Kafa Harshen Qasa

Harshen Hausa yana xaya daga cikin manyan harsuna guda uku da aka amince da a yi nazarin su a makarantun qasar nan. Haka nan yana cikin harsunan da ake fassara al'amura na gwamnati a cikinsa. Wannan kuwa ya faru ne saboda harshen yana da hanyar da ake rubuta shi, kuma yana da shimfixaxxun qa'idojin rubuta shi.

3.8 Samuwar Jaridu da Mujallu a Qasar Hausa

Waxannan kalmomi na jarida da mujalla asalinsu kalmomin Larabci ne waxanda suke nufin labarai da bayanai da ake rubutawa ko ake bugawa, su fito da wani suna da aka ba jaridar ko mujallar a wani kayyadajjen lokaci, kullum-kullum ko mako-mako ko sau biyu a wata ko a wata-wata ko sau huxu a shekara ko kuma a shekara-shekara (Gidan Dabino 2004:394). Jaridu da mujallu dai wasu vangarori ne na kafafen yaxa labaru, waxanda ake amfani da su don samar da bayanai a kan abin da ya shafi al'umma. Waxannan kafafe suna taka muhimmiyar rawa a rayuwar al'umma, musammam ma waxanda suke da ilimin zamani; wato waxanda suke iya karatu, domin kuwa suna gabatar da labaransu ne a rubuce domin karantawa. A bisa tarihi jaridu sun riga mujallu fara samuwa a qasar Hausa.

3.8.1 Jaridu

Tun da ake yin rubuce-rubuce a qasar Hausa, kafin qarni na ashirin, ba a nuna samuwar jarida ko mujalla ba don wayar da kan jama'a ko kuma don sadarwa a tsakanin mutanen (Bunza 2009:23-24). A qasar Hausa akwai rubuce-rubuce waxanda suka yi kama da jaridu da mujallun zamani, waxanda suke qunshe da labaru da wasiqu da hikayoyi da shaguve da ra'ayoyi da siyasa da mulki da kimiyyar magunguna da tattalin arziki da kuma zaman iyali. Akwai kuma waxanda

ake haxa harsuna biyu ko ma ukun gaba daya, sai dai suna zagayawa a tsakanin malamai da sarakuna da mabiyansu ne kawai.

A cikin shekarar 1859 ne aka fara samun jarida a Nijeriya inda wani Rabaran Henry Townseed ya fara buga jarida ta farko mai xauke da harsuna biyu (Ingilishi da Yarabanci) mai suna Iwe Irohin. Ko da a cikin rubutun boko ma ba a fara tsara jarida ana bugawa da harshen Hausa ba sai a cikin wannan qarni na ashirin, wato a wajen shekarar 1932, bayan an buxe makarantun ilmin boko a larduna, an kuma sami isassun masu iya karanta Hausa cikin rubutu lokacin ne jaridun Hausa suka fara bullowa (Gidan-dabino 2004:395).

Jaridar Hausa ta farko da aka fara bugawa a Arewa ita ce jaridar Nijeriya Ta Arewa mai shafi 22 a shekarar 1932. A lokacin ana sayar da ita sisi kuma a maxaba'ar Gwamnati da ke Kaduna ake buga ta. Ita ma tana fitowa a cikin harsunan Ingilishi da Hausa da Larabci, a jere cikin shafuka tare da hotuna a wasu shafukan, kowane vangare da sunansa, ta Hausa an kira ta da Jaridar Nijeriya Ta Arewa ta Ingilishi kuma Northern Provinces News ta Larabcin kuwa Jaridat-Al-Nijeriya Al-Shimaliyya.

Bayan mutuwar wannan jarida sai aka sami vullowar wasu jaridu guda biyu, wato Daily Mail da Daily Comet waxanda ake wallafawa da harshen Ingilishi. Duk da yake jaridun ba a cikin harshen Hausa suke ba, amma suna qunshe da wasu labarai a cikin harshen Hausa a wasu daga cikin shafukansu. Su dai waxannan jaridu hada-hadar siyasar jamhuriya ta farko da ta gudana a tsakanin jam'iyyar NEPU da jam'iyyar NPC ce musabbabin samuwarsu. 'Yan jam'iyyar NPC wadda take da goyon bayan gwamnati suka yi amfani da jaridar Daily Mail wajen yaxa manufofinsu da yin farfagandar siyasa. Ita kuwa jam'iyyar NEPU mai cibiya a Kano ta yi amfani da jaridar Daily Comet, kuma wannan ne ya sa jaridar wadda ake bugawa a Legas ta buxe reshenta a Kano (Yahaya 1988:141/Bunza 2009: 25).

Aikin jarida ya qara faxaxa a Arewacin Nijeriya, saboda haka a shekarar 1939 aka yanke shawarar qago jarida don a riqa yaxa ta lardi-lardi don a wayar da kan jama'a game da abin da ke faruwa a cikin qasa da kuma qasashen waje, musamman ma da yake a cikin wannan shekara ne yaqin duniya na biyu ya varke. wannan jarida ita ce 'Gaskiya Ta Fi Kwabo. A watan Janairu na 1939 aka fara buga ta, Editanta na farko shi ne marigayi Dr. Abubakar Imam, mataimakinsa kuwa shi ne Mr. Gilas. Ma'anar sunan jaridar shi ne gaskiyar da ake faxa a cikinta, ta fi kwabon da za a saye ta. A shekarar 1941 ne aka vullo da wata jarida mai suna Suda don ta riqa bayar da labarun yaqe-yaqe, musamman na qasashen waje.

An kafa Hukumar talifi ta jihar Arewa wato 'Northern Reginal Literature Agency' (NORLA) a shekarar 1941, daga cikin ayyukan hukumar akwai shirya waxansu jaridu cikin harshen Hausa da wasu harsuna domin amfanin larduna. Misali:

Jaridar Zaruma	lardin Sakkwato
Himma	lardin Katsina
Gamzaki	lardin Filato
Zumunta	lardin Bauchi
Bazazzaga	lardin Zazzau
Haske (ta farko)	lardin Neja
Arxo	lardin Adamawa
Albishir	lardin Borno
Sodangi	lardin Kano.

Akwai kuma wasu jaridu da ake bugawa don 'yan makaranta da sauran masu sha'awar karanta Hausa, Jaridun su ne Jakadiya da Aboki da Majalisarku da kuma mujallar Alfijir wadda take bayanin yadda ake gudanar da sana'o'i. A tsakanin shekarun 1953 zuwa 1959, lokacin da hukumar NORLA take aiwatar da ayyukanta

na rubuce-rubuce don wayar da kan jama'a, waxannan jaridu sun yi tashe, amma da rufe hukumar Norla su ma jaridun suka vace (Gidan Dabino 2004:396)

3.8.2 Bunqasar Jaridu Da Mujallu A Arewacin Nijeriya

A sakamakon rufe hukumar Norla jihar Arewa ta shiga halin ni-'yasu ta fannin jaridu domin sai da ya zama babu wata jarida a Arewa in baya ga jaridar Gaskiya Ta Fi Kwabo. Daga baya sai aka yi ta samun sababbin jaridun Hausa. A shekarar 1980 jaridar Maganar Kano ta bayyana, kamfanin Sarkimedia ne suke buga ta, amma ba ta fi shekara biyu ba aka daina jin xuriyarta. A dai wannan shekarar jaridar 'Yancin Xan'adam ta fito da kuma takwararta ta Turanci wato 'Nigerian Standard' dukkansu ba su wuce shekara huxu ba suka vace.

Kamfanin jaridar Concord ya fara buga jaridar Amana a cikin shekarar 1981, wadda ake bugawa a Zariya, ita ma sai aka wayi gari babu amo ba labari. A dai cikin wannan shekara ta 1981 gwamnatin jihar Kano ta kafa kamfanin Triump, su ma suka fara buga jaridar Albishir ta Hausa da kuma ta ajami mai suna Alfijir. A shekarar 1985 waxannan jaridu aka haxa su waje xaya, vangare xaya Hausa xaya vangaren kuma ajami. Jaridar Zuma ta fito a shekarar 1982, wadda kamfanin buga jaridar Telex yake bugawa, kuma ya samar da wata mujalla ta Musulunci wadda ake kira Nasiha, mai bayar da bayani a kan harkokin addini da wasu matsaloli na yau da kullum. Mujallar Abokiyar Hira wadda kamfanin Albah suka fara bugawa ta fito sau xaya a shekarar 1987 daga nan ba ta sake fitowa ba (Gidan Dabino 2004:397). Ya zuwa akwai jaridu da suke wallafa labarai da harshen Hausa daga ciki akwai jaridar Rariya da Leadership Hausa daAminiya da Gamzaki. Haka nan akwai waxanda suke xauke da labarai da suka shafi addinin Musulunci kamar su Almizan da At-tatbiq da sauransu.

3.8.3 Mujallu

Ita dai mujalla yawancin bayanan da suke a cikinta sun shafi wayar da kan jama'a ne a kan abin da ya shafi rayuwarsu ya Allah ko dai yadda ake qera wata

na'ura ko sarrafa ta ko yadda ake gudanar da wata sana'a ko al'ada ko xabi'un wata halitta ko tarihin kafuwar wata al'umma da sauran makamantan su. Babu wani bayani wanda yake nuna samuwar wata mujalla kafin shekarar 1953.

Mujallar Alfijir wadda ta riqa fitowa sau xaya a kowane wata tare da hotuna masu kyau, ita ce mujalla ta farko wadda aka fara bugawa a cikin harshen Hausa a shekarar 1953, kuma Hukumar Yaqi da Jahilci Ta Arewaci Nijeriya (NORLA) ce take buga ta. Ana buga ta a kamfanin Gaskiya da ke Zariya don sayarwa a ko'ina a kan kuxi nai-nai. A qarshen shekara kuma sai a tara dukkan fitowa sha biyun a buga su a wuri xaya tare da yi masu bango mai kauri ana sayarwa sule tara (Bunza 2009:28).

Kamfanin Soyayya Communication, sun fara buga mujallar Ruwan Zuma wadda take bayar da labarai cikin hotuna ne a shekarar 1991, dalilin kafa wannan mujalla shi ne don a samar da abin karatu da kuma nishaxantarwa, ganin a lokacin mujallar Ikebe Super ta mamaye Hausawa. Da ta mutu sai editanta ya kafa wata mujallar mai suna Tambari, ta fito a shekarar 1992, ita kuma tana bayar da labarai na ban dariya a cikin zanen hotuna. A shekarar 1992 aka kafa mujallar Gwagwarmaya ta 'yan'uwa wadda kamfanin I.M. Publication da ke Zariya suke bugawa. Mujallar Matambayi ta zo a shekarar 1993, wadda ita ma take bayar da labaru masu xauke da hutuna na zane. Muryar Bebeji kuma ta bayyana a shekarar 1994, wadda Sashin Yaxa Labaru da Al'adu da ke Ma'aikatar Kyautatuwar Zaman Jama'a ta Karamar Hukumar Bebeji suke bugawa. Kamfanin Al-kalam Communication Ltd., Kaduna, sun fito da mujallar Tambari a shekarar 1995. Jaridar Muryar 'Yan Kasuwa mai bayar da labarun harkokin kasuwanci wadda qungiyar 'yan kasuwar Sabon Gari suka xauki nauyi, ta fito a shekarar 1995, Jaridar Haske Maganin Duhu kuwa ta fito ne don faxakarwa ga masu amfani da wutar lantarki, a shekarar 1998 aka fara ta, kamfanin Haske Maganin Duhu da haxin gwiwar Sashin Wayar da Kai Da Yaxa Labarai na Ma'aikatar NEPA da ke

Shiyyar Kano suke bugawa. A shekarar 1999 qungiyar Kula Da Kare Haqqin Xan'adam ta Nijeriya (Human Rights Monitor) wadda take a Jihar Kaduna suka fito da wasu mujallu guda biyar, wato Muryar Mata da Dimokuradiyya Mata da Lura Da 'Yancin Shari'a da Jinsi Da Addini da kuma Shaida. Akwai Kakakin NOA wadda Hukumar Faxakarwa Ta Qasa reshen Jihar Kano take bugawa.

A yanzu akwai jaridu da mujallu masu bayar da labaran yau da kullum kimanin guda goma sha bakwai waxanda suke fitowa kowanne lokaci, akwai Almizan da At-tajdid da Gamzaki (sabuwa) da Sawaba Albishir (sabuwa) da Alfijir (sabuwa) da At-tatbiq da Bazawara da Gaskiya Ta Fi Kwabo da Manuniya da Magama da Sakon Zamfo da Zavi Sonka da Alfurqan da Alburhan da kuma Hantsi. Sannan akwai guda takwas masu fitowa jefi-jefi, kamar Adala da Ar-Risala da Al-Ihsan da Al'aqeedatus Sahiha da Haske Maganin Duhu da Taskira (sabuwa) da Jakadiya (Sabuwa) da kuma Dillaliya (sabuwa) (Gidan Dabino 2004:398). Har yanzu akwai mujallu da suke fitowa lokaci-lokaci kamar mujallar Kunnen Gari da Muryar Arewa da mujallar Fim. Bayan nan akwai ma waxanda wasu hukumomi na qasashen duniya suke wallafawa, misali akwai Mujallar Magama ta Ofishin Jakadancin Amirka A Nijeriya. Haka nan akwai na kiwon laffiya kamar mujallar Kulawa.

3.9 Allunan Tallace-Tallace (Billboards)

Akwai hanyoyi da dama da masu talla (musamman na zamani) kan bi wajen tallata hajarsu. Xaya daga cikin waxannan hanyoyin ita ce ta amfani da harshe (a rubuce). Wannan kan taimaka wajen jnyo hankalin mai saye (Abdulmumini 2010: 52-53) daga cikin bigiren da ake amfani da rubutu a fagen talla shi ne ta amfani da allonan talla. Allunan talla dai takardu ne manya da qanana da ake amfani da su domin tallata wani abu ko don yin sanarwa a game da wani abu. Akan yi amfani da irin waxannan takardu a manyan alluna da akan sanya a gefen tituna don bayar da sauqin karantawa ga matafiya, wasu kuma akan liqa su a jikin bango wasu kuma

akan raba su domin karantawa. Hanyoyi ne na yin talla a cikin rahusa domin kuwa ba su kai tsadar yin talla a gidan radiyo ko talabijin ko jaridu da sauransu ba.

Fasta-fastar da ake amfani da su a ma'aikatun lafiya da na siyasa da na tallace-tallacen kamfanoni suna daga cikin irin waxannan takardu, sai dai kawai fasta-fasta sun fi qanqanta a kan irin waxanda akan sanya a gefen tituna

3.9.1 Ire-Iren Allunan Talla

Akwai ire-iren allunan talla (Bill Boards) da dama wasu na manyan katakai ne waxanda akan kafa su a gefen tituna a garuruwa, wasu kuwa na takardu ne da akan liqa su a jikin bangaye. Haka nan akwai waxanda suke liqe a jikin motoci da waxanda ake rarrabawa domin isar da saqonni zuwa ga jama'a. (http://www.oohinternational.com)

Na Katako

Su dai ire-iren waxannan alluna manya ne da akan kafa a gefen tituna ta yadda masu wucewa za su iya karantawa. Ana amfani da irin waxannan alluna don yin talla ya Allah ta ababen masarufi ko ta 'yan takarar siyasa ko faxakarwa ko wayar da kan al'umma a kan wani al'amari na kiwon lafiya ko wani shiri wanda gwamnati take da niyyar aiwatarwa

Akan shirya ire-iren waxannan ne ta yadda za su xauki hankalin masu wucewa, kuma akan yi masu manyan rubutu ne kuma marasa yawa ta yadda masu wucewa, musamman a bisa ababen hawa za su iya gani su kuma karanta su daga nesa kuma a cikin kyaftawa da bisimilla, (rataye na 1)

Takardu (fasta)

Irin waxannan takardu suna xauke ne da hotuna, kuma ana amfani da su ne, musamman don liqawa a jikin bangaye. Su ma ana amfani da su don yin tallace-tallace. Irin waxannan takardu 'yan siyasa suna amfani da su domin tallata jam'iyyu da 'yan takararsu, (rataye na 2).

Qananan Takardu (flyers/pamplates/coupons)

Ana amfani da irin waxannan takardu ne domin sanarwa ko yin bayani a game da wani al'amari, misali faxakarwa a game da wani abu da ya shafi kiwon lafiya ko wayar da kan al'umma, ko kuma wani taro na qara wa juna sani da sauran makamantansu. Irin waxannan takardu akan yi su ne falle xaya, kuma ana rarraba su ne ga jama'a ko liqawa a wajen taruwar jama'a kamar makarantu ko kasuwanni da saurnsu.

3.9.2 Muhimmancin Allunan Tallace-Tallace

Allunan tallace-tallace suna da matuqar muhimmanci, musamman a wannan zamani. Gwamnatoci da 'yan siyasa da 'yan kasuwa duk suna amfani da su domin tallata abin da suke son tallatawa ga al'umma. Daga cikin muhimmancinsu akwai

Wayar da kai da faxakarwa

Akan yi amfani da irin waxannan alluna domin faxakarwa da kuma wayar da kan jama'a, musamman a game da abin da ya shafi kiwon lafiya da kuma wasu manufofi na gwamnatoci. Misali akwai alluna masu wayar da kan al'umma a game da illar shan taba da cutar qanjamau da zazzavin cizon sauro da kula da mata masu juna biyu da alluran rigakafi da sauran su (rataye na 3).

Tallata Abin Sayarwa

Kamfanoni suna amfani da allunan talla wajen tallata hajarsu. Ta haka ne mutane suke samun sahihan bayanai a game da abin da ake tallatawa. Misali kamfanonin sadarwa na wayar tafi-da-gidanka (salula) sun fi amfani da wannan hanya wajen tallata ayyukasu na sadarwa da kuma bayyana wa jama'a yadda za su ci moriyar waxannan shirye-shirye (rataye na 4).

Samar da Bayanai

Ana samun bayanai a game da sababbin abubuwa na zamani. Ba wannan kawai ba har ma 'yan siyasa suna amfani da wannan hanya domin tallata 'yan takararsu tare da yaxa manufofin jam'iyyunsu. Ta haka ne ma sauran jama'a za su gamsu da manufofin har su jefa masu quri'arsu a lokacin zave.

Qawata Muhalli

Allunan talla, musamman manya waxanda ake kafawa a manyan birane sukan qawata wurare, musamman da dare. Akan yi amfani da fanti mai xaukar ido a jikin irin waxannan alluna. Haka nan akwai na zamani waxanda ake haxa wa wutar lantarki domin bayar da haske tare da yi masa launi iri daban-daban.

Hanyar talla mafi sauqi

Talla ta yin amfani da allunan talla ta fi kowace hanya ta zamani sauqi ta fuskar kashe kuxi domin idan aka kafa allon talla yakan xauki tsawon lokaci (aqalla sati shida) kafin a cire shi. A domin haka ne al'umma da dama za su samu damar karantawa, ba kamar talla a kafafen yaxa labarai irin su su talabijin da radiyo ba waxanda sai wanda yake da kusanci da su ne kawai zai iya sanin an yi talla a cikinsu ko kuma wanda yake tare da su ne a lokacin da aka yi tallar zai iya sanin abin da ake yi.

3.10 Naxewa

A wannan babin an yi waiwaye a game da rubutun Hausa inda aka waiwayi samuwar rubutun boko a qasar Hausa da irin nasarorin da rubutun ya samau da daidaita qa'idojinsa. Haka nan babin ya kawo ma'anar rubutu da muhimmancinsa da muhimmancin yin amfani da qa'idojin rubutu. Sannan an kawo taqaitaccen bayani a kan samuwar jaridu da mujallun Hausa da kuba bayanin allon talla da ire-irensa da muhimmancinsa.

BABI NA HUXU

YANAYIN KWAMACALA A RUBUTUN HAUSA

4.0 Gabatarwa

Kamar yadda yake a dukkan rubutu na harsuna, rubutu a harshen Hausa yana tattare da wasu qa'idoji. Wato dai ba ana yin sa kara zube ba ne. Kamar yadda Mukhtar (2010:1) ya bayyana cewa,

> *Rubutu yana tare da wasu dokoki da qa'idoji, kama tun daga kan haruffa (baqaqe da wasula) har ya zuwa kan gina gavovin kalma da samar da kalmomi daban-daban da kuma jimloli. Har ila yau yana tattare da qa'idoji na haxewa da raba kalmomi tare da amfani da sauran alamomi, kamar aya da waqafi da ayar tambaya da ta motsin rai, da sauransu.*

Don haka ya zama wajibi mai rubutu ya kiyaye waxannan qa'idoji. Qa'idar rubutu ta qunshi abubuwa da dama, tun daga yadda ake rubuta kalmomi da muhallin haxewa ko rabawar kalmomi da kuma yadda ake amfani da alamomin rubutu. Ya zama wajibi ga mai rubutun Hausa ya fahimci halayen rubutacciyar magana da iya amfani da ita yadda ya kamata, sannan iya san iyakacin haruffan da ake amfani da su a rubutun Hausa, kuma ya iya karanta Hausa cikin sauqi ya kuma iya rubuta ta bisa qa''ida domin isar da saqo daidai (Yakasai da Muázu 2010)

Rashin kiyaye qa'idojin rubutu yakan haifar da kwamacala. Qamusun Hausa (2006:262) ya bayyana kwamacala da 'Hargitsa abubuwa iri daban-daban'. Wato dai hargitsa abubuwa ba a bisa qa'ida ba. Kwamacala a nan na nufin yin rubutu ba tare da bin qa'idar da aka shimfixa ta yin sa ba. Manufar amfani da qa'idojin rubutu ita ce tabbatar da ma'anar abin da ake rubutawa ba ta sauya ba. A nan abu biyu na iya faruwa a sanadiyyar rashin kiyaye qa'idojin rubutu. Abu na farko shi ne sauyawar ma'ana na biyu kuwa shi ne salwantar ma'anar baki xaya. Misali

sauyawar muhallin harafi ko gava ko kalma a ciki rubutu yakan iya sauya ma'ana a cikin rubutu. Misali:

Sa mata kai biyu (a sanya wa wani abu (jinsin mace) wani abu mai kai biyu).

Sa matakai biyu (a sanya mataki guda biyu).

Sama ta kai biyu (samaniya ta kai adadin biyu).

(Sa'id 2004:11)

Ga wani misalin kuma.

Tafi tsare shi	je ka tsare shi (go and protect/defend him)
Ta fi tsare shi	tsaron da ta yi masa ya fi na sauran (she protect him well)
Ta fitsare shi	ta yi masa fitsari (she has urinated on him)

(Ado da Rabeh 2008:3)

Haka nan abin yake a waxannan misalai,

Ba shi(give him)	bashi (loan)
Ku sato (you (pl) should steal)	kusato (come closer)
Ya qi (he refused)	yaqi (war)
Ya ji (he heard)	yaji (pepper) (Hassan 2010:15)

Wani qarin misalign kuma shi ne:

Ta je fadama	(She has gone to the marshy low-lying land)
Ta je fa dama	(She has also been to the place)
Ta je fada ma	(She has already gone)
Taje fa dama	(Comb to the right)

Wani lokaci ana iya samun sauyawar ma'ana a dalilin rashin amfani da alama a cikin rubutu. Misali:

Matarsa ta haihu **ya** mace (matarsa ta haihu, amma abin da aka haifa ya mutu)

Matarsa ta haihu '**ya** mace (matarsa ta haifi xiya mace)

Babbar matsalar da ake fuskanta a fagen rubutun Hausa ita ce ta kasa tantance qa'idojin rubutun, don haka sai a yi ta samun kwamacala. Wani lokaci ma sai a rubuta wani abu daban da abin da ake tunanin an rubuta, daga qarshe sai ya kasance ba a samu isar da saqon da ake son isarwa ba. Abubuwan da ya zama wajibi a sani domin kauce wa irin wannan matsalar su ne sanin nahawun harshen Hausa da sanin inda ya kamata a haxe kalma ko kuma raba ta daga nan sai sanin yadda ginin kalmomin yake, sannan sai yin qoqarin amfani ko kiyaye qa'idar a yayin gudanar da rubutu.

Haka nan akwai bambanci a tsakanin Hausar baka (wadda al'umma suke amfani da ita a yau da kullum) da kuma rubutacciyar Hausa (wadda ta ginu a kan tsarin daidaitacciyar Hausa), misali,

Ya sai da gona yai aure (Hausar baka)
Ya sayar da gona ya yi aure (rubutacciya/daidaitacciyar Hausa)
(Hassan 2010:17)

Dokokin harshe sun taka muhimmiyar rawa wajen fitar da dokoki ko qaídojin rubutun Hausa. Waxannan dokin harshe sun haxa da na furuci da tsarin sauti da na ilimin qirar kalma da kuma na maána. Don haka duk abin da ba shi da ma'ana a kan kansa, to dole ne ya haxu da wani vangare na kalma ko wata kalma ko qwayar kalma a yayin rubutu (Yakasai da Mu'azu 2010)

Akwai matsaloli iri daban-daban da ake fuskanta a rubutun Hausa:

i matsalar raba kalma a muhallin da ake haxawa

ii matsalar haxe kalma a muhallin da ake rabawa

iii matsalar yadda ake rubuta kalmomi

iv matsalar amfani da alamomin rubutu

v matsalar rashin amfani da daidaitacciyar Hausa

vi samun savani a kan yadda ake rubuta kalmomi

Dukkan waxannann wurare ana samun matsalolin rubutu dangane da su a cikin litattafai da jaridu da mujallu da allunan talla da rubuce-rubucen da ake yi a jikin abubuwan hawa da ma sauran rubuce-rubuce na Hausa.

4.1 Littattafai

Ana samun matsaloli da dama da suka shafi qa'idojin rubutun Hausa a littattafai. Irin waxannan littattafai sun kama tun daga na zube har zuwa waxanda da aka yi don koyar da qa'idojin rubutu. Kodayake matsalolin da suke a cikin wasu littattafan sun fi na wasu yawa. Abin al'ajabi shi ne akan samu kurakurai da dama a littattafan da aka wallafa su don yin gyara ga matsaloli a rubutun Hausa waxanda masana ko masu ilimin qa'idojin rubutu suka wallafa. Irin wannan yakan zama mai dokar barci yana gyangyaxi ke nan. Kamar yadda aka ambata a baya, matsalolin da ake fuskanta sun haxa da:

i matsalar amfani ko rashin amfani da manyan haruffa

ii matsalar raba kalma inda bai dace ba

iii matsalar haxa kalma inda bai dace ba

iv rubutun Hausa da tsarin rubutun Ingilishi

v rashin amfani da daidaitacciyar Hausa

vi savanin yadda ake rubuta kalmomi

i Matsalar Amfani da Manyan Haruffa

Wannan matsala tana xaya daga cikin matsalolin da ake samu a cikin littattafai, wato wuraren da aka sanya babban harafi a maimakon qarami ko inda aka yi amfani da qaramin harafi a maimakon babba. Misali:

(1) *A farkon 1900 Gwamnatin Ingila ta karve ragamar mulki daga hannun sarakunan Hausawa.Gwamna Lugga shi ne aka* ***Xanqawa*** *ragamar 'yan Nijeriya ta Arewa.*
(Muhammed 2008:6)

(2) *A ganina an fara rubutun ajami tun gabanin* ***musulunci*** *ya zo qasar Hausa. Ai gabanin Musulunci akwai karatu da rubutu a qasar Hijaz. Ita qasar Hijaz, watau* ***saudiyya*** *ta yanzu, tun gabanin bayyanar addinin* ***musulunci*** *suna da hulxa da qasashen Afirika irin su Habasha, da Misra, da Morocco, da sauransu.*
(Bunza 2002:18)

A misali na 1 kalmar **Xanqawa** (danqa wa) kamata ya yi a rubuta ta da qananan haruffa, amma sai aka rubuta farkonta da babban harafi. Sannan an yi amfani da harafi **x** a maimakon harafin **d**. A misali na 2 kuwa kalmomin **musulunci** da **saudiyya** kamata ya yi a rubuta farkonsu da babban harafi don sunayen yanka ne.

ii Matsalar Raba Kalma Inda bai Dace ba

Wannan matsalar ta shafi raba kalma a muhallin da ya kamata a haxe ta. Ana samun irin wannan matsala a litattafai, har ma da littattafai masu koya ko bayani a kan qa'idojin rubutu. Kamar yadda aka ambata a baya, wannan yana iya sauya ma'anar saqon da ake son isarwa ko ma ya salwantar da ma'anar gaba xaya. Misali:

(3) *A wajen waqoqi kuma ya shirya littafin Tsofaffin Waqoqi Da Sababbin Waqoqi na Alh. Mudi Spikin da sauransu. Wannan Kamfani har yanzu yana nan kuma* ***ya na*** *ba da himma wajen bunqasa rubuce-rubucen Hausa. (Muhammed 2008:12)*

A misali na 3 an raba kalmar **yana** inda aka rubuta wakilin suna da manunin lokaci a matsayin kalmomi daban-daban. Sauran wuraren da aka samu irin wannan matsala a wannan littafin sun haxa da:

	kuskure	**daidai**	**shafi**
a	wata qila	wataqila	22
b	gab a	gaba	24
c	dab an-daban	daban-daban	30
d	wad annan	waxannan	30
e	many an	manyan	32,37
f	daidai ta	daidaita	36
g	sunan ta	sunanta	57
h	mots in	motsin	58
i	ya ke	yake	58
j	malamin sa	malaminsa	64

A wani misalin kuma:

(4) *Waxannan suka karanci Hausa cikin Ma'aikatun Hukuma **su kafi cancan ta** su yi wani abu a kan wannan. (Bunza 2002:201)*

A misali na 4 an raba kalmar **suka** da **cancanta,** sannan aka haxa **ka** (a matsayin manunin lokaci) da kalmar aikatau (fi)

iii Matsalar Haxa Kalma Inda bai Dace ba

Ita kuwa irin wannan matsala akasin wadda ta gabata ce wato ana haxa kalma a wurin da ya kamata a raba ta. Misali:

(5) *Bayan qarewar yaqi a 1945 sai Gwamna Rqhards na Nijeriya ya nemi Gwamnatin Ingila ta **baiwa** Hukumar Adabi taimakon kuxi... (Muhammed 2008:9)*

A nan haxa kalmar **bai** da **wa** yana iya sauya ma'anar kalmomin zuwa ma'anar mace mai mauta (**baiwa**). A maimakon a rubuta su a matsayin xaixaikun kalmomi. Wuraren da aka samu irin wannan matsala a littafin sun haxa da

	kuskure	**daidai**	**shafi**
a	Xanqawa	danqawa	9
b	kaucewa	kauce wa	16
c	Aina	A ina	57
d	akan	a kan	60
e	karanxori	karan-xori	62
f	dominjama'a	domin jama'a	64

A wani littafin da aka samu irin waxannan kurakurai kuma, ga misalin yadda ya bayyana:

(6) *Wannan ba yana nufin suka ga da'awar da muka ambata a lamba ta xaya ba. abin da marubucin **yafi** raja'a gare shi ne kawai. (Bunza 2002:42)*

A misali na 6 ma matsalar haxa wakilin suna zagin aikatau (ya) aka yi da kalmar aikatau (fi). Kowane rukuninsa daban anahawu don haka a rabe za a rubuta su a matsayin kalmomi daban-daban.

iv Rubutun Hausa da Tsarin Rubutun Ingilishi

Irin wannan matsala ita ce wadda ta shafi yin rubutun Hausa da tsari ko siga irin ta wani harshe daban, musamman ma Ingilishi. Misali:

(7) *Misali Mista Bergery ya rubuta Qamusan Hausa, 'Hausa Dictionary'.Sannan kuma ga Dictionary of Hausa Languages na R.C. Abraham. Awajen **Grammar**, kumaga Hausa Grammar na Robinson da kuma Yau da Gobe. na J. Lowry Maxwell, da sauransu da yawa.*
(Muhammed 2008:)

A wannan misali da ya gabata (na 7) kalmar '**grammar'** ya kamata a fassara ta zuwa '**nahawu'**, sannan a cire ayar da ta zo bayan 'Yau da Gobe'. Don haka jimlar ya kamata ta kasance: A wajen nahawu kuma ga 'Hausa Grammar' na Robinson da kuma 'Yau da Gobe' na J. Lowry Maxwell, da sauransu da yawa.

v Rashin Amfani da Daidaitacciyar Hausa

Sau da yawa karin harshe yakan bayyana a cikin rubuce-rubuce. Ita ma irin wannan matsala tana ruxa mai koyo ya kasa fahimtar wace ce daidaitacciyar Hausa, musamman idan littafin yana magana ne a kan daidaitacciyar Hausa ko qa'idojinta. A nan ana samun yin amfani da kalma ko jimla wadda ta sava daidaitacciyar Hausa. Ga misalin irin matsalar:

(8) *Ana cikin haka, a cikin 1939, sai yaqin Duniya na biyu ya tashi. Kuma Turawan Ingila suka shiga **xiban** sojoji daga Nijeriya don su taimake su yaqi… (Muhammed 2009)*
Sauran wuraren da aka samu irin wannan matsala sun haxa da:

	kuskure	**daidai**	**shafi**
a	cin gashin kanshi	cin gashin kansa	3
b	xiban sojoji	xibar sojoji	8
c	cikakken ma'ana	cikakkiyar ma'ana	60

(9) *Masana sun **daxa juna sani** wajen rubuta kalmomi masu gava xaya irin su: da wa YI SU Ga, cewa ko suda babban baqi ake fara harain farko ko qarami? Wasu da babba suke farawawasu da qarami. Abin buqata a **doge** da xay kar a **shirvata** su. (Bunza 2002: 119).*

A misali na 8 da na 9 an samu rashin amfani da daidaitacciyar Hausa a inda a misali na 8 aka sami **xiban sojoji** a maimakon **xibar sojoji**. A misali na 9 kuwa Karin harshen Sakkwatanci aka samu wato, "Abin buqata a **doge** da xay kar a **shirvata** su". Kamar yadda Hassan (2010:17) ya bayyana.

vi Savani

A wasu lokuta akan samu savani a kan abin da marubuci yake ambata a cikin bayaninsa, amma kuma a cikin misalan da yake bayarwa su sava wa bayaninsa. Wato dai bayani daban misali daban kamar yadda ya faru a misali na 10 da na 11:

(10) *Har ila yau, ana amfani da alamar aya tsakanin awa da minti na agogo. Misali **6:30**.*
Waxannan kaxan ne daga cikin jimlolin Hausa masu xauke da alamomin aya.
Qarshen magana duka, ana amfani da alamar aya wajen kawana zance wato kammalawa
(Muhammed 2008:57)

Haka nan a misali na 11, a shafi na 58:

(11) *A dukkan qarshen alamar mats in rai, babban harafi ne zai biyo baya. Akan yi amfani da alamar mots in tai maimakon alamar tambaya don nuna motsin rai wato wani hali ko yanayin da mai magana yake, ciki. Wani lokaci don nuna halin ba-zata. Wasu misallan alamomin motsin rai sun haxa da:*
Ah!, Ace!, Ashe!, Assha!, Haba!, Kai!, Kayya!, Kaico!, Madalla!, Maraba!, Tirqashi!, Tir!, Wash!, Oho!, Mts!, Yawwa!,
Dubi yadda ake amfani da alamar motsin rai a cikin jimla:
A ce! Na san zai aika.
Ah! har ka iso.
Ashe! kai ka ka zo.
(Muhammed 2008::58)

A misali na 11 an yi amfani da alamar motsin rai, amma haruffan da suka biyo bayan alamar suka kasance qananan haruffa ba kamar yadda aka yi bayani a cikin misalin ba, wato "*A dukkan qarshen alamar matsin rai, babban harafi ne zai biyo baya."*

vii Amfani da Jimloli Marasa Ma'ana

Wasu lokuta akan samu marubuci ya yi amfani da jimloli marasa cikakkiyar ma'ana ta yadda mai karatu zai samu matsala wajen fahimtar saqon da marubuci yake qoqarin isarwa. Mafi akasari rashin sake karanta abin da aka rubuta ne yakan hifar da irin wannan matsala, kamar yadda ya faru a misali na 12:

(12) *Kuma an zuba ido don ganin irin rawar da Kamfanin Gaskiya tare da na NNPC za su taka a wannan shiri.* ***Bayan da Ilimi kyauta ya yi masu wadata almajiran wannan shirin da isassun abubuwan karantawa na Hausa.***
(Muhammed 2008::13)

Sauran wuraren da aka samu irin wannan mtsala sun haxa da shafi na 35 da 46 da 51.

4.2 Jaridu da Mujallu

A jaridu da mujallu ma akwai matsalar sava qa'idojin rubutu na Hausa. Irin waxannan matsaloli iri xaya ne da waxanda ake samu a litattafai wato sava qa'idar haxe kalma ko rabawa da matsalar yadda ake rubuta kalmomi. Irin wannan matsala ta ratsa mafi yawa daga cikin jaridu da mujallun Hausa. Ga misalan ire-iren waxannan matsaloli:

4.2.1 Haxe Kalmomi

A nan marubuta sukan haxe kalmomi a wurin da bai dace ba mafi akasari sukan haxe kalmomin ne ta la'akari da yadda ake furta kalmomin ko kuma rashin sanin cewar kalmomin a rabe ya kamata su kasance ko la'akari da kasancewar xaya daga cikin kalmomin mai gava xaya ce. Daga cikin muhallan da aka fi samun irin wannan matsala akwai:

Mallaka

Kalmomin mallaka wasu kalmomi ne da suke nuna mallakar, wani abu da ake magana a kansa. Akwai hanyar nuna mallaka guda biyu a harshen Hausa, akwai doguwar mallaka da gajerar mallaka. A doguwar mallaka takan zo da dogon mahaxi wato '**na'** idan abin da aka mallaka namiji ne da kuma '**ta'** idan abin da

aka mallaka mace ce. (Galadanci 1976:28-30). An fi samun matsala a fagen rubutu a yayin da doguwar mallaka ta zo tare da wakilin suna. Misali

nawa	naka	namu
naku	nasu	nata

Idan aka samu irin wannan mallaka ana haxe harafin mallakar (na/ta) da wakilin sunan da suke tare, wato ba a rarrabe su a yayin rubutu.

Ita kuwa gajerar mallaka takan zo ne da sunan da aka mallaka da gajeran mahaxin (harafin) mallaka **(-n/-r).** Ana sanya mahaxin mallakar **–n** idan abin da aka mallaka namiji ne ko kuma jam'i. Sannan a sanya harafi **–r** idan abin da aka mallaka mace ce. Akan rubuta kalmar da aka mallaka da gajeren mahaxin mallakar a matsayin kalma guda (domin mahaxin mallaka na –n ko –r ba ya zama a matsayin kalma, duk kuwa da cewar rukuni ne mai zaman kansa a nahawu). Idan mallakar ta zo da suna ana rubuta su a rabe, misali

rigar Aliyu	littafin xalibi	zoben Hajara
jakar Amina	takalmin Zainab	jakan fatake

Idan kuwa mallakar ta zo da wakilin suna, akan haxe sunan da aka mallaka da gajeren harafin mallakar da wakilin sunan da ya yi mallakar a matsayin kalma xaya (domin mahaxin mallaka na –n ko –r ba za su iya haxuwa da wakilin suna (-**rka** ko –**nsa**) a matsayin kalma xaya ba). Misali,

rigarka	littafinsa	kayansu	xakinsu
Jakarta	takalminki	gidanmu	garinku

(Galadanci 1979: 28-29/Bunza 2002:106-109)

Akan samu kuskuren rabawa a tsakanin kalmar da aka mallaka da wakilin sunan da ya yi mallakar a cikin rubutun da ake yi a jaridu da mujallu na Hausa. Misali:

(13) *Gwamnatin qasar Sin, wato China, ta hukunta wasu jami'anta kimanin 17,500 a watanni takwas na wannan shekara bisa laifin almubazzaranci da* ***dukiyar su****.*
(Jaridar Gamzaki ta ranar 27 ga Oktoba zuwa 4 ga Nuwamba 2006:11)

(14) *...* ***Rubutun ta*** *ya ta'allaqa ne kacokam kan abubuwan da ta fahimta game da adabin Hausawa-* ***Rubutun su, finafinan su, waqoqin su, raye-rayen su****, da kuma irin gallazawar da gwamnatin Kano ta ke yi wa ma'abota waxannan fannonin (abin da ko kaxan Talatu ba a goyi bayan sa ba).*
(Mujallar Fim ta Janairu 2011, fitowa ta 133:12)

(15) *A ranar 1 ga Oktoba, 2010, qasar nan za ta cika shekara 50 da samun 'yancin kai. Godiya ga gwarzayen shugabanni da su ka taka rawa wajen gina* ***qasar mu****. 'Yan Nijeriya sun yarda, har yau, ba a cika wa qasar nan* ***alqawarin ta*** *ba, don haka Allah Ya yi dare, gari yawaye, zamani ya kawo mu na na wani zangon mulki da zai gina* ***qasar mu*** *Nijeriya.*
(Mujallar Fim ta Nuwamba 2010, fitowa ta 130:2)

A misalai na 13 zuwa na 15 da suka gabata kalmomin **rubutun ta** da **rubutun su** da **finafinan su da waqoqin su da raye-rayen su** da **qasar mu** an rubuta su a bisa kuskure domin kuwa an sava qa'idar haxe wakilin suna da sunan da suka yi mallaka da sunayen da aka mallaka. Ga yadda kalmomin ya kamata su kasance:

rubutunta	ba	rubutun ta	ba
rubutunsa	ba	rubutun su	ba
finafinansu	ba	finafinan su	ba
waqoqinsu	ba	waqoqin su	ba
raye-rayensu	ba	raye-rayen su	ba
qasarmu	ba	qasar mu	ba
alqawarinta	ba	alqawarin ta	ba

Haxuwar Wakilin Suna da Manunin Lokaci

Idan lamirin suna (manunin suna) ya gabaci manunin lokaci, wato wanda aka yi amfani da su a lokaci sababbe da lokaci mai ci (na 1 da na 2), haxa su ake yi da manunin lokaci. Misali:

Lokaci sababbe

yakan	sukan	mukan	takan
nakan	kikan	akan	kakan

Lokaci mai ci na 1

yana	tana	suna	kuna
muna	kina	ana	kana

Lokaci mai ci na 2

yake	take	kake	suke
muke	kuke	ake	kike

amma idan lamirin lokaci (manunin lokaci) ne ya fara zuwa, ana rubuta su a matsayin kalmomi daban-daban. Misali:

za ni	za ka	za ki
za mu	za su	za ta (Galadanci 1976:111)

Ga misalin irin kwamacalar da ake samu:

(16) *In kuma **mu ka** sauko nan baya-baya, mun ga yadda a zamanin yakin musulunci na karni na goma sha tara a nan kasar Hausa **a ka** rika yawace-yawace na neman ilimi.....*
(Mujallar Dakin Kara, Fitowa ta biyu, Maris 2009:1)

(17) *…. Wato a kyale duk wanda ke son takara ya yi takarar mukamin da **ya ke** so, kuma a tabbatar da an yi adalci wajen fito da wanda jama'a ke so…*
(Jaridar Gamzaki ta ranar 27 ga watan Octoba zuwa 4 ga watan Nuwamba, 2006:9)

(18) *Wani misalin kan irin hangen nesan Malam Aminu Kano shi ne, a zamanin da **ya ke** shugabancin jam'iyyar PRP, babu jam'iyyar da **ya ke** gwagwarmaya da ita tamkar jam'iyyar NPN mai mulkin Nijeriya a 1979 zuwa 1984. Kasancewar NPN **ta na** da alama ce mai masara, sai magoya bayan PRP **su ka** shiga goya buhun masara a bayan babura **su na** vula buhun **su na** yaryaxi da ita a kan tituna...*
(Jaridar Leadership Hausa ta ranar 26 ga Afirilu zuwa 2 ga Mayu, 2013:3)

Rubuta **ya ke** da **ta na** da **su ka** da **su na** (a misali na 16-18) kuskure ne domin a haxe ya kamata a rubuta su kamar haka; **yake** da **suka** da **tana**. Amma idan manunin lokaci ya zo kafin wakilin suna, wato kamar yadda yake a lokaci mai zuwa na 1, ba a haxe manunin lokaci na '**za'** da wakilin suna, misali:

za ta za su za ya za mu za a (ba za'a ba)

za ku za ni za ka za ki

Haxe manuni lokaci na mai zuwa na xaya (**za**) da wakilin suna ko aikatau kuskure ne a rubutun Hausa kamar yadda ake samu a a jaridu da mujallu, Misali,

(19) *Kuma abin da **zamu** lura dashi maza da mata mu sani in har wani ya riqa yabon xan'uwansa, to lokacin zai ji kullum yana qara shiga zuciya, sai ma wani ya riqa faxan ashe dai wance na so na, ko ta ce ashe dai angona na sona qwarai, Allah ya bamu ikon yin haka.*
(Jaridar At-tatbiq ta ranar Juma'a 13 - 27ga watan Mayu, 2011 fitowa ta 189:9)

(20) *Gwamnati da hadin guiwar wasu kungiyoyi su taru su karfafa makarantun Allo, inda **za'a** rika ciyr da daliban, da taimakon sutura, domin a hana su bara.*
(Mujallar Gani Da Ido, Maganin Tambaya ta watan Mayu, 2009:15)

A misalan da aka bayar na 19 da na 20 an haxe manunin mutum (wakilin suna) da manunin lokaci a matsayin xaixaikun kalmomi a maimakon kubuta su a rabe, wato **zamu** da **za'a**.

Haxuwar ‘ma’ Da Wakilin Suna

Akan samu haxuwar ‘**ma’** da gajeren wakilin suna mai gava xaya a yayin rubutu. Idan haka ta faru ana rubuta su ne a haxe, wato a matsayin kalma xaya. Don haka ga yadda ya dace a rubuta su;

Mani (mini)

maki (miki)

maku mana

masu mata

maku maka

A nan wakilin suna ne ya biyo bayan ‘**ma’** xin, kuma wakilin sunan zai iya zama na namiji ko na mace ko tilo ko kuma jam’i. Ga dokar qa’idar rubutu a haxe za a rubuta su ba a rabe ba. (Bunza 2002). Misali

a Ya hana **mana** yin rubutu.

b Sun aiko **mata** da saqo.

A misalai na 21 da na 22 sai aka yi kwamacala rabawa:

(21) *Yaqara da cewa,"farfajiyar Sarauniya Amina an bar shi ya fara zubewa har babu gyara, amma zuwan wannan gwamnati sai mai girma gwamna ya ce mu je rubuto **ma sa** duk abubuwan da suka kamata gangane yadda za qara inganta harkokin yawon buxe ido a jihar Kaduna……*
(Jaridar Leadership Hausa ta ranar Juma’a 9-15 ga watan Maris, 2012:7)

(22) *Dubban xaruruwan yara ake tilasta wa shiga yaqi, ko kora su zuwa gudun hijira ko canja **ma su** matsugunni, ko yi **ma su** fyaxe, ko a bautar da su, ko kuma nakiyoyi su nakasa su.*
(Mujallar Kulawa ta watan Janairu/Faburairu 2005:4)

A nan kalmar **ma** ta gabaci walikin suna, amma a maimakon rubuta su a haxe sai aka raba su wato kowace kalma ta yi zaman kanta, wato **ma sa** da **ma su** a maimakon **masa** da **masu**.

Tsawon kalma

Tsawon kalma ba ya sanyawa a raba ta a yayin rubutu. A koyaushe akan rubuta kalma kome tsawonta. Kalmomi irinsu

santamemiya

tavarvarewa

danqararriya

lallanqwasawa

Dukkan waxannan da ma wasunsu ana rubuta su ne a matsayin kalma xaya domin kuwa dama kalmomi ne xaixaiku. Don haka ba za a raba su ba a rubutu don ganin tsawonsu. A lura da waxannan misalai:

(23) *A lokacin da direban ya ce, lalle sai dai ta bar maganar tunkuxe ta, lokacin kuma ya yi mata barazanar zai sa sa kama ta, sai ta ce, kana iya yin kaha; shi kuma sai ya aikata. 'yankwanaki kaxan sai Parks ta* ***qalu-balanci*** *kamawar da aka yi mata.*
(Mujallar Magama ta Ofishin Jakadancin Amirka A Nijeriya ta watan Maris/Afrilu 2013:8)

(24) *...Amma duk da wannan kira da ya yi, basu yarda sun bari ba, sai ma suka riqa yi wa junansu wasiyyar cewa kada su rabu da allolinsu, kamar yadda yake* ***gaba ta*** *a Ayar.*
(At-tatbiq ta 189 ta ranar Juma'a 13 ga Mayu, 201 zuwa27 ga Mayu, 2011:5)

Kalmomin **qalu-balanci** da **gaba ta** kalmomi ne xaixaiku don haka tsawonsu ba ya sanyawa a raba su kamar yadda aka yi a misalan da suka gabata (na 23 da 24). Don haka **qalubalanci** da **gabata** ya kamata a rubuta.

Kalmomi masu gava xaya

Kalmomi masu gava xaya ana rubuta su a matsayin kalmomi masu cin gashin kansu, wato ba a haxe su da kalmomin da suke a gabansu ko bayansu, misali:

to qi ji yi

zo ci sha ga da sauransu Misali:

1. Ga shi ka ba su.
2. Ga mu mun zo.
3. Ya sha ya ji.
4. Af! To ba ka ji ba?

Su ma kalmomi masu gava xaya, musamman kalmomin aikatau irin su **ci** da **sha** da yi da sauran makamantansu, ana samun matsalar haxe su da sauran kalmomi a cikin rubuce-rubucen da ake yi a jaridu da mujallu. Ga misali:

(25) *Kuma abin da **zamu** lura **dashi** maza da mata mu sani in har wani ya riqa yabon xan'uwansa, to lokacin zai ji kullum yana qara shiga zuciya, sai ma wani ya riqa faxan ashe dai wance na so na, ko ta ce ashe dai angona na **sona** qwarai, Allah ya **bamu** ikon yin haka.*
(Jaridar At-tatbiq ta ranar Juma'a 13 – 27ga watan Mayu, 2011 fitowa ta 189:9)

(26) *Sun **bamu** wasu takardu (coupon) domin mu samu abinci. Ni da na je neman abincin na shiga layi, da layi ya kai guna, na dauki wani abinci wanda yake kuxin da ke jikin katin bai kai kuxin abincin ba sai kawai wani Ba'Amirke ya ba ni cikon dala xaya in cika in sayi wannan abincin,*
(Mujallar Magama ta Ofishin Jakadancin Amirka A Nijeriya ta watan Janairu 2004:3)

Kalmomin **ba** da **mu** da **shi** da **so** da **na**, dukkansu kalmomi ne masu gava xai-xai don haka kowace kalma za ta ci gashin kanta ne a wajen rubutu, amma ba a rubuta su a haxe kamar yadda ya bayyana a misali 25 da 26).

Wakilan Sunaye da Aikatau

Haxuwar wakilin suna da aikatau wata matsala ce mai rikitarwa a fagen rubutun Hausa. A dukkan wakilan sunaye babu wanda ake haxewa da kalmar aikatau xin da take a gabansa. Haxewa za ta iya haifar da gurvacewar ma'ana. (Bunza 2002:142-146). Misali'

a **Ta ga** abin da ake faxa mata

b **Ya yi** aikin da aka sanya shi.

c **Ta fi** shi qoqarin yin karatu

Ga misalan yadda ake sava wannan qa'ida:

(27) *MALAM AHMAD SALKIDA xan jarida ne wanda ya fara kawo rahoton qungiyar Ahlus-Sunnah Lilda'awati Wal-jihad, wacce **akafi** sani da Boko Haram wanda wasu ke zargin xan jarida ne mai alaqa da Boko Haram...*
(Leadership Hausa ta ranar Juma'a 26 ga Afirilu zuwa 2 ga Mayu 2013:11)

(28) *Janar Oshinowo **yaceyaji** dadin aiki da sojojin da **yayi** aiki dasu a jihar saboda hadin kan da suka bashi yayin da yake jagorancinsu.*
(Mujallar Kunnen Gari, (in ka ji, kowa ya ji) Fitowa ta 1 ta watan Maris, 2012:7)

Kamar yadda aka yi bayani, kalmomi masu gava xaya ana rubuta su ne daban ba tare da la'akari da rashin yawan gavovinsu ba. A misali na 27 an haxe kalmomin **aka** da **fi**. A misali na 28 kuwa kalmomi huxu ne ka haxe suka zama kalma xaya wato **ya** da **ce** da **ya** da **ji**, sannan kuma an haxe kalmar **ya** da **yi**.

Akan da a kan

Waxannan wasu kalmomi ne masu rikitarwa a cikin rubutun Hausa. **Akan** tana nunin lokaci sabo ne, wato abin da aka saba yi koyaushe. A yayin rubutu ana rubuta ta ne a matsayin kalma guda (domin wakilin suna na a da ya gabaci manunin lokaci na **kan**), misali

(i) **Akan** yi shuka idan ruwan damina ya sauka.

(ii) **Akan** sha shayi da safe.

Haka nan **a kan** tana danganta karvau da aikin da aka yi, wato wuri ko abin da ake magana a kansa shi ne karvau xin jimlar. Misali;

(i) Muna zance **a kan** harshen Hausa.

(ii) Na xebe zargi **a kan** sha'aninsa.

Ita kuwa **a kan** kalmomi ne guda biyu (zagi da sassauqan bayanau) da suka samar da sarqaqqen bayanau. Kalma ta farko ita ce kalmar ‘a’ (mai nuna dangantaka ta bigire/wuri), kalma ta biyu kuwa ita ce kan mai ma’anar bisa. Idan waxannan kalmomi suka haxu suna bayar da ma’anar a bisa. Misali:

(i) An xora littafi **a kan** (a bisa) kujera

(ii) Muna zaune **a kan** tabarma.

(Bunza 1990:66)

Marubuta a jaridu da mujallun Hausa ba kowanne ba ne yake iya bambancewa tsakanin **a kan** mai ma’anar a bisa da kuma **akan** wadda take xauke da lamirin suna da kuma lamirin lokaci wadda take nuni a kan sababben lokaci ko lokaci sabau ba. Sau da yawa sukan rubuta **akan** a maimakon **a kan**. Misali:

(29) *KU KARANTA JARIDAR GAMZAKI DOMIN SAMUN INGANTATTUN LABARAI DA SHARHE-SHARHE **AKAN** HARKOKIN SIYASA, TATTALIN ARZIKI DA ZAMANTAKEWAR JAMA’A A CIKIN NIJERIYA DA SAURAN KASASHEN DUNIYA*
(Jaridar Gamzaki ta ranar 27 ga watan Octoba zuwa 4 ga watan Nuwamba, 2006:5)

(30) *….. wannan a taqaice yana nuna wajibcin aiki da abin da Allah Ya saukar da yin haquri da juriya **akan** haka bisa duk abin da zai biyo baya sakamakon aikin da kau da kai daga dukkan soki-burutsu na maqiya Allah **akan** an bi Shari’a.*
(Mujallar Sautus Sunnah juzu’i na 2 fitowa ta 1, Mayu 2001:5)

Marubuta da dama sukan kasa bambancewa tsakanin **a kan** da **akan**. A dukkan misali na 29 da na 30 an rubuta **akan** wadda take nuni a kan lokaci sabau (sababben lokaci) a maimakon **a kan** wadda take da ma’anar ‘a bisa’.

4.2.2 Raba kalmomi

A nan ma akan samu kurakurai da dama ta dalilin haxa kalma a maimakon rabawa wanda hakan shi ma yakan haifar da sauyawar ma’ana ko salwantar ta.

Kamar yadda (Yakasai da Mu'azu 2010) suka bayyana, duk abin da ba shi da ma'ana ta kansa dole ne a haxa shi da wani vangare na kalma ko wata kalma ko qwaya kalma. Rashin kiyaye wannan doka ma yakan haifar da kwamacala iri daban-daban.

Wakilin Suna a Matsayin Aikau Ko Karvau

Wakilin suna yakan zo a cikin jimla domin ya wakilci suna. Idan kuwa haka ne zai iya zama aikau ko karvau a cikin jimla. A koyaushe aka samu wakilin suna ya zo a matsayin aikau ko karvau ana rubuta shi ne daban, ba a haxe shi da wata kalma. Misali:

Ya same **mu**.	Ya mare **shi**.
Ta sanar da **shi** labari.	Ta yaga **shi**.
Mun kira **su**.	Mun zane **su**.
Sun aike **ku**.	An buge ku.

Ga misalin wannan kwamacalar:

(31) *Mahaifinta Ya **Kulleta** a Banxaki Tsawon Shekara Goma*
*Wata ba-falasxinuwa, 'yar shekara 21, ta bayyana wa hukumomi cewa an **rufeta** a ban xaki har tsawon shekara 10, kuma babanta ne ya yi mata haka. Ba ya **barinta** ta fita daga cikin makewayin sai cikin dare, don ta share gidansu*
(Jaridar Aminiya ta ranar Juma'a 27 ga Janairu, 2012:22)

(32) *Shin ta ina ne shugabancin Madan Waziri ya fi na Malam Nuhu Ribaxu? Wane aiki ne ta yi ko kuma waxanne varayin gwamnati ne ta kama, kuma aka **hukuntasu** daidai da abin da doka ta ce? Nawa ta iya qwatowa daga waxannan varayi? Ba zanyi mamaki ba idan Madam Waziri na nufin, cewa shugabancinta ya fi na Nuhu Ribaxu ta wajen sukurkucewar lamari a hukumar EFCC ba, domin kuwa an riqa tafka ta'asa*
(Jaridar Gaskiya Ta Fi Kwabo ta ranar 11 ga watan Disamba, 2011:4)

A misali na 31 da na 32 an haxe kalmomin aikatau da wakilan sunayen da suka zo bayansu a matsayin kalma guda. Yin haka kuskure ne a rubutun Hausa.

Abin da ya kamata a yi shi ne a raba kalmomin aikatau da wakilan sunayen da suka zo a matsayin karvau xin jimlar; kamar haka, ‘kulle ta’ da ‘rufe ta’ da ‘barin ta’ da ‘hukunta su’.

‘ba’ Mai Korewa (da sauran kalmomin a’antawa)

Ana amfani da kalmar ‘ba’ domin kore tabbatuwar zance a harshen Hausa. Ana rubuta wannan ‘**ba’** xin ne daban, wato ba a haxe ta da kowace kalma, misali:

Ba haka **ba** ne.

Ba zai zo **ba**.

Ba shi **ba** ne.

Ba a surutu a nan. (ba **ba’a** surutu a nan ba)

(Ado da Rabeh 2008:24)

Akan rubuta ba’a (muzantawa) a maimakon ba a (hani). Wannan kuskure ne wanda yake sauya ma’anar abin da ake qoqarin rubutawa.

Misali:

(33) *Binciken da wakilinmu ya gudanar a cikin garin Kaduna ya nuna cewa har ranar Alhamis akwai wuraren da **ba’a** fara yin rajistar ba duk da cewa akwai jama’a suna jiran tsammanin hukumar ta INEC ta zo ta fara yi masu rajistar*
(Jaridar Gamzaki ta ranar 27 ga watan Octoba zuwa 4 ga watan Nuwamba, 2006:5)

(34) *Wannan ba shi ne aikin juriya da Rosa Parks ta **faraba** a cikin bas. Tun kafin wannan ma, ta yi wasu yunquri. Ta tsaya tsayin daka wajen samun ‘yanci, ta tsaya tsayin daka don daidaituwa wajen kaxa quria da gwagwarmaya wajen yin shari’ar gaskiya a qarqashin qungiyar nan mai suna – NAACP.*
(Mujallar Magama ta Ofishin Jakadancin Amirka A Nijeriya ta watan Maris/Afrilu 2013:9)

(35) *Aminiya: To ina budurwa take a yanzu?*
*Ai a lokacin **ba’a** rigaya an xaura mana auren baa bin ya faru. Sai dai na samu labarin yanzu haka tana aure a wani gida har da yaranta da kuma jikokinta.*
(Aminiya ta ranar Juma’a 22-28 ga watan Maris, 2013:3)

Haxe kalmar '**ba'** da kalmar da ta zo kafin ita ko bayanta shi ma kuskure ne. Wani lokaci irin wannan kuskure yana iya haifar da sauyawar ma'ana, musamman idan aka haxe ta da harafin '**a**'. Ma'anar sai ta koma **ba'a** (muzantawa). Don haka ya kamata a raba su wato 'ba a'. A misali na 34 ma '**fara ba'** ya kamata a rubuta ba '**faraba'** ba.

Haxuwar Korewa 'ba' da Wakilin Suna ko Aikatau

Idan aka samu wakilin suna ya biyo korewa ta 'ba', kowanne yana zaman kalma ce mai zaman kanta don kuwa kowanne yana da hukuncinsa na nahawu; ana rubuta kowanne daban da xan'uwansa, misali;

a **Ba** ya ji, **ba** ya gani.

b **Ba** ta da alqibla, shi ya sanya take da wahalar fahimta.

Idan kuwa korewa ta zo da aikatau shi ma hukuncin duk xaya ne; kowanne ana rubuta shi daban a matsayin kalma mai cin gashinta, misali

a **Ba** ji **ba** gani.

b **Ba** aiki **ba** samu.

Haka nan ana samun korewa ta zo da wakilin suna da aikatau a lokaci xaya. To a nan ma dai kowace kalma ce mai zaman kanta don haka daban ake rubuta su, ba a haxe su a yayin rubutu.

a Ba ta so.

b Ba mu yi.

(Bunza 2002:153-154)

A lura da wannan misali:

(36) *Har abada ba zan mance da wani tsohon banza ba da ya yi mutuwar wulaqanci a Ibadan ba aka kuma rasa wanda zai kawar da shi don muguwar varnar da yake yi kafin ya mutu. Don a lokacin da **baya** lafiya ga shi **baya** iya yi wa kansa komai, amma waxansu Gayu ke kawo masa giyar goggoro suna xura masa yana kwance a kusa da bola, don kowa ya qi yarda ya tsaya kusa da shagonsa ya yi jiyya. Da haka ya mutu saboda*

*haka kowa ya qyale gawar tasa dama kusa da wani juji yake kwance yana jiyya kuma abin baqin ciki Bahaushe ne **musulmi** ko kuma in ce musulmiya.*
(Jaridar Gaskiya Ta Fi Kwabo ta ranar 11 ga watan Disamba, 2011:13)

(37) *"Mun yi imanin cewa mudin **bamu** sanya mutanen da idan suka yi ruwa, suka yi tsaki a cikin harkokin jama'a ba, to da wuya mu cimma nasarar kusantar da harkokin lafiya ga yaran da ke bukatarsu…"*
(Mujallar Kulawa ta watan Janairu/Fabrairu 2005:12)

Ita ma irin wannan matsala ta so ta yi kama da wadda aka yi bayani a baya, wato a raba tsakanin ba da wakilin suna da ya zo bayanta. Haxe wakilin suna da harafin **ba** yana iya sauya ma'ana, kamar yadda ya bayar a kalmar **baya** da **bamu** a misali na 36 da na 37 a maimakon **ba ya** da **ba mu.**

Zagage (jakadu)

Zagage, kalmomi ne waxanda ake amfani da su kafin suna ko wakilin suna domin nuna wuri ko lokaci ko kuma yanayi (hanyar aiwatar da wani abu). Kalmomin zagage sun haxa da '**da'** da '**a**' da kuma 'wa'

Zagin 'a'

Idan zagin '**a**' ya zo tare da bayanau (mai nuna wuri ko lokaci ko yanayi) ana rubuta kowanne daban. Misali,

a **Wuri**

a An ajiye littafi **a bisa** kujera.

b Ana magana **a kan** abin da ya shafi Hausa

c Sun zauna **a gefen** gado

b **Lokaci**

a **A shekaranjiya** ne aka fara karatu a makarantar.

b **A xazu** maniyyata aikin haji suka fara tashi zuwa qasa mai tsarki.

c **A gobe** ake sa ran zuwan shugaban.

c Yanayi

a Ya wuce **a guje**.

b Xalibai sukan zauna a aji **a natse**.

c **A hankali** ake shiga jama'a.

Zagi 'a' a Yayin Haxuwa da Aikatau

Zagin '**a**' yakan haxu da aikatau masu siga iri biyu; na farko yakan haxu da aikatau mai gava xaya, sannan yakan haxu da aikatau mai fiye da gava xaya. A duk lokacin da zagin 'a' ya zo da aikatau mai gava xaya (ko fiye) kowanne yana cin gashin kansa ne wato ana rubuta su ne a rabe (Bunza 2002:150/Wurma 2005:85-86). Misali;

a **A yi** aiki ya fi zaman banza

b **A sa** baka ya fi a **rataya**.

Ga misalain yadda ake sava wannan:

(38) *... kodayake a lokacin shi bai san inda za su ba, saida ya ji ana cewa ga wani kwali can ba **asan** abin da ke ciki ba. "Da muka je wajen sai muka buxe kwalin inda muka ga jaririya ce a mace….*
(Jaridar Aminiya ta ranar Juma'a 28 ga Janairu, 201:7)

(39) *… Hasali ma domin ya cimma burin **kaiwa** ga madafan iko a Nijeriya Ojukwu ya kafa jam'iyyar siyasa, amma ta gaza taka rawar **azo** a gani, hatta a yankin Ibo.*
(Mujallar Kunnen Gari, (in ka ji, kowa ya ji) Fitowa ta 1 ta watan Maris, 2012:10)

A misalai na 38 da 39 da aka gabatar akwai matsalar haxe zagagen '**a**' da '**wa'**. A misali na farko an haxe 'a' da aikatau 'san'. A misali na biyu kuwa an haxe kalmar aikatau 'kai' da kalmar '**wa'**.

Zagin 'da'

Zagin **'da'** yakan haifar da rauni ga marubuta a cikin rubutu. Wannan zagi yakan kasance a muhalli guda hudu; yakan haxu da suna ko wakilin suna, yakan

kuma haxu da manunin lokaci sannan ya zo tare da aikatau. Amma a jaridar **Rariya** da mujallar **Kulawa** ga yadda aka rubuta su:

(40) *Da alamu dai wasu iyayen yara a yankin sun daina barin 'ya'yansu su tafi makaranta sakamakon tsoron* ***abinda*** *ya faru. Kuma hanya xaya da yaran za su iya amfani da ita zuwa makaranta ba tare da an qetare rafin ba, sai an kwashe sa'o'i huxu ana tafiya a qasa saboda nisan ta.*
(Jaridar Rariya ta ranar 9-22 ga watan Maris, 2012:5)

(41) *Fiye da yaro xaya a cikin yara uku ba su da wurin kwana, fiye da kasha 16 daga cikin 100 na yaran da shekarunsu ba su wuce biyar ba, sun rasa abinci mai gina jiki,* ***yayinda*** *kasha 13 daga cikin 100 na dukan yara ba su san inda hanyar zuwa makaranta take ba…*
(Mujallar Kulawa ta watan Janairu/Faburairu 2005:4)

(42) *…A cikin 2003 kaxai, mutane miliyan 2 da dubu 900 ciwon qanjamau ya hallaka,* ***yayinda*** *mutane miliyan 4 da dubu 800 ke xauke da qwayoyin cutar….*
(Mujallar Kulawa ta watan Janairu/Faburairu 2005:4)

A wannan misalin (na 40) kuwa haxe kalmar '**abin'** da zagin '**da'** shi ne ya haifar da kuskuren da aka samu.. A misali na 41 da 42 kuwa an haxe kalmar **yayin** da zagin **da**. Ba a rubuta **abinda** da **yayinda** a matsayin kalma xaya, sai dai a raba, wato abin da da kuma yayin da.

a Haduwarsa da Suna ko Wakilin Suna

Idan zagin 'da' ya zo da suna ko wakilin suna, yakan yi aikin mahaxi ne a cikin jimla. Ya fi rikitarwa idan ya zo da wakilin suna ganin cewar akasarin wakilan sunaye masu gava xaya ne. Idan aka sami wannan zagi ya zo da suna ko wakilin suna ana rubuta su ne daban-daban ba a haxe ba, wato kowanne yana a matsayin kalma ta daban ne. Misali,

Tafi tare **da** shi.

Da ita **da** kai duk xaya ne.

Da ni **da** su duk xalibai ne.

Haka nan ana gina jimlar sharaxi a shuxaxxen lokaci da wannan zagi, misali.

Da haka ka yi, **da** ya fi.

Da ta gan shi, **da** ba haka ba.

b Haduwarsa da Lamirin Lokaci

Idan wannan zagi ya haxu da lamirin lokaci, za a rubuta kowannensu a ware ya ci gashin kansa shi kaxai ba tare da wani ba (Bunza 2002:154).

Misali:

Yaran **da ke** aikata haka sun daina.

Mutanen **da ke** kawo kayan sun iso.

Jama'ar **da ke** jiransa suna da yawa

c Haxuwarsa da Aikatau

Idan zagin 'da' ya zo da aikatau, hukuncin dai iri xaya ne kamar yadda aka yi bayani a baya, ma'ana ba a haxe 'da' xin da kalmar aikatau xin da suka zo. Misali

Da so **da** qi ba su haxuwa.

Da ji **da** gani suna cikin rahamomin rayuwa. (Bunza 2002:156).

Lura da waxannan misalan:

(43) *A nan ma malamin mu marigayi Sheikh Ja'afar Mahmud Adam (Allah ya jiqansa) ya ce: Ma'ana saboda kura-kuran da suka yin a shirka (da kangare wa Annabi Nuhu), sai aka dulmiyar **dasu** a cikin ruwa, sannan aka shigar **dasu** cikin wuta. Wato da aka halakar **dasu** da ruwa, suka mutu, sai kuma aka shigar **dasu** cikin wuta nan take a qarqashin ruwan….*
(Jaridar At-tatbiq ta ranar Juma'a 13 - 27ga watan Mayu, 2011 fitowa ta 189:7)

(44) *… idan ba haka ba ai kowa ya riga ya sani cewa masu tuni aka rurrusa mana masallatai, don haka ba mu da masallaci ma balle har afake da hana zuwa har a hana sauran jama'a , kuma jama'a kar su manta da cwa waxanda su ka kawo wannan tsari*

*na kafirci **dake** gudana a yanzu sai da fa su ka karkashe mutane masu yawa kuma su ka jefa jama'a cikin matsanancin hali fiye da wanda ake ciki a yanzu…..*
(Jaridar Leadership Hausa ta ranar Juma'a 9-13 ga watan Maris, 2012.:5)

(45) *Kuma da dama daga cikin shafukan sun yi ta yayatawa da neman goyon bayan miliyoyin jama'a **dake** amfani da intanet das u fito su nuna adawarsu ga wannan dokar….akwai shafukan yanar gizo **dake** taimakawa wajen karya dokar haqqin mallaka da kuma safarar jabun manhajar kwamfuta.*
(Muryar Arewa, fitowa ta 8, Maris 2012:13)

A misali na 43 haxe zagin '**da'** da wakilin suna '**su'** shi ne ya haifar da kwamacalar da aka yi. Misali na 44 da na 45 haxe zagin '**da'** da manunin lokaci '**ke'** shi ne ya haifar da kuskuren. Kalmomin ya kamata su kasance '**da su'** da kuma **'da ke'**, amma ba a haxe su ba kamar yadda aka gabatar a misalan.

Zagin'wa' da xafa qeyar 'wa'

A qa'idar rubutun Hausa ba a haxe kalmar 'wa' a matsayin jakada da kowace kalma da take a bayanta. Ita dai 'wa' (jekada) kalma ce da take nuna cewa aikin da ake magana a cikin jimla ya tabbata ko ya kasance a kan karvau (wato wanda aikin ya faxa a kansa). Ana gane ko rarrabe jakada **wa da –wa (**ta xafi) da cewa shi kullum xauke yake da Karin sautin qasa (\ ) ne, kuma ba ya iya xaukar xafi ko a rava masa wata qwayar ma'ana (yakasai da Mu'azu (2010). **Ga** misalan yadda take kasancewa:

(a) Usman ya tsone **wà** Ali idanu.

(b) Na saya **wà** Kabir keke.

(c) Tanko ya sayar **wà** Garba da gidansa.

(d) An daka **wà** xalibai tsawa.

To amma idan '**wa'** ta zo a matsayin xafa-qeya ko gavar kalma, musamman ga kalmomin aikatau, ana haxe ta ne da kalmar da ta zo da ita. A nan kalmar tana tashi ne daga matsayinta na aikatau ta koma suna xan aikatau. Misali:

(a) Ladi tana **rubutawa** da kyau.

(b) Yana **sayarwa** idan ana buqata.

(c) Lawal yana **karyawa** da safe.

(d) Kome ka gani a kasuwa na **sayarwa** ne.

(Sa'id 2004:13-14 da Wurma 2005:89-90).

Ga irin wannan misali:

(46) *.....gwamnan jihar ta Katsina ya taka rawar gani wajen **samawa** matasar jihar ayyukan da za su dogara da kansu, a cewarsa gwamnan ya buxe cibiyar **koyawa** matasa sana'o'in hannu wanda yin hakan zai taimaka wajen rage zaman kashe wando ga matasan jihar bakidaya.*
(Jaridar Leadership Hausa ta ranar Juma'a 9-15 ga Maris 2012:9)

(47) *Sannan ya **yabawa** gwamnatin jihar dangane da irin taimakon da take **baiwa** rundunar. A karshe ya nemi jami'an tsaro na JTF da su **baiwa** sabon kwamandan hadin kai kamar yadda suka bashi yayin dake aiki dasu.*
(Mujallar Kunnen Gari, (in ka ji, kowa ya ji) Fitowa ta 1 ta watan Maris, 2012:7)

A cikin waxannan misalai (na 46 da 47) an yi amfani da **wa** a matsayin xafa-qeya a maimakon jakada shi ya sa kalmomin **samawa** da **koyawa** da **yabawa** da **baiwa** suka sauya matsayinsu a nahawu wato na aikatau da jakada suka koma suna xan aikatau. A nan an xauki zagin '**wa'** a matsayin vangaren kalmomin a maimakon ya ci gashin kansa. Don haka a rabe ya kamata a rubuta su wato haka, **sama wa** da **koya wa** da **yaba wa** da **bai wa.**

Dirka

Ita kuwa dirka wasu kalmomi ne ‘yan qanana waxanda suke taimaka wa jimloli su dire sosai da sosai. Wannan nau’i na rukunin nahawu na qara kwalliya da cikar zance ko jimla (Yakasai da Mu’azu 2010) Kalmomi ne masu dangane da jinsi da kuma adadi. Kalmomin dirka kalmomi ne masu daidaitawa. Akwai kalmomin dirka guda biyu a Harshen Hausa (Wurma 2005:63). Su ne:

ne: ga suna ko wakilin suna da yake namiji ne ko jam’i. misali,

i Aliyu **ne** xalibin da ya zo

ii Itatuwa **ne** aka shuka

iii Sani **ne** ake nema tun jiya

iv Binta da Zainab **ne** suka ci jarabawar.

ce: ga suna ko wakilin suna da yake mace. misali,

i Hussaina **ce** xalibar da ta zo

ii Ita **ce** shugabar taron

A qa’idar rubutun Hausa ba a liqa wa kalmomin dirka kowace irin kalma, a gabanta ko a bayanta, duk inda suke suna fitowa ne su kaxai. Amma an sava wannan a waxannan misalan:

(48) *Shekaru 12 daga nan baya kuma wani ya tava cin zarafin Malama Parks, saboda ta shiga cikin motarsa Bas ta gaban motar, alhali kuwa qofar motar ta baya ta **cunkushene**.*
Ya cukumo rigarta ya tunkuxo ta waje. Wannan ya sat a haukace masa, har ma ta daina hawa motarsa na wani lokaci.
(Mujallar Magama ta Ofishin Jakadancin Amirka A Nijeriya ta watan Maris/Afrilu 2013:8)

(49) *Ya kuma yaba da matakin da gwamnatin tarayya ta xauka na shirin yin afuwa ga ‘ya’yan qungiyar Boko Haram, inda yace **matakine** wanda ya dace wanda kuma zai taimaka domin dawowar zaman lafiya a faxin qasar bakixaya.*
(Jaridar Leadership Hausa ta ranar Juma’a 26 ga Afirilu zuwa 2 ga Mayu, 2013:8)

Haxe kalmomin dirka da suna ko wakilin suna kuskure ne saboda kowanne rukuni ne mai zaman kansa. Haka na faruwa ne saboda kalmomin dirka kalmomi ne masu gava xaya, don haka sai a riqa xaukar su a matsayin vangaren kalmar da ta zo tare da su. A misali na 48 da ya gabata an haxe kalmar **cunkushe** da **ne** da kuma **mataki** da **ne** a misali na 49 a matsayin kalma xaya, a maimakon a rubuta kowace kalma daban.

Haxuwar Wakilin suna tambayau da Dirka

Wakilin suna tambayau su ne nau'o'in wakilan sunayen da ake amfani da su a yayin yin tambaya. Wakilin suna tambayau iri biyu ne akwai na gaba xaya (wanda ya haxa da mutane da abubuwa) da kuma fayyatacce (wanda yake rarrabe mace da namiji) Su dai waxannan wakilan sunaye sukan zo ne a matsayin kalma xaya mai cin gashin kanta. Misalin wakilin suna tambayau su ne,

Na gaba xaya	Mutum	wa	su wa		
	Abubuwa	me	su me (da me)		
Fayyatacce	(namiji)	wanne			
				(jam'i)	waxanne
	(mace)	wacce			

(Sani 1999:65)

Idan aka samu haxuwar wakilin suna da kalmar dirka a yayin rubutu, kowanne zai ci gashin kansa ne, ma'ana za a rubuta kowanne a matsayin kalma xaya. Misali,

Wane ne shugaban makarantar?

Wace ce ta ce a yi haka?

Waxanne ne suka dace da aikin?

Haka nan idan dirka ta zo da wakilin suna rakavau, nan ma kowanne za a rubuta shi a matsayin kalma daban mai cin gashin kanta. Shi dai wakilin suna rakavau shi ne wakilin sunan da za ya iya zama shi kaxai ya kuma ci gashin kansa, wato ba tare da ya haxu da wasu kalmomi na nahawu ba. Misali ni, kai, shi, ita, su, mu, ku, (Sani 1999:65).

Shi ne wanda aka sha jin labarinsa.

Ita ce ta bayar da babbar kyauta.

Su ne suka tafi gasar karatu.

Mu ne aka tura mu wakilci sauran.

Akan samu akasin haka a cikin rubuce-rubuce, wato dai akan sava wannan qaidar inda akan rubuta kalmomin wakilin suna tambayau ko rakavau haxe da kalmomin dirka a matsayin kalma guda, kamar a wannan misalin:

(50) *.....sai na ji yace **shine** wane kuma malami ne ga waxannan tsofaffin xalibai, kuma a yanzu haka shi kwamishina ne na mutu-ka-raba a wata hukuma ta jihar su.*
(Mujallar Dakin Kara, Fitowa ta biyu, Maris 2009:23)

(51) *.....Haka kuma akwai masu ganin kamar suna soyayya ne da fitacciyar jaruma Samira Ahmad. Shin **wanene** Shaba? **Menene** asalin sa? Jarumin, mawaqin kuma furodusa ya faxe mana biri har wutsiya.*
(Mujallar Fim ta Janairu 2011, fitowa ta 133)

Kamar yadda aka yi bayani a kan kalmomin dirka cewa ba a haxa su da kowace kalma (ko da kuwa wakilin suna ne). A misalan da suka gabata na 50 da 51 an haxe kalmomin dirka da wakilan sunaye. A misali na 50 an haxa wakilin suna **shi** da dirka **ne**. A misali na 51 kuwa an haxe **wanne** da **mene** da dirka **ne** wanda yin haka ya sava qa'idar rubutun Hausa, wato dai an yi kwamacala:

Wakilin Suna da aikatau mai gava xaya

Wakilin suna, musamman zagin aikatau yakan haddasa ruxani idan ya zo gabanin aikatau mai gava xaya. Wakilin suna (zagin aikatau) shi ne irin wakilin sunan da yakan zo kafin aikatau; wato da ya zo sai aikatau ya biyo bayansa. Shi kuwa aikatau mai gava xaya shi ne nau'in aikatau da yake xauke da gava xaya irinsu ci da sha da yi da sauransu.

A koyaushe aka samu haxuwar wakilin suna zagin aikatau da aikatau (ko wane iri ne) ba a haxe su a cikin rubutu; ana rubuta kowannensu daban , misali,

a Ya zo, ya ci, ya sha, sai hamdala.

b Sun ji, sun bi, sun amfana.

A jaridu da mujallu kuwa akan kasa rarrabewa a tsakanin irin waxannan aikatau masu gava xaya, sai a riqa haxe su da sauran kalmomi, musamman takwarorinsu masu gava xaya, ga misali:

(52) *Wannan al'amari ya xaure man kai kwarai da gaske,* ***ace*** *mutum da ke matsayin kakana har yanzu (da ni kaina na yi shekaru ina aiki) yana aikin gwamnati.*
(Mujallar Dakin Kara, Fitowa ta biyu, Maris 2009:23)

(53) *… Kwanci tashi sai wasu 'yan sandan suka zama tamkar kunamar da idan ba su harbe ka ba, sun harbi wani naka. Suke jingine aikin kare rayuka da dukiya suka koma kare bukatun ma'abota hannu da shuni da kuma masu fada* ***aji****.*
(Leadership Hausa ta ranar Juma'a 2-8 ga Maris 2012: 4)

A misali na 52 da na 53 an haxe kalmomin aikatau na **ce** da **ji** da harafin **a** wadda yake a matsayin wakilin suna. Yin haka kuskure ne domin ana rubuta kowanne a matsayin kalma mai cin gashin kanta.

'ma' ta Qarfafawa

Qarfafawa dai shi ne nuna tabbatuwar faruwar wani abu ga mai magana ko wanda ake magana a kansa (Bunza 2002:162). Kalmar 'ma' tana daga cikin

kalmomin da ake amfani da su don qarfafawa a nahawun Hausa. Idan aka yi amfani da wannan kalma a cikin rubutu, daban ake rubuta ta; wato ita ma tana cin gashin kanta ne a matsayin kalma mai ‘yanci. Misali:

Kai **ma** ka zo.

Su **ma** sun yarda.

Shi **ma** haka yake.

(54) ***Shima*** *shugaban karamar hukumar Jos ta arewa Barrister Timothy Buba wanda a lokacin zabensane a shekara ta 2008, aka fara rikici a zamanin gwamna Jonah David Jang, yayi tsokaci akan zaman lafiya.*
(Mujallar Kunnen Gari, (in ka ji, kowa ya ji) Fitowa ta 1 ta watan Maris, 2012:6)

(55) *“Mu ne, muk kafa jam’iyyar, amma ta kaucewa layin da muka kafa ta a kai, har ta kutsa ta faxa ciki qasurgumin daji, sai dai a lura b azan bita a cikin dajin ba,* ***hasalima*** *a yanzu bani da sha’awa da ita.”*
(Leadership Hausa ta ranar Juma’a 26 ga Afirilu zuwa 2 ga Mayu 2013: 16)

A misali na 54 da na 55 kuskuren da ya faru shi ne an haxe kalmar **shi** da **hasali** da kalmar qarfafawa ta **ma**. Haka nan duk inda **ma** ta zo ba a haxe ta da wata kalma

Aikatau xan aji biyar

Aikatau kalma ce da ke nuna aiki a cikin jimla. To akwai wani nau’insa da ake kira aikatau musabbabi ko fi’ili haddasau. Misalin irin wannan aikatau su ne:

Shayar da Bayar da Sayar da Tabbatar da

Rikitar da Bugar da Tsallakar da

Daga waxannan misalai da ke sama za a iya fahimtar cewa ba a haxe harafin qarshe na ‘**r**’ da take a qarshen kalmar aikatau da kalmar da ke biye da ita su zama kalma xaya kamar haka:

Ba a rubuta

Shayarda bayarda sayarda Saukarda

Rikitarda bugarda tsallakarda Tabbatarda

Haka nan kuma ba a nashe harafin r xin da kalmar da, take a gaban aikatau xin ko su saje, su zama kalma xaya kamar yadda ake yi a wajen furucinsu, misali:

Ba a rubuta

shayadda bayadda sayadda tabbatadda

rikitadda bugadda shigadda tsallakadda

Haka kuma ba a nashe harafin –r da harafin ‘da’ da yake a farkon kalmar da ke gabanta rubuta su kamar haka:

shayad da bayad da sayad da tabbatad da

rikitad da bugad da shigad da tsallakad da

(Wurma 2005:50).

Ana samun sava wannan qa’ida, musamman ta haxe irin wannan aikatu da kalmar da wadda take biye da shi. Misali:

(56) *Ya ku ‘yan uwa! ta yaya za ku ji dadi a duniya alhali Mala’ika mai kaho ya dora kaho a bakinsa, yana sauraron izinin Allah, yaushe za a umurce shi da busawa, sai ya busa. To a wannan lokacin tsoron busar zai* ***firgitadda*** *duk halittun sammai da kasa. Sai fa wanda Allah ya so ya tsare kawai.*
(Jaridar Gamzaki ta ranar 27 ga Oktoba zuwa 4 ga Nuwamba 2006:10)

Wani lokaci akan gutsura irin wannan nau’o’in aikatau a yayin magana (ko a rubuce), wato a mayar da su masu gava xaya. Misali:

mayar mai

bayar ba

kawar kau

tsayar tsai da sauran makamantansu.

Hukuncinsu daidai yake da aikatau xin da ba a gutsure ba; ma’ana dai ba a haxe shi da kalmar da ke a gabansa ko a bayansa. An fi samun matsala da irin

waxannan aikatau idan jekada ‘da’ ta biyo bayansu. Ko da hakan ta faru hukuncinsu dai yana nan bai canza ba. Misali

Mai da bayani

Ba da labari

Kau da matsala

Fid da tsammani

Tsai da magana.

Haka nan ma hukuncin yake idan sauran kalmomi sun biyo bayan irin waxannan aikatau.

Misali

A **bar wa** Allah dukkan al’amura.

A **xau** haquri da abin da ya faru.

(Bunza 2002:160-162)

Ga wasu misalai na wuraren da ake sava wannan qa’idar:

(57) *BATUN zaven **fidda** gwani wanda jam’iyyar PDP ta tsara za a gudanar a ranar Asabar, 17 ga watan Disamba 2011 inda za a zavi wanda ya fi cancanta ya yi wa jam’iyyar takarar zaven gwamna a jahar Sakkwato, da hukumar zave mai zaman kanta (INEC) ta tsara za ta gudanar…*
(Gaskiya ta fi kwabo ta ranar Litinin 5 zuwa Laraba 7 ga Disamba, 2011:7)

(58) *… don haka ne ya yi kira da cewar yanzu abinda ya fi amfani a gare mu shine mu tashi tsaye tsayin daka don ganin mun **kauda** ko kuma aqalla mun rage yawan yaxuwar wannan cuta a cikin al’umma.*
(Mujallar Xakin Kara, fitowa ta 3, Mayu 2009:14)

Kamar yadda ya gabata ba a haxe gutsurarren aikau da kalmar da ta biyo bayansa. An fi samun wannan matsalar idan kalmar ‘**da’** ce ta biyo bayan irin wannan gutsurrren aikatau kamar yadda ya bayyana a misali na 57 da 58 inda aka yi kuskuren rubuta **fidda** da **kauda** a maimakon **fid da** da **kau da**.

Rashin Amfani da Haruffa Masu Qugiya

A harshen Hausa akwai haruffa masu qugiya guda uku; **v, x** da **q**. amfani da waxannan haruffa yana taimakawa qwarai a wajen bambance wasu kalmomi masu wahalar tantancewa idan ba a yi amfani da su ba. Haka nan rashin yin amfani da haruffa masu qugiya yakan haifar da sauyawar ma'ana (Sa'id 2004:4).

zaki da zaqi

baki da baqi

kari da qari

(59) *Rinin kamfala sana'a ce da za a iya faraway da jari **karami**, watau kimanin Naira dubu 30 zuwa Naira dubu 50. A na iya fara matsakai ciyar harkar da kamar Naira dubu 200, inda za a **dauki** mutum biyu zuwa uku aiki, **wadanda** za su kasance **kwararri**.*
(Aminiya ta ranar Juma'a 19 ga Nuwamba, 2010:11)

A misali na 59 rashin amfani da haruffa masu qugiya a kalmomin **karami** da **dauki** da **wadanda** da kuma **kwararri** ya mayar da kalmomin kamar ban a Hausa ba. Kamata ya yi kalmomin su kasance; **qarami** da **xauki** da **waxanda** da kuma **qwararri.**

Rashin Amfani da Manyan Haruffa a Wajen da ya Dace

Qa'idar rubutun Hausa ta keve wurare na musamman inda ya dace a yi amfani da manyan haruffa. Irin waxannan wurare sun haxa da farkon sunayen mutane da na garuruwa da sunayen ubangiji da sunayen mala'iku da sunayen tsibirai da unguwanni da nahiyoyi da ranaku da watanni da sunayen harsuna da shiyoyyi da qabila da kuma sunaye muqamai. Haka nan ana amfani da manyan haruffa bayan yin amfani da ayar tambaya da aya da alamar zancen wani (tsakure) da alamar motsin rai da kuma a farkon jimla (Wurma 2005:71-72)

Amfani da manyan haruffa yana da matuqar muhimmanci. Da yawa akan yi amfani da manyan haruffa a wuraren da ba su dace ba, wani lokaci ma akan

gwamutsa manya da qananan haruffa a wuri guda. Wani lokaci kuwa rashin bambancewa tsakanin manyan haruffa da qanana shi ne yake haddasa haka.

Muhallan amfani da manyan haruffa sun haxa da:

(i) **Farkon sunayen yanka**: wato sunayen mutane da garuruwa da unguwanni da qasashe da tsibirai da tafukka da kamfunna da littattafai sauransu. A irin waxannan sunaye dole ne harafin farkonsu ya kasance babban harafi, misali

(ii) **Farkon jimla ko zance**: Duk jimlar da za a fara rubutawa dole ne harafin farkon jimlar ya kasance babban harafi ne (Sa'id 2004:15), misali:

a. Hanyar Allah ta fi ta cali yawa.

b. Tukkura da Baqo duk Umbutawa ne.

c. Sarki ya naxa galadima bara.

(iii) Dukkan harafin da ya biyo bayan **alamar aya** da **alamar tambaya** da **alamar ruwa-biyu** da **alamar zancen wani (tsakure)** da **alamar motsin rai** dole ne ya kasance babban harafi, domin kuwa sabuwar jimla ce takan zo bayan waxannan alamomi. Lura da waxannan misalai:

a. Hukumar 'yan-sanda ta yi gargaxi ga masu son tayar da hankalin jama'a. Duk wanda aka samu da hannu wajen haddasa fitina zai xanxana kuxarsa.

b. Ga yadda tsarin yake: Da farko akan fara gyaran gona, daga nan sai shuka, bayan nan sai noman furi da na maimai.

. Da sarki ya nisa, sai ya ce, "Na gamsu da wannan jawabi naka."

d. Assha! Yin haka bai dace ba.

A misali na 59 zuwa na 62 kuwa an sava wannan qa'idar:

(60) *Mahaifinta wanda asalinsa xan Isra'ila ne, ya shiga hannu, an kuma miqa shi ga hukumomin Isra'ila. An gurfanar da shi a kotu tun ranar Laraba, kamar yadda **Mai Magana** da yawun 'yan sandan Isra'ila ya bayyana.*
(Jaridar Aminiya ta ranar Juma'a 27 ga Janairu, 2012)

(61) *Rabi Baturiya, **rabi** Bahaushiya, TALATU DANNY ta yi bankwana da masoya tare da bayyana dalilan tan a son Hausawa da kuma zama 'yar wasa.*
(Mujallar Fim, fitowa ta 133 Janairu 2011:7)

(62) *....Masu iya **Magana** sun ce alheri danko ne ba ya faduwa kasa banza. ko tantama babu duk mutumin da yake jihar **katsina** ya san cewa Alhaji Ibrahim Shehu Shema ya gaji dimbin ayyuka na alheri da shugaban kasa Alhaji Ummaru Musa ya dasa wato dashen da ya yi gashi nan maigirma gwamna **shema** yana bashi **Ruwa** kuma dashen ya mike har yan fara yadokai ya yi 'ya'ya ma……*
(Mujallar Gani Da Ido, Maganin Tambaya ta watan Mayu, 2009:4)

(63) *Taimakon da Hukumar Raya **qasashe** ta Amirka (USAID) da **sashen** Raya **qasashe** na Ingila (DFID) suka ba Nijeriya ya sanya Nijeriya a yanzu tana da.....*
(Mujallar Magama ta Ofishin Jekadancin Amirka a Nijeriya (Sifili na 17, lamba ta 2. Yuli 2011:4)

A misali na 60 kalmomin **Mai Magana** da aka fara rubuta su ba babban harafi kuskure ne domin ba su cikin muhallan da ake farawa da babban harafi. Misali na 61 kuwa sunan **rabi**, sunan yanka ne don haka ya kamata a fara rubuta shi da babban harafi. A misali na (62) an fara rubuta **shema** da qaramin baqi domin kuwa sunan yanka ne, amma sai aka rubuta suna gama-gari (**ruwa**) da babban harafi. A misali na qarshe (63) an fara rubuta sunan hukuma da qaramin baqi. Ga yadda sunayen hukumomin ya kamata ya kasance: **Hukumar Raya Qasashe ta Amirka** (USAID) da **Sashen Raya Qasashe na Ingila** (DFID).

4.2.3 Rubuta kalmomi

Ire-iren waxannan kurakuran su ne waxanda ake samu a yayin rubuta kalmomi a xaixaikunsu, ma'ana haruffan da ya kamata a yayin rubuta kalmomi (spelling rules). Da dama akan rubuta kalmomi a bisa kuskure. Wuraren da aka fi samun irin wannan matsala sun haxa da,

Xaurin wasalin ‘ai’ da harafin ‘y’

Harafin **y** ba ya zuwa bayan xaurin wasalin **ai** a cikin rubutun Hausa, a maimakon haka sai a mayar da wasalin ‘**i**' na xaurin zuwa harafin ‘**y**’, kenan, sai a samu ‘**y**’ guda biyu, misali:

Bayyana	ba	baiyana	ba
Ayyana	ba	aiyana	ba
Gayya	ba	gaiya	ba
Tarayya	ba	taraiya	ba

Shi ma harafin ‘**w**’ ba ya zuwa bayan xaurin wasalin ‘**au’** a cikin rubutun Hausa, a maimakon haka sai a mayar da wasalin ‘u' na xaurin zuwa harafin ‘w’, kenan sai a samu harfin ‘**w**’ guda biyu, misali:

Tawwada	ba	tauwada	ba
Tsawwala	ba	tsauwala	ba
Yawwa	ba	yauwa	ba

(Bunza 2002:104)

(64) *Shugaban kungiyar na Nijeriya Alh. Shuaibu Abubakar ne ya **baiyana** hakan a garin Jos , a wajen kaddamar da kalandarsu ta shekara ta 2012, reshen karamar hukumar Jos ta arewa. (Mujallar Kunnen Gari, (in ka ji, kowa ya ji) Fitowa ta 1 ta watan Maris, 2012:7)*

*(65) Dole Katsinawa su ce Allah ya ji qan Ummaru Musa ‘Yar’adua! Duk ximbin **aiyukan** ci gaban da ya yi wa jihar Katsina a hawan san a farko, (wanda har ta sa Katsinawa ke ganin ba’ayi ba, ba za kuma a yi ba) wannan bai hana shi sake nunnunka **aiyukan** alkhairi ga al’ummar Katsina ba a hawan sa a biyu qarewa ma, **aiyukan** da umaru ya yi a hawansa a biyu sun rubanya irin **aiyukan** da ya yi a hawan san a farko… (Leadership Hausa ta ranar Juma’a 26 ga Afirilu zuwa 2 ga Mayu 2013: 35)*

A nan kurakuran da aka samu a dukkan misalan su ne na rubuta **ai** da harafin **y**, a maimakon ninka harafin **y** xin. Don haka **bayyana** da **ayyuka** za a rubuta ba baiyana da aiyuka ba.

Dangantakar Harafin m da n a Cikin Kalmomi

Waxannan baqaqe guda biyu, wato **m** da **n** baqaqe ne da suke yi wa junansu shigar giza-gizai, musamman a maganganu na baka na yau da kullum. Sau da yawa akan yi amfani da xayansu a muhallin da xayan ya kamata ya kasance. Saboda haka ya zama wajibi a iya tantance muhallin da ya dace a yi amfani da kowanne daga cikinsu, bisa qa'idar rubutun Hausa. Daga cikin muhallinsu akwai:

A koyaushe ana rubuta harafin m a tsakiyar kalma idan baqin da yake biye da ita baleven harafi ne (harafin da leven sama da na qasa suke haxuwa wajen furta su),

wato b v f m, misali:

baleven b

tumbi	ba	tunbi	ba
tambari	ba	tanbari	ba
gumba	ba	gunba	ba
ambaliya	ba	anbaliya	ba
gambara	ba	ganbara	ba

baleven v

hamvare	ba	hanvare	ba
zumvure	ba	zunvure	ba
tumvuke	ba	tunvike	ba
jimviri	ba	jinviri	ba
vamvare	ba	vanvare	ba

baleven f

rumfa	ba	runfa	ba

atamfa ba atanfa ba

tumfafiya ba tunfafiya ba

gurumfa ba gurunfa ba

baleven m

kammalawa ba kanmalawa ba

yamma ba yanma ba

gammo ba ganmo ba

kamfani ba kanfani ba

To, amma ana rubuta baqin n a sauran muhallan, wato inda ba baleven harafi ba ne ya zo a gaba ba, misali:

gungume ba gumgume ba

tuntuve ba tumtuve ba

ganzaki ba gamzaki ba

gansheqa ba gamsheqa ba

Haka nan, ana rubuta harafin n a qarshen kalma ko da kuwa kalmar da take gabanta ta fara ne da baleven harafi (wato b v f ko m), misali:

Yalon Bello ba yalom Bello ba

Ramin vera ba ramim vera ba

Gidan varayi ba gidam varayi ba

Fiffiken fara ba fiffikem fara ba

Hoton mota ba hotom mota ba

Dukkan kalmar da ke qarewa da baqin m ana barin ta haka nan, wato ba a sanya baqin n ya maye gurbinta kamar yadda yake kasancewa a yayin furuci ko maganganu na yau da kullun, misali:

mutum ba mutun ba

kullum ba kullun ba

malam ba malan ba

jingim ba jingin ba

Kalmomin amsa-kama da suke qarewa da harafin m su ma ana barin su da m xin, misali:

zugudum ba zugudun ba

cinjim ba cinjin ba

kwatsam ba kwatsan ba

gam ba gan ba

(Galadanci 1976:108-109)

Ana samun kwamacala a kan abin da ya shafi wannan qa'ida. Ga misalai:

(66) *Ba shakka Sanata Usman Abdulaziz mutum ne da ya iya hulxa da jama'a da son ganin ya bayar da qwaqqwaran* ***gudunmuwa*** *wajen ci gaban al'ummarsa da qasa baki xaya.* ***Gudunmuwarsa*** *a cikin Majalisar Dattawa Ta Qasa a bayyane take ganin irin yadda yake taimakawa wajen gabatar da qudurori masu alfanu ga al'umma....*
(Muryar Arewa, fitowa ta 8, Maris 2012:18)

(67) Shi kuma Samson ya fara ne lokacin da neman sanin "Nawa ***gudunmuwar*** *a matsayina na xan qasa", da tarihi tare da tambayoyi. Ya jefa ma xalibam tambayoyi da yawa don ya fahici ko suna fahimtar abin da ake koyar da su a matsayinsu na 'yanqasa...*

A misali na 66 da 67 an sanya harafin **n** a maimakon harafin **m** a kalmar **gudunmuwa** a maimakon **gudummuwa** kamar yadda (Galadanci 1979:108-109) ya bayyana.s

Maimaicin Tagwayen Haruffa

Idan aka samu maimaitawar tagwayen haruffa a cikin rubutun Hausa, ana maimaita harafin farko ne kawai ba tare da maimaita na biyun ba misali

shasshafa ba shashshafa ba

gyaggyara ba gyagygyara ba

(Ado da Rabeh 2008:16)

(68) *...Allah ta'ala yana cewa ga Manzon Sa sallallahu 'alaihi wa sallam '... inda ka kasance mai kaushin hali, mai* ***qeqasheshshiyar*** *zuciya da (sahabbai) sun watse daga gare ka…..'. Suratul Aali Imran aya ta 159.*
(At-Tatbiq fitowa ta 189 ta ranar Juma'a 13 zuwa Juma'a 27 ga Mayu, 2011:6)

(69) *Kuma ka sani, ya Muhammadu wanda ya yi waiwaye a cikin sallarsa, to Ubangiji zai sa a mako masa sallarsa a fuska. Idan kuwa ya rinjaye ni a cikin sallarsa, ya zo ya yi ta shi kadai, to sai in sanya shi ya yi ta a ciki gaggawa, ya dinga dungura ta kamar yadda zakara yake* ***tsatstsagar*** *dawa, nan da nan kamar koton kurciya....*
(Kunnen Gari, fitowa ta 3, Mayu 2012. Sh: 30)

A wannan misali an samu maimaicin tagwan harafin '**sh'** da '**ts'**, amma a maimakon a maimaita harafin farko na '**s**' da '**t**' kalmar ta zama **qeqashesshiyar** zuciya da **tsattsagar** dawa sai aka maimaita dukkan haruffan ta zamo **qeqasheshshiyar** zuciya da **tsatstsagar** dawa.

4.2.4 Alamomin da Ake Amfani da su a Rubutu

Waxannan waxansu alamomi ne waxanda ake amfani da su domin rarrabewa ko nuna dangantaka tsakanin jimloli ko sassan jumloli. A taqaice dai, wasu alamomi ne da ake yi a cikin rubutu domin fayyace wasu abubuwa da rubutun ke nufi ko domin rarrabe wasu jimloli da wasu. Da alamomin rubutu ne ake qawata rubutu da dokar karatu da rubutu ta aminta da su. Ingancin rubutu da ci gabansa ya dogara a kan alamominsa da ke tafiya tare da su.(Bunza 2002:165)

Aya

Aya kalma ce ta Larabci wadda take nufin alama ko wurin tsayawa a karatu. Aya ita ce alamar da aka fi amfani da ita daga cikin alamomin rubutu. Haka nan, babu wata jimla da za a rubuta ba tare da an yi amfani da aya a qarshenta ba. Aya alama ce mai nuna kammaluwar zance, wato dai ita ce ke nuna cikar ma'anar

zance ko jimla; ashe kenan, ita ce iyakar jimla ko zance, kuma da ita ake rufe magana ko jimla.

Dukkan zancen da ya zo bayan aya sabon zance ne, saboda haka, duk harafin da ya biyo dole ne ya kasance babban harafi ne. A wajen mai karatu, ana buqatar ya dakata domin numfasawa a duk lokacin da ya zo kan aya yayin karatunsa. Ashe aya a wajen mai karatu babbar dakatawa ce wadda ke bayar da damar numfasawa. Idan ya yi haka, sai ya ji daxin tashi da karatunsa da sabuwar murya. Ga misalan yadda ake amfani da aya a qarshen jimla:

(70) *.....gwamnan jihar ta Katsina ya taka rawar gani wajen samawa matasar jihar ayyukan da za su* ***dogara da kansu, a cewarsa*** *gwamnan ya buxe cibiyar koyawa matasa sana'o'in hannu wanda yin hakan zai taimaka wajen rage zaman kashe wando ga matasan jihar bakidaya.*
(Jaridar Leadership Hausa ta ranar Juma'a 9-15 ga Maris 2012:9)

(71) Malam Hassan Muhammadu tsoho ne tugub tunda har jikinsa ke karkarwa a uk lokacin da zai amsa tambaya. Ya kan yi murmushi da ***nuna tawakkali. Da farin cikin cewa*** *ya yi shekarunsa 60, amma ya jaddada cewa ya zarce 60.*
(Mujallar Kulawa ta Janairu/Farurairu 2005:14)

A misalin da ya gabata, an yi amfani da alamar waqafi a maimakon aya, domin kuwa a misali na 70 inda aka rubuta …za su **dogara da kansu**… aya ya kamata a sanya, sannan '**a cewarsa** gwamnan ya buxe…' ta fara da babban harafi. A misali na 71 kuwa daga **don ganin an karya addinin musulunci,** jimlar ta qare, sannan **Allah yasa mu dace** wani sabon zance ne ya kamata a sanya aya ba waqafi ba. Kuma harafin farkon jimlar ya kasance babban harafi.. a misali na 71 kuma sanya aya aka yi a tsakiyar jimla a maimakon a qarshenta, don haka jimlar ba ta bayar da wata cikakkiyar ma'ana ba.

Waqafi

Ita ma kalmar waqafi kalma ce mai asali daga harshen Larabci, wadda take nufin dakatawa. A rubutu waqafi yana nufin ‘yar dakatawa ta xan lokaci. Idan aka zo a kan waqafi mai karatu zai xan tsaya ba da jinkiri da yawa ba. A wajen mai karatu waqafi wata alama ce ta dakatawa, sai dai dakatawar ba ta kai tsawon ta aya ba, wato dai ‘yar taqaitacciyar dakatawa ce. Wannan jinkiri shi ne yake bai wa mai karatu damar numfasawa. Waqafi kan zo a matsayin gavar zance ko jimla, kuma ajiye numfashi kawai ake yi a ci gaba da karatu, ma’ana ba a dakatawa gaba xaya da nufin kammaluwar ma’ana.

Idan an yi amfani da alamar waqafi, ana ci gaba da rubutu da qaramin harafi ne, sai fa idan sunan yanka (wato sunayen mutane ko garuruwa ko unguwanni ko qasashe ko koguna ko tsibirai da sauran makamantansu) suka biyo bayanta. Daga cikin wuraren da ake amfani da waqafi a wajen rubutu akwai:

- Wajen raba vangarorin jimla, musamman sarqaqqiyar jimla da harxaxxiyar jimla.

Sarqaqqiyar jimla ita ce wadda aka haxe jimla mai ‘yanci da maras ‘yanci suka zama jimla guda, misali:

a. Da zarar an fahimci juna, yana da wuya a riqa samun faxace-faxace a cikin al’umma.
b. Kar ka yarda da abin da take faxa, in ba haka ba kuwa ka ji kunya.
c. Jamilu yakan zo makaranta, ba tare da ya ci abinci ba.

Ita kuwa harxaxxiyar jimla ita ce wadda aka haxe jimloli biyu ko fiye masu cikar ma’ana suka zama jimla xaya, misali:

a. Usman yana aiki, Amiru kuwa yana barci.
b. Dila bai yi musu ba, suka taho da biri har gefen gari.

- Wajen gabatar da maganar wani kai tsaye, wato dai ana sanya alamar waqafi kafin sanya alamar qauli (zancen wani), misali

a. Mutumin ya ce masa, “Ba ka ji sunan garin ba?” Ya ce, “Na ji”

b. Malam Dogo ya dubi dutse ya ce, “Fayau, buxe dutsen kuxi!”

- Wajen raba zance mai xauke da sharaxi da kuma jawabin sharaxin. Wato ma’ana bayan gabatar da sharaxin sai a sanya alamar waqafi kafin gabatar da abin da zai faru bayan cikar shaxin, misali:

a. Idan ba ka gaji ba, ga wani aikin nan ka ci gaba.

b. Ka nisance ta, in ba haka ba ta cuce ka.

c. Da an ce yaro ya kangare, yana da wuya a iya tanqwara shi.

- Wajen rarraba ayyuka da suka kai biyu ko fiye a cikin jimla guda, wato dai ko an yi amfani da kalmomin mahaxi ko kuwa ba a yi ba, misali:

a. ‘Yan kasuwa suka zo, su ga kayan, su saya, su sayar, sannan su koma garuruwansu.

b. Musa kan tashi da safe, ya yi wanka, ya ci abinci, sannan ya tafi makaranta.

- Haka kuma ana sanya alamar waqafi kafin gabatar da kalmomin mahaxi; wato kalmomin da ake amfani da su domin haxe vangarorin jimla, misalin waxannan kalmomin su ne: **sai** da **amma** da **kafin** da **sannan** da **duk da haka** da **sai dai** da sauransu, misali:

a. Shugaban ya shigo,amma bai zauna ba ya fita abinsa.

b. Tun da Kabir ya shigo, sai Tanko ya fita.

c. Na ji jawabinka, duk da haka ka yi haquri.

(72) *Sufeto janar na ‘yan sandan qasar nan, mohammed Abubakar, ya tabbatar da cewa lallai rundunar ‘yan sandan qasar na tattare da **ximbin matsaloli amma cewa ya soma** xaukar matakin magance su xaya bayan xaya*
(Jaridar Kariya ta 9-22 ga Maris, 2012:5)

(73) *Ko a matakin mazavarsa bai yi wa al’ummarsa nisa ba domin yakan ziyarce su akai, akai tare da sauraren buqatunsu da kuma tabbatar da cewa kwalliya ta biya kuxin sabulu.*
(Muryar Arewa, fitowa ta 8 ga watan, Maris 2012:18)

Akwai kuskuren rubuta sunan **Muhammed** da aka fara da qaramin baqi, amma kuskuren da ya shafi waqafi a nan shi ne daga '**ximbin matsaloli'** kafin 'amma cewa…' akwai alamar waqafi da ya kamata a sanya; sai jimlar ta kasance kamar haka, '…**rundunar 'yan sandan qasar na tattare da ximbin matsaloli, amma cewa ya soma**…'. A misali na 73 kuwa an yi amfani da waqafi a maimakon karan-xori (akai, akai a maimako a-kai-a-kai).

Alamar Tambaya [?]

Kamar yadda sunanta ya nuna, Alamar tambaya alama ce da ake ajiye ko kammala zance da ita. Ana amfani da ita a qarshen jimlar tambaya. Dukkan harafin da ya zo bayan alamar tambaya dole ne ya kasance babban harafi domin kuwa sabon zance ne. Murya kan sauka ne a duk lokacin da aka yi amfani da wannan alama (Wurma 2005:79).

a. Me kake buqata?

b. Ina za ka je?

c. Yaushe za ka tafi?

Dukkan jimlar da ta fara da **me** ko **yaushe** ko **ina** ko **wa** ko **wane** to akwai alamar tambaya. Haka kuma, rashin amfani da alamar tambaya na iya sauya ma'anar jimlar, misali:

a. Wannan gidan sarki ne? (tambaya)

b. Wannan gidan sarki ne. (tabbataccen zance)

a. Shugaban taron ya zo? (tambaya)

b. Shugaban taron ya zo (tabbataccen zance)

Dukkan harafin da ya biyo bayan wannan alama dole ne ya kasance babban harafi. Ashe alamar tambaya tana xaya daga cikin alamomin ajiye magana.

(74) ***KUN SAN KUNYA KUWA ???***
(At-tatbiq, fitowa ta 227, ranar Juma'a 11 zuwa 27 ga watan Janairu, 2013. Sh7)

Yin amfani da alamar tambaya fiye da xaya a qarshen jimla kuskure ne, don haka da alamar tambaya guda xaya ake qare jimlar tambaya, ba kamar yadda ya gabata a misali 74 ba.

Alamar Motsin Rai [!]

Wannan alama tana xaya daga cikin alamomin tsayar da magana don haka babban harafi kan biyo bayanta, domin kuwa alama ce ta ajiye magana. Alamar motsin rai alama ce da take nuna zancen da aka yi cikin vacin rai ko fushi ko tausayi ko mamaki ko tsoro ko kwaratsi ko xoki ko dai wani abu mai sosa zuciya ko jan hankali. Alamar motsin rai alama ce da take nuna kalamin da aka yi cikin vacin rai ko baqin ciki ko razana ko tausayi ko murna ko tsoro ko fushi ko wuya ko kwaratsi ko xoki ko dai wani abu mai sosa zuciya ko jan hankali (Sa'id 2004:19/Wurma 2005:80). Lura da waxannan misalai:

i. Tausayi:

a. Wayyo! Allah ya ba shi lafiya.

b. Kaico! Ashe haka abin ya faru?

c. Ikon Allah! Bai san za su cuce shi ba.

ii. Haushi ko fushi.

a. Ahayye! Yau ana teburin giwa.

b. Kash! Wannan maganar tasa ba ta dace ba.

c. Kai Waldima, ni ne zan ci abincinka kyauta! Ni za a faxa wa haka a cikin mata!

iii. Wuya ko tsoro.

a. Wayyo Allah! An riqe mani qafa.

b. Wash! Don Allah ku taimake ni.

c. Kash! Wa ya ce ku gaya musu?

iv. Qara ko kwaratsi.

a. Yana cikin tafiya sai ya ji an kwaxa masa kira Maidabo! Maidabo!! Maidabo!!! Har sau uku.

b. Da sarkin yaqi ya ji haka sai y ace, “Qaryarku arna!. Ta Allah ba taku ba.”

c. Kabir yana cin abinci, sai ya ji qara kwarats! Ya tashi ya ruga a guje

v. Murna ko xoki

a. Da malamin ya ji haka sai ya ce, “Alhamdu lillahi! Allah ya tarfa wa garinka nono.”

Akan samu kuskuren bin wannan qa’idar a jaridu ko mujallu, misali,

(75) *Xan uwa maikaratu nasan kaima kana ganin yadda kunya ta zama zama a yau, ta zama abin cewa* ***kash!!!*** *Wani abin haushi ma da takaici shine za kaga mace matar Aure mai mutunci tana tafe tana cin abinci ko tana shan Rake ko Gyaxa ko dai wani abu wanda koda namiji bai daga cikin kamala a gare shi a ga yana ciye-ciye aka Titi balan tana ‘ya mace…….*
(At-tatbiq, fitowa ta 227, ranar Juma’a 11 zuwa 27 ga watan Janairu, 2013:3)

*(76) Ya ku ‘****yan uwa! ta yaya*** *za ku ji dadi a duniya alhali Mala’ika mai kaho ya dora kaho a bakinsa, yana sauraron izinin Allah, yaushe za a umurce shi da busawa, sai ya busa. To a wannan lokacin tsoron busar zai firgitadda duk halittun sammai da kasa. Sai fa wanda Allah ya so ya tsare kawai.*
Jaridar Gamzaki ta ranar 27 ga Oktoba zuwa 4 ga Nuwamba 2006:10

A nan akwai kuskuren shi ne iri biyu; na farko an yi amfani da alamar motsi rai fiye da xaya (yin haka ya sava qa’ida), na biyu kuma an yi amfani da qaramin harafi bayan an yi amfani da alamar tsayar da magana domin alamar motsin rai tana xaya daga cikin alamomin da ake tsayar da magana da su (duk abin da ya zo bayansu dole ne ya kasance babban harafi domin kuwa sabon zance ne). Haka ma kuskure ne amfani da alamar motsin rai fiye da xaya a cikin jimla domin kuwa da zarar an yi amfani da xaya to yana nuna zance ya qare.

Karan-Xori [-]

Wannan alama ce da ake amfani da ita a wurare da dama a cikin rubutu, kuma kamar yadda sunan ya nuna, alama ce da ake xora kalmomi da ita a cikin rubutu. Wuraren da ake amfani da ita sun haxa da:

1. Wajen da aka yi auren kalmomi, wato wajen da aka haxe kalmomi biyu ko fiye da haka masu ma'ana daban-daban domin su samar da kalma guda xaya wadda ke xauke da ma'ana daban da ma'anoninsu na asali. Daga cikin irin waxannan kalmomi akwai:

a. Harxaxxen suna: Irin wannan suna kan samu ne ta hanyar tattaruwar kalma biyu ko fiye don su samar da suna guda (Galadanci 1976:111/Sa'id 2004:19), misali:

fid-da-sartse	kwale-kwale	qyal-qyal-banza
cin-da-zugu	tuma-qasa	bar-ni-da-mugu
farar-wuta	tu-mazagi	shiga-da-alwalarka
farar-qasa	cin-zanzana	faxi-ka-mutu
karya-kumallo	a-kori-kura	ihunka-banza
mace-da-goyo	gaya-wa-jini-na-wuce	

b. Tagwan sifa (sifa nanatau): irin wannan sifar na samuwa ne a yayin da aka ninka sassauqar sifa a wajen siffanta suna, misali:

Riga fara-fara
Yaro dogo-dogo
Hatsi buhu-buhu
Sutura launi-launi
Kaya iri-iri
Zare kala-kala
Takalma qafa-qafa

2. Wajen samar da jam'in wasu kalmomi da akan samar da jam'insu ta hanyar cikakken ninkai, misali:

Tilo	Jam'i
talla	tallace-tallace
sata	sace-sace
rubutu	rubuce-rubuce
karatu	karance-karance
saqa	saqe-saqe

3. Wajen maimaita kalma domin qarfafawa a cikin zance ko magana, misali:

a. Yanzu-yanzu Usman ya tafi gida, idan kana son samun sa ka yi maza-maza ka tafi gidansa

b. Yawan tsugune-tsugune a ofisoshin shuwagabanni da yin gulmace-gulmace ba ya da wani amfani

4. Ana sanya karan-xori tare da wasu kalmomin amsa-kama, misali:

a. Mahaukacin ya wuce buguzum-buguzum kamar ana cizon sa.

b. Rubutun da babu bin qa'ida ya zama fankam-fayau.

c. Lumbu-lumbu, wutar qaiqai.

(Ado da Rabeh 2008)

(77) ***YANDAKA-BA BARA BA ABOKIN SHAWARA***
(Mujallar Dakin Kara, Fitowa ta biyu, Maris 2009:11)

(78) ***ALMAJIRCI DA BARACE BARACE***
(Mujallar Dakin Kara, Fitowa ta biyu, Maris 2009:1)

(79) *Wannan dangantaka takan soma ne a yayin da mace da mace suka zauna kusa da kusa, ana zama za a fara gaisawa, daga nan kuma sai a fara musayar murmushi zuwa dariya zuwa kuma magana* ***jefi jefi.*** *Zumuncin ya fi saurin qulluwa idan akwai yara a tsakani. Inda xayar za ta dinga yi wax an xayar wasa , har a kai gab a shi abinci kamar alewa ko biskit, inda ita kuma uwar yaron za ta ji daxi an kula xanta. Shikenan kuma kin ci nasara akanta don ki na qaunar xanta.*
(Jaridar Rariya ta ranar 9-22 ga watan Maris, 2012:17)

Yin amfani da karan-xori a kanun labari a misali na (77) kuskure ne domin kuwa kalmar korewa ta '**ba'** ba a haxe ta da wata kalma. A kan labari na biyu kuwa (misali na 78) kalmar '**barace-barace**' jam'i ce ta bara, ya kamata a sanya karan-xori a tsakaninsu (domin kuwa kalmar ce gaba xaya aka maimaita). A misali na (79) kuwa an sami tagwan sifa wadda akan samu karan xori a tsakanin kalmomin. Rashin sanya karan dori a misali na (78) da na (79) kuskure ne, amma sanya shi a misali na (77) kuskure ne.

Alamar Tsakure[" "]

Wannan alama ce mai nuni da zancen wani. Mai rubutu zai kawo zancen da wani ya yi a cikin rubutunsa. Akan sanya zance da wani ya faxa kai tsaye, wato ba tare da an qara wani abu kome qanqantarsa ba. Ana sanya waxannan alamomi ne daga sama. Alamu ko waqafi biyu na farko alamu ne na buxe magana, alamu na biyu na qarshe kuwa alamu ne na rufe magana. Duk harafin da ya biyo bayan alamun buxe magana dole ne ya kasance babban harafi ne. Ana sanya waqafi kafin sanya alamun buxe magana (Bunza 2009:43-44) Misali:

Ya tambaye ni uwar xakinsa, na ce, "Ajali ya same ta a can qasar aljannu."

Idan maganar da wani ya yi gutsuro ta aka yi, ma'ana ba daga farko aka gutsuro ta ba, akan sanya alamar zarcewa wato ayoyi guda uku sai a ci gaba da kawo zancen, amma harafin farko ya kasance qaramin baqi, misali:

…. ya ce "… ai ba ku kuka tsamar da ni ba, Allah ne ya tsamar da ni"

Haka kuma idan ba a kai qarshen maganar da aka tsakuro ba, akan sanya waxannan ayoyi guda uku kafin a rufe tsakuren, misali:

"Ta marabce shi ta kawo masa ruwa ya sha..."

(80) *... Sannan ya ce,"muna yin wannan ne domin fahimtar da al'uma su kara ba shema dammar samun ci gaba da mulkin jihar katsina a shekara ta 2011".*
(Mujallar Gani Da Ido, maganin Tambaya ta watan Mayu, 2009:7)

(81) *…Haka kuma wakilin namu ya buga ma shugaban waya amma kuma bai samu amsar komi ba akan haka, sai dai kuma shugaban ya shedawa wata kafar watsa labarai ta kasashen Turai cewa, "shida jam'iyyar PDP mutu –ka-raba".*
(Mujallar Kunnen Gari, (in ka ji, kowa ya ji) Fitowa ta 1 ta watan Maris, 2012:27)

A dukkan misalan a aka bayar an fara rubutu da qaramin harafi bayan an buxe alamar tsakure. Yin haka kuskure ne domin ba a tsakiyar jimla aka yi tsakuren ba.

Alamar Hamza [']

Alamar hamza waqafi ne da ake sanyawa a saman gavar kalma (ba a qasa ba) domin rabawa tsakanin gavar da ta qare da wasali da kuma maqwabciyarta da ta fara da wasali (ba a amfani da wannan alama a farkon kalmar da ta fara da wasali). Ana amfani da wannan alama ne saboda dalilai guda biyu: Na farko domin nuna cewa ba xaurin wasali ko tsawon wasali ake nunawa ba, na biyu kuwa domin sauqaqa furuci (Bunza 2002:184-186), misali,

Ma'ana	Mu'amala	Ba'a
Da'awa	Xa'a	Addu'a
A'isha	Mu'azu	Sa'adatu
Bidi'a	Xabi'u	A'a

Rashin amfani da wannan alama kan sanya furucin kalmar ya yi wuya ko kuma a ji kamar ba kalmar Hausa ba ce, misali,

(82) *Sai ya kasance ba ya sauraren kowa sai ni, kuma baya biyayya ga kowa sai ni, Ya Muhammadu ina aikin* ***alummar*** *taka ya ke? Gani ina umarnin talakawa ina cewa da su Sallah ba ta talakawa ba ce ……. (Kunnen Gari, fitowa ta 3, Mayu, 201:30)*

(83) ..Allah ta'ala yana cewa ga Manzon Sa sallallahu 'alaihi wa sallam '… inda ka kasance mai kaushin hali, mai qeqasheshiyar zuciya da (sahabbai) sun watse daga gare ka…..'. Suratul Aali Imran aya ta 159.

(At-Tatbiq fitowa ta 189 ta ranar Juma'a 13 zuwa Juma'a 27 ga Mayu, 2011:6)

A misali na 82 kalmar **al'umma** da ba a sanya alamar katsewa tsakiyarta ba sai kalmar ta yi bambarakwai wato kamar ba kalmar harshen Hausa ba. A misali na (83) kuwa an sanya alamar katsewa a muhallin da bai dace ba domin kuwa ba a sanya wannan alama a gavar farkon kalma da ta fara da wasali (sai dai idan a tsakiya ko qarshen kalma gavar take) kamar dai yadda bayani ya gabata.

4.3 Allunan Talla

A qoqarin tallata haja ko wayar da kan jama'a ko faxakar da su a kan wani al'amari, akan samu matsalolin rubutun da ake isar da saqon. Ire-iren matsalolin da ake samu sun haxa da kuskuren haxe kalma ko rabawa a muhallin da bai dace ba da rubuta kalmomi ba daidai ba da kuma gwamutsa Hausa da wani harshe, musamman ma harshen Ingilishi.

a Kuskuren Haxa Kalma a Muhallin Rabawa

Irin wannan matsala tana samuwa ne a yayin da aka haxa kalmomi a maimakon a rubuta su a rabe. An fi samun irin wannan matsala a kalmomi masu gava xaya. Misali,

(84) *"Sauran mata a kodayaushe suna yaba girkina"*
*...**zaisa** ki ki **kware** a girki.*
(Duba rataye na 5a)

A wata tallar kuma an rubuta kamar haka,

(85) *"Girkinta **shine** mafi kyau"*
*...**zaisa** ki ki kware a girki.*
Allon tallar Vedan (Duba rataye na 5b)

*(86) Ingancin da **zaka** amince dashi*

Allon tallar fulawar Honeywell (Duba rataye na 6)

An haxe kalmar '**zai'** da '**sa'** a matsayin kalma xaya a maimakon a rubuta kowace daban. Haka nan rashin amfani da harafin '**q**' ya sanya kalmar '**kware'** ta

yi kamar ba Hausa ba. A talla ta biyu (misali na 85) kuma an haxe kalmomin '**shi'** da '**ne'** a matsayin kalma xaya. A misali na 86 kuma an haxe manunin lokaci na lokaci mai zuwa na '**za'** da wakilin suna na '**ka'**, haka nan an haxe zagin '**da'** da wakilin suna '**shi'**.

b Kuskuren Raba Kalma a Muhallin Haxawa

Wannan kuskuren yana faruwa ne a sakamakon raba kalma maimakon haxewa, musamman a wajen rubuta mallaka ko kuwa don tsawon kalmar. Misali.

(87) *In zazzabin cizon sauro ya kama ka nemi magani mai wannan alama ACTm da hoton ganye kawai. Kuma kyauta ne a wasu asibitocin Gomnati. Yanzu ne yakamata mu nuna kwazonmu, ka bada Gudumuwar ka yanzu!*
Allon tallar maganin zazzavin cizon sauro na ACT. (Duba rataye na 7)

A misalin da ya gabata (87) akwai kurakurai dadama, na farko na rubuta kalmar Gomnati a maimakon gwamnati, na biyu kuwa shi ne na rubuta kalmar mallaka a rabe, wato **Gudumuwar ka** a maimakon **Gudumuwarka**. Sannan an rubuta kalmomin ya kamata a rabe. Haka nan ya kamata a sanya aya bayan kalmar **qwazonmu**, sannan kalmar da ta biyo baya (**ka**) ta fara da babban harafi.

c Rubuta kalmomi bisa kuskure

A nan akan rubuta kalmomi bisa kuskure. Mafi akasari hakan kan faru ne kasancewar masu irin waxannan rubuce-rubuce ba Hausawa ba ne ko kuma ba su da masaniya a game da rubutun Hausa, don haka sai su rubuta kalma kamar yadda kunnensu yake jiye masu ko yadda suke furta kalmomin. Misali,

(88) *Uwa da babi irinta*
Noodles da babu irinta
Allon tallar taliyar Indomie (Duba rataye na 8)

d Gwamutsa Hausa da Ingilishi

(89) *see who's using glo premium...*
mai gida da kainsa.
(Allon tallar kamfanin Glo)

(Duba rataye na 9)

A misali na (88) an rubuta **babi** a maimako **babu**, sannan a misali na (89) an samu matsaloli har iri uku a cikin layi uku da aka yi amfani da su don yin wannan tallar. Matsala ta farko dai ita ce ta fara gabatar da tallar da Ingilishi aka kammala ta da Hausa. Ta biyu ita ce ta raba kalmar **maigida**, sannan matsala ta uku ita ce ta rubuta **kainsa** a maimakon **kansa**.

e Rashin Amfani da Daidaitacciyar Hausa

Irin wannan matsala ta qunshi amfani da wani kari wanda ba daidaitacce ba, wani lokaci ma akan yi amfani da kari fiye da xaya a yayin gudanar da rubutu. Misali.

(90) *Kutabbatar anyima yaranku rigakafi*
Alluran rigakafi kyautane!
Muhadakai domin mu kawar da cutan
Sha'inna a Nigeria
(Duba rataye na 10)

A wannan misali akwai matsalar haxe kalma bisa kuskure, inda aka haxe kalmomi (**anyima**) a maimakon a raba su, aka yi amfani da karin harshen Katsinanci da Zazzaganci (**cutan**), sannan aka rubuta kalmar shan'inna bisa kuskure (**sha'inna**), kuma aka rubuta **Nigeria** da tsarin Ingilishi. Kamata ya yi jimlolin su kasance kamar haka,

(91) *Ku tabbatar an yi wa yaranku riga-kafi.*
Allurar riga-kafi kyauta ne!
Mu haxa kai domin mu kawar da cutar
Shan'inna a Nijeriya
A wani misalin kuma,

(92) *INUWA BAKYA*
KYAMAR KOWA

Allon taya Gwamna Shema murnar naxa shi Sarkin Yaqin Hausa.

(Duba rataye na 11)

A misali na 92 kuwa amfani aka yi da karin harshen Katsinanci (**bakya**) a maimakon a yi amfani da daidaitacciyar Hausa (**ba ki**).

4.4 Abubuwan Hawa

Rubutu a jikin abubuwan hawa ba sabon al'amari ba ne. Akan yi irin wannan rubutu ne mafi akasari don yin habaici ko gugar zana game da wani al'amari (Bunza 2005:17). An fi samun irin waxannan rubuce-rubuce a jikin abubuwan hawa da suke na haya ne. Akwai rubutun da akan yi ta amfani da fenti, musamman a jikin motoci, akwai kuma wanda akan yi a jikin takardu (stickers) da ake liqawa. Da yawa daga cikin ire-iren waxannan rubuce-rubuce suna cike da kurakurai, musamman ganin cewar direbobin ne suke rubuta abin da suke so a sanya a jikin ababen hawansu ko kuma su faxa wa marubutan abin da suke so a rubuta masu a jikin abin hawansu. Waxannan masu sana'a ta yin rubuce-rubuce a jikin motoci ba su da cikakken ilimi a game da rubutun Hausa don haka ne ake samun kwamacala iri daba-daban. Misali sau da dama masu abubuwan hawa kan liqa '**KAKINI DUBU SUSONI**' a jikin abin hawansu. A irin waxannan rubuce-rubuce akwai kurakurai da suka haxa da haxe kalma ko rabawa a muhallin da bai dace ba rubuta kalmomi bisa kuskure. Misalan ire-iren kurakuran sun haxa da:

(93)

(i) Allah yatsare
(ii) Tafiya tafizama
(iii) Kabassu
(iv) Alherine
(v) Bajira
(vi) Abarwa Allah yafiayitsafi
(vii) Fadi alheri kokayi shiru.
(viii) Jamuje

A misalan da aka gabatar a 93 an yi kwamacala iri biyu; ta farko ita ce ta haxe kalmomi a muhallan raba su, ta biyu kuwa ita ce tahaxe wakilan suna da kuma nashe su a matsayin kalma xaya (iii). Ga yadda ya kamata su kasance:

(i) Allah ya tsare
(ii) Tafiya ta fi zama
(iii) Ka bar su
(v) Ba jira
(vi) A bar wa Allah ya fi a yi tsafi
(vii) Faxi alheri ko ka yi shiru

(iv) Alheri ne (viii) Ja mu je

4.5 Sauran Rubuce-rubuce

Sauran wureren da ake samun matsaloli a fagen rubutun Hausa sun haxa da katin gayya da rubutun da ake yi a wurare don sanar da jama'a ko faxakar da su a kan wani al'amari da allunan da akan yi amfani da su don sanarwa (sign boards) da takardu da ake amfani da su a fagen kiwon lafiya da sauran makamantansu. Misali sau da yawa akan rubuta,

Malam anhana zuba shara anan (rataye na 12)

Ana sayarda katin waya anan

Doka anhana fitsari anan (duba rataye na 13)

Haka nan ma kamfanoni kan buga qananan takardu don tallata hajarsu ko yin qarin bayani a kan abin da suke sayarwa. Akan samu matsalolin rubutu a irin waxannan takardun. Misali:

Mai gida da kainsa

Kamfanin glo

San'u da zuwa

Fadi abinda kake so ka fadi

Kamfanin MTN

Karin Dibara

(Abdulmumini 2010:59)

4.6 Naxewa

A wannan babi an gabatar da yanayin kwamacalar da ake samu a jaridu da mujallu da allon talla da abubuwan hawa, musamman motoci ta hanyar kawo yadda aka gabatar da rubutun a waxancan wurare, da kuma inda kurakuran suke. An yi haka ne domin nuna yadda yanayin kwamacalar yakan kasance.

BABI NA BIYAR

DALILAN KWAMACALA DA MATAKAN GYARA

5.0 Gabatarwa

Bayanai sun gabata a game da qa'idojin rubutu da kuma yadda ake sava su a cikin rubuce-rubucen da ake yi a littattafai, musamman masu bayani a kan qa'idojin rubutu, da jaridu da mujallu da allunan talla da abubuwan hawa da ma sauran rubuce-rubuce. Wannan kwamacala tana faruwa ne saboda wasu dalilai da suka shafi marubuta da editocin da kuma masu taimaka masu a wajen gudanar da aikinsu.

5.1 Abubuwan da Bincike ya Gano

Wannan bincike ya gano wasu muhimman abubuwa da suka shafi kwamacala a rubutun Hausa. Abu na farko shi ne binciken ya gano cewar kwamacalar da ta fi zama rowan dare ita ce ta haxa kalmomi a muhallin day a kamata a raba. Irin wannan matsala ta fi shafar kalmomi da gavovinsu ba su wuce biyu ba. Hakan kuwa yana faruwa ne ta dalilin rashin fahimtar cewar kowace kalma tana da rukuninta a nahawu, kuma ba kowaxanne rukunai ba ne ake haxewa a yayin rubutu ba.

Haka nan binciken ya gano cewar akwai wasu dalilai da suke haddasa kwamacala a rubuce-rubucen. Kamar yadda bayani ya gabata waxannan dalilai sun shafi marubuta da editoci ne da masu taimaka masu wajen gudanar da ayyukansu. Waxannan dalilai sun haxa da:

Rashin Sani

Dalili na farko da ke haddasa kwamacala a rubuce-rubuce shi ne rashin masaniya game da shi kansa rubutun Hausa. Rashin sani shi ne babban abin da ke haifar da yin kwamacala a rubutun Hausa, musamman irin wanda ake yi a jikin motocin haya. Haka nan za a tarar cewa yawanci marubuta da editoci da wakilan da ke gudanar da aikin wallafa jaridu da mujallu ba su sami tarbiyya wadatacciya ba a game rubutun Hausa ba. Babu karatu mai zurfi a kan harshen Hausa ko qa'idojinsa ba, musamman masu yin rubuce-rubuce a jikin ababen hawa, kuma ba su yi wasu kwasa-kwasai masu nasaba da rubutu ba. Suna dai da tunanin cewar kowane Bahaushe zai iya rubuta Hausa.

A wasu jaridun akwai wannan matsalar kasancewar editocin da mataimakansu babu wanda ya karanta Hausa ko ya yi wani kwas a game da rubutun Hausa, don haka rubutun yakan kasance ba a bisa qa'ida ba. Haka nan dukkan waxanda aikin rubutu ko bugawa ya shafa babu mai masaniya a game da qa'idojin rubutun Hausa. Don haka babu wanda zai iya fahimtar kuskure bare ya yi gyara a kai. Ko da yake kurakuran da ake samu a wasu jaridu ko mujallu ko littattafai sun fi na wasu yawa.

A game da allunan talla kuwa da ganin wasu kurakuran za a iya fahimtar cewa ba ma Hausawa ne suke yin rubuce-rubucen ba, musamman ganin cewar ba qa'idar rubutu kawai ake karyawa ba har ma da qa'idar nahawun harshen Hausa. (Duba rataye na 14)

Qyuya

Qyuya tana sanadiyyar faruwar wasu abubuwa a yayin rubutun littattafai jaridu da mujallu. Daga ciki akwai barin kwamfuta tana yin gyara da kanta (auto corrections) wanda hakan yakan jaza rubuta wasu kalmomi a bisa kuskure domin

kuwa ita kwamfuta tana yin gyara ne a kan kalmomin da suka yi kama da na harshen Ingilishi. Misali:

(93) *Malamin ya kara da cewa idan al'umma ta zauna babu sa'ar yi to hakan ba'a bun da zai haifar sai zaman banza, sace-sace, fada-fade da neman kawo rashin zaman lafiya. Kuma a wani bangaren kuma Dattijon ya yi kira ga Gwamnati da ta* ***samara*** *ma matasa aikin yi don rashin* ***samara*** *da aiki ga matasa* ***yak an*** *sa matasan su fahimci rashin adalci daga gwamnati, har kuma zai yi bayuwa zuwa ga yi mata bore.*
(Jaridar At-tatbiq, fitowa ta 227, ranar Juma'a 11 zuwa Juma'a 27ga Janairu, 2013. Sh:2)

Wannan yakan haifar da rubuta kalmomi da jimloli marasa ma'ana kamar yadda aka nuna a misali na 93 inda aka rubura **samara** a maimakon **samar** da kuma kalmar **ya kan** a maimakon **yakan**.

Wani lokaci kuma ta dalilin qyuya, marubuta da editoci ba su sake bin abin da suka rubuta bayan an buga domin yin gyara a kalmomin da aka yi kuskure wajen rubuta su kafin gurzawar qarshe. Don haka sai a yi ta samun kalmomi da a wani lokaci an rubuta su daidai wani lokaci kuwa a rubuta su a bisa kuskure.

Haka nan saboda matsalar qyuya, dukkan takarda da wani ya rubuto domin bugawa a jarida akan buga ta ne kamar yadda mai ita ya aiko da ita, ba tare da yi mata wani gyara a game da qa'idar rubutu ba. Wannan shi ne yakan haifar da rashin daidaito a cikin rubutun don haka a wasu wuraren akan rubuta kalmomi daidai a wani wuri kuwa sai rubuta su a bisa kuskure.

Qyuya takan haifar da qin zama don koyon yadda ake yin rubutu daga masana ko ta hanyar littattafai masu koyar da yadda ake yin rubutu a Hausa. Da marubuta da editoci da wakilai da masu yin rubuce-rubuce a jaridu da mujallu za

su zauna su koyi yadda ake rubutun Hausa da an samu warware ko rage matsalar yin kwamacala.

5.2 Matakan Gyara

Babban mataki na farko da ya kamata a bi don kawo gyara a rubuce-rubucen waxannan kafafen isar da saqonni (da ma wasu) shi ne na samun editoci da suke da masaniya a game da rubutun Hausa. Rashin sanin qa'idar rubutu ita ce babbar matsalar da take haifar da kwamacala. Don haka wanda bai san qa'idar yin abu ba, ba za ya san cewar yana yin abun ba daidai ba, bare ma ya san matakin yin gyara. Don haka ya kamata editoci da wakilai da masu yin rubuce-rubuce a jaridu su san hanyar yin rubutun Hausa ta hanyar bin qa'idoji.

Hanya ta biyu ita ce ta halartar kwasakwasai da tarukan qara wa juna sani masu alaqa da rubutun Hausa daga lokaci zuwa lokaci don tabbatar da ganin marubuta, musamman editoci, suna halartar taron qara wa juna sani da kuma bin diddigin duk wani cigaba da aka samu a game da qa'idojin rubutun Hausa. Wannan zai taimaka wajen tabbatar da saqon da ake isarwa yana isa bisa ma'anar da ake son ya isa.

Wani matakin kuma shi ne na rage qyuya don kulawa da yin gyare-gyare ga abin da kwamfuta ke yi wa gyara, domin wani lokaci kwamfuta ce take yin gyara da kanta (auto correction). Wannan yakan taimaka wajen haifar da kwamacala a cikin rubutu. Su kuma masu buga labaru a kwamfuta su fahimci cewar yin gyara da kwamfuta take yi wa kalmomin Hausa yana sava qa'idar yadda ya kamata a rubuta su, don haka sai sun yi taka-tsantsan a yayin gudanar da aikinsu. Haka nan akwai buqatar samar da wani shiri na kwamfuta (coputer programme) wanda zai taimaka wajen yin gyara (auto correction) ga kalmomin Hausa bisa qa'idar rubutun harshen Hausa.

Masu karanta jaridu da mujallu suna da gudummuwar da za su iya bayarwa, musamman idan suka ci karo da wani abu da ba a rubuta shi a bisa qa'ida ba su jawo hankalin editoci da marubuta a game da gyaran. Wannan zai taimaka wa editoci wajen fahimtar kurakurai.

Akwai kuma buqatar shirya wa editoci da marubuta taruka na qara wa juna sani don faxakar da su muhimmancin qa'idojin rubutun Hausa da kuma illar da rashin amfani da qa'idar yake iya haifarwa. Haka nan akwai buqatar kafa wata hukuma wadda za a xora wa alhakin kula da ganin ana amfani da qa'idojin rubutu yadda ya dace a fagen wallafe-wallafe da ake yi a jaridu da mujallu da allunan talla ma sauran littattafai da ake wallafawa.

5.3 Matsalolin da Rubutun Hausa yake Fuskanta

Saboda harshe yana sauyawa, musamman saboda sauyawar zamani da qarin bunqasa da kuma cuxanya da sauran harsuna, dole ne a riqa cin karo da wasu matsaloli da suke ci wa rubutun Hausa tuwo a qwarya. Matsalolin sun haxa da:

Rashin Wadatattun Na'urorin Masu Rubuta Haruffan Hausa

Duk da kasancewar rubutun Hausa ya samu damar cin gajiyar qoqarin masana (irin su Uba Abdalla) ta hanyar sama masa hanyar rubutu a kwamfuta, har yanzu akwai sauran rina a kaba domin kuwa har yanzu akwai ayyukan masana da dama da ba a samu sanya su a yanar sadarwa ta internet ba, wadda tana xaya daga cikin hanyoyin samar da bayanai na zamani da ake amfani da su a duniya. Haka kuma duk wannan qoqarin da aka yi na samar wa Hausa mazauni a duniyar zamani yunqurin da masana a rubutun Hausa suka yi bai kai na a zo a gani ba, domin kuwa ana samun matsalolin rashin bin qa'idojin rubutu a cikin rubuce-rubucen da ake bugawa a shafukan yanar sadarwa ta internet. Ashe ya kamata a samu masana rubutun Hausa su yi ruwa da tsaki a cikin irin wannan harka, domin tabbatar da ana samar da bayanai sahihai ta amfani da sahihiyar hanyar rubutu ba kwamacala ba.

Rashin Qwararrun Malamai

Wata matsalar da kuma take ci wa rubutun Hausa tuwo a qwarya ita ce ta rashin qwararrun malaman da za su riqa koyar da rubutun Hausa tun daga makarantun firamare zuwa na sakandire ta yadda xalibai za su tashi da sanin qa'idojin rubutun Hausa. A mafi yawancin lokaci akan samu kurakurai a rubutun malamai waxanda suke koyar da Hausa a makarantun firamare da sakandire (har ma da gaba da sakandire kamar kwalejojin ilimi da na kimiyya da ma jami'o'i). Wannan ba ya rasa nasaba da rashin saka darussan qa'idojin rubutu a manhajar makarantun firamare da sakandire, domin bayar da damar bai wa xalibai darasi na musamman a kan qa'idojin rubutun Hausa. Don haka sai xalibi ya kai matakin gaba da sakandire ba ya iya bambance qa'idojin rubutun Hausa.

Rashin bai wa fannin Hausa Muhimmanci a Makarantu

Rashin bai wa wannan fanni na Hausa muhimmanci tare da rashin wadatattun littattafai na koyar da qa'idojin rubutu ya haifar da matsalar da dama daga cikin xalibai a makarantun sakandire ba su iya rubutu da sahihiyar Hausa ko bisa ingantaccen bin qa'idar rubutu (Sa'id 2002:137). A halin yanzu ma ana neman soke nazarin harshen Hausa ga xalibai masu nazari a fanni kimiyya da fasaha a manyan .makarantun sakandire

Rashin Samun Qwararrun Editocin Jaridu da Mujallu.

Ganin cewar jaridu da mujallu suna taka muhimmiyar rawa a wajen samar wa al'umma bayanai da suka shafi harkokin yau da kullum, kuma da dama suna xaukar jaridu da mujallu a matsayin wani ma'auni na gwajin sahihancin qa'idojin rubutun Hausa yana da kyau a samu etidoci waxanda suka qware a fannin qa'idojin rubutu, don ganin an kauce wa hargitsa-balle a cikin rubuce-rubucen jaridu da mujallun Hausa.

Wallafe-wallafe Kara Zube.

Akwai masu qoqarin yin wallafe-wallafe da harshen Hausa ta kowanne fanni, wannan ya taimaka wajen yaxa rubuce-rubuce marasa ma'ana, musamman

ta fuskar qa'idojin rubutu (Sa'id 2002:137). Akan sami wallafe-wallafe da dama da ba a samu sa albarkar wani masanin qa'idojin rubutu a cikinsu ba, illa dai kawai mawallafi ya rubuta abinsa, ya buga, yana sayarwa kawai don neman abin duniya. Irin waxannan wallafe-wallafe sun haxa da adabin kasuwar Kano da sauran litattafai na addini da na tallace-tallace da na kiwon lafiya, wani lokaci ma har da na gwamnatoci.

Rashin Samun Haxin Kan Malamai

Rashin samun daidaito na malamai ma wata matsala ce da rubutun Hausa yake fuskanta. A dukkan matakan ilimi tun daga firamare har zuwa matakin gaba da sakandire akan sami malamai da ba su yarda da ba su sani ba, don haka suke ganin duk abin da suka rubuta daidai ne, ba sai sun kai wa wani malami abokin aiki ya duba tare da ba su shawarwari ba.

Rashin Samun Sahihiyar Hanyar Koyar da Rubutun Hausa a Makarantu

Wata matsalar da ake samu ita ce ta rashin samun wata sahihiyar hanyar koyar da qa'idojin rubutu. A koyaushe aka zo koyar da wannan batu a makarantu, musamman na gaba da sakandire akan koyar da muhallin haxe kalma da rabaawa ne ba tare da rarrabewa a tsakanin rukunan nahawu ba bare faxin dalilan da suka sanya ake haxawa ko rabawa ba. Idan har za a cigaba da koya wa xalibai qa'idojin rubutu ta hanyar haxawa ko rabawa to kwalliya ba za ta biya kuxin sabulu ba.

5.4 Matakan Inganta Rubutun Hausa

Ganin akwai waxancan matsaloli da aka zayyaana a baya, waxanda su ne suke ci wa rubutun Hausa tuwo a qwarya, ake ganin ya kamata a sanu hanyoyin da za a magance ko shawo kansu. Daga cikin hanyoyin ko matakan akwai:

Samar da Qwararrun Malamai

Hanya ta farko ita ce ta samar da qwararrun malamai waxanda za su riqa koyar da qa'idojin rubutu a makarantu, musamman ganin cewar akwai malamai da

dama a matakai daban-daban na makarantu waxanda su kansu suna da matsala a game da qa'idojin rubutu ta yadda za a xauko gyare-gyaren tun daga qasa, wato tun daga matakin firamare da sakandire, su kuma xalibai su tashi da yin rubutun Hausa kamar yadda ya dace.

Samar da Wadatattun Na'urori Masu Rubuta Haruffan Hausa

Samar da na'urori na zamani domin yin rubuce-rubuce da kuma wallafe-wallafen rubutun Hausa za ya taimaka ainun wajen qara bunqasa harshen. Samar da tsarin rubutu irin na kwamfuta wadda yake yin gyara (auto correction) ga dukkan kalmomin da ba a rubuta su daidai ba zai taimaka wajen sauqaqa irin kwamacalar da ake samu a rubuce-rubuce, musamman waxanda suka shafi xab'i

Zama Don Bitar Qa'idojin Rubutu a kai-a kai.

Ganin cewar akwai matsaloli da dama da sukan taso a game da rubutun Hausa, akwai bukatar gudanar da tarurruka lokaci-lokaci domin bai wa masana damar warware matsalolin da suke tasowa a game da rubutun Hausa. Harshen Hausa harshe ne da yake bunqasa tare da tafiya daidai da zamani ashe akwai buqatar warware matsalolin da suke taso masa daga lokaci zuwa lokaci.

Samun Qwararrun Editocin Jaridu da Mujallu.

Samar da editocin da suka qware a rubutun Hausa zai qara rage yawan kurakuren da ake samu a rubutu na yau da kullum, domin kuwa al'umma da yawa suna xaukar jaridu da mujallu a matsayin wani ma'auni na awon sahihancin rubutun Hausa.

Kula da Wallafe-wallafe Kara Zube.

Akwai buqatar a samar da wata hukuma wadda za ta riqa bita tare da tace wallafe-wallafe, musamman ta fuskar bin qa'idojin rubutu, don tabbatar da ana yin rubutun yadda ya dace. Rashin irin wannan hukuma shi ne ya haifar da wallafe-wallafe kara zube ta yadda kowa sai ya rubuta abin da ya ga dama ya kuma yaxa

shi ga al'umma, wanda hakan ya haifar da ruxani a kan yadda ake yin rubutun Hausa.

Samun Haxin Kan Malamai

A nan ana magana a kan yadda malamai za su riqa aminta da junansu, sau da dama ana samun wasu malamai suna qin amincewa da abin da wani malami ya yi bayani, musamman ganin cewar matsayinsu guda ta fuskar matakin ilimi ko wanin wannan. Wannan matsala ce ta kawo buqatar a riqa yin zama don tattaunawa tare da cimma wata matsaya.

Samun Sahihiyar Hanyar Koyar da Rubutun Hausa a Makarantu

Ya kamata a samu wata sahihiyar hanyar koyar da qa'idojin rubutu. Idan har za a samu wata sahihiyar hanya to da xalibai za su iya fahimtar dalilan da suke sanya a raba ko a haxa kalma to da xalibai za su samu sauqin ahimtar batun. Amma idan ana koyarwa ta hanyar axar muhallin rabawa ko haxawa zai kasance xalibai na qoqarin hardace dokar a maimakon fahimtar ta.

5.5 Naxewa

A wannan babi an bayyana abin da wannan bincike ya gano waxanda suka haxa da dalilan da suke haddasa yin kwamacala a rubutun Hausa da matsalolin da rubutun Hausa yake fuskanta tare da hanyoyi ko matakan da za a xauka domin yin gyara ko inganta shi

BABI NA SHIDA

KAMMALAWA DA SHAWARWARI

6.0 Gabatarwa

Dangane da nazarin da ya gabata a wannan bincike muna iya qarfafa cewar akwai dalilai guda biyu waxanda suke haddasa kwamacala a rubutun Hausa. Na farko shi ne take sani. Wannan matsala ta shafi inda masu ilimi, musamman a harshen Hausa, suna yin rubutun a bisa kurakurai. Irin wannan matsala ce ake samu a littattafai na nazarin harshen Hausa, musamman fannin koyar da qa'idojin rubutu.

Dalili na biyu kuwa shi ne rashin sani, wato inda ake samun marubuta da ba su san kome a game da rubutun Hausa ba bare ma qa'idojinsa, amma suna yin rubuce-rubuce a harshen. Wannan ya haxa da rubuce-rubucen da ake yi a jikin katin gayyata da waxanda ake yi don sanarwa ko gargaxi (duba rataye na 12 da 13) da kuma wanda ake yi a jikin allunan talla inda akan bai wa waxanda ba Hausawa ba damar cin karensu babu babbaka (duba rataye na 8 da 15)

Manyan muhallan da ake yin kwamacalar dai guxa huxu ne:

- waxanda suka shafi haxe kalmomi
- waxanda suka shafi raba kalmomi

- yadda aka amfani da alamomi a cikin rubutu
- kurakuran da suka shafi yadda ake rubuta kalmomi

6.1 Kammalawa

Ta la'akari da bayanan da suka gabata, musamman babi na uku an bi diddigin samuwar rubutun Hausa da faxi-tashin da aka sha don sama masa qa'idoji da kuma irin gwagwarmayar da ya sha har ya kai matsayin da yake a yau. A babi na huxu kuwa an yi bayanin yadda qa'idojin rubutun Hausa suke da yadda ake sava amfani da su (wato yanayin kwamacalar da ake samu). Wannan bincike ya tabbatar da cewar ana yin kwamacala, wato rashin bin qa'idojin rubutu kamar yadda ya dace. Waxannan matsalolin sun kama tun daga yadda ake rubuta kalmomi da haxe kalmomi a maimakon rabawa da kuma rabawa a maimakon haxewa, sannan da rashin amfani da alamomin rubutu ta hanyar da ya dace.

Wannan aiki xaya ne daga cikin nazarce-nazarce da aka gudanar a game da jaridu da mujallu inda aka bibiyi diddigin kwamacala da ake samu a litattafai, musamman masu bayani a kan qa'idojin rubutu da jaridu da mujallu da allunan talla da abubuwan hawa da ma sauran rubuce-rubuce, da kuma dalilan da suka haifar da wannan kwamacala. A qoqarin cim ma wannan buri an bibiyi ayyukan da suka gabata masu dangantaka da wannan aiki da malamai masana da xalibai 'yan uwana suka gabatar a lokuta daban-daban. Bisa waxannan nazarce-nazarce ne aka xora wannan aiki. Gundarin aikin ya kalli wasu muhimman al'amura da suka shafi qa'idojin rubutun Hausa inda aka yi nazarin su xai-xai da xai-xai da nufin fito da kurakurai daban-daban da aka yi a waxannan kafafen yaxa labaru da ilimantar da

al’umma. Binciken daga qarshe ya nuna irin yadda matsalolin suke da kuma matakan da za a bi don ganin an warware ko shawo kansu.

Daga qarshe ana fata wannan aiki ya zaburar da masana da xalibai masu nazarin harshen Hausa, su xora a kai a kan nazarin jaridu da mujallu da ma sauran fannoni da suka shafi qa’idojin rubutun Hausa, musamman dangane da abin da ya shafi rubuce-rubucensu. Da fatan kuma wannan aiki ya zama sanadiyyar kawo gyare-gyare a waxancan kafafen isar da saqo (da ma wasun su).

6.2 Naxewa

Wannan aiki ya qunshi babi shida; a babi na farko an gabatar da maqasudin gudanar da bincike da muhimmancinsa da hasashen binciken da farfajiyar da za a gudanar da shi tare kuma da kawo hanyoyin gudanar da binciken. A babi na biyu kuwa an yi nazari ko waiwaye a kan ayyukan da suka gabata masu alaqa da wannan aiki domin tabbatar da ganin wannan aikin bai ci karo da wani da aka gudanar a baya ba tare kuma da samo muhimman bayanai da za su taimaka wajen gudanar da wannan aikin. A babi na uku an yi nazarin tarihin samuwar rubutu a qasar Hausa da kuma tarihin irin cigaban da ya samu ta fuskoki daban-daban irin su samuwar qa’idojinsa da kuma bunqasarsa. A babi na huxu ne aka gabatar da yanayin kwamacalar da ake samu inda aka gabatar da ire-iren kurakuran da ake samu ta fuskar rashin bin qa’idojin rubutun Hausa wanda shi ne aikin ya mayar da hankali a kansu wato a littattafai, musamman masu bayani a kan qa’idojin rubutu da jaridu da mujallu da allunan talla da ababen hawa da ma sauran rubuce-rubuce,. A babi na biyar an gabatar da abin da binciken ya gano tare da dalilan da suka haddasa hakan, sai a qarshe aka kawo shawarwari da kuma kammalawa, sannan aka kawo manazarta.

6.3 Shawarwari

Ganin irin bunqasar da harshen Hausa yake yi, musamman a wannan qarni, da kuma irin yaxuwar da yake samu ta fuskar masu amfani da shi a faxin duniya, akwai buqatar harshen ya tafi daidai da zamani kamar dai yadda sauran manyan harsuna na duniya irin su Larabci da Ingilishi da Faransanci da sauran makamantan su suke yi. Haka nan tun da yake jaridu da mujallu suna daga cikin manyan hanyoyin sadarwa na zamani da ake amfani da su a duniya, yana da kyau su ma su kasance suna bayar da sahihan bayanai, musamman ta amfani da rubutu kamar yadda ya dace, wato dai ta amfani da qa'idojinsa kamar yadda ya kamata.

Akwai buqatar qungiyoyin Nazarin Harshen Hausa da na Havaka shi su tashi tsaye don kare martabar harshen ta hanyar yin gangamin hana yin rubuce–rubuce kara zube, musamman a allunan talla, ba bisa qa'ida ba, tare da wayar wa gwamnatocin jihohi kai, musammam jihohin da Hausawa ne a cikinsu da su bai wa harshen Hausa da rubutunsa muhimmanci. A baya an sami wata jihar da ta kafa kwamitin ilimi, amma da kwamitin ya zauna don tattaunawa a game da sauran fannonin ilimi, sai mataimakin gwamnan jihar ya yi watsi da batun da aka kawo a game da harshen Hausa, a tunaninsa kowane Bahushe ba ya da matsala game da harshen. Da aka buqaci ya bambanta tsakanin 'Sama ta kai bakwai' da 'Sa mata kai bakwai' da 'Sa ma ta kai bakwai' a rubuce sai abin ya gagari Kundila. Don haka ya bayar da damar sanya batun harshen Hausa a cikin batutuwan da kwamitin za ya duba (Alhassan).

Sauran shawarwarin da wannan bincike yake bayarwa su ne: Akwai buqatar jaridu da mujallu su riqa ba editocinsu horo na musamman a game da yadda ake gudanar da rubutun Hausa da yadda ake amfani da qa'idojinta.

Qungiyoyin Nazarin Harshen Hausa da na Havaka shi su sanya ido a kan kamfanoni masu bayar da tallace-tallace a allunan talla da sauran hanyoyin talla a rubuce su tabbatar da ana rubuta abin da ya dace kamar yadda ya dace, wato ta amfani da qa'idojin rubutu yadda ya kamata ba kawai yin kwamacala ba.

A sanya koyon qa'idojin rubutu a manhajar makarantun sakandire ta yadda xalibai za su samu horo tun daga tushe a kan yadda ake bin qa'idojin rubutun Hausa.
Sanya wajibcin iya rubutun Hausa a bisa qa'ida a kan kowane xalibin jami'a kafin kammala karatunsa. Duk ya kasance jami'o'i su daina yaye xalibai waxanda ba su iya bin qa'idojin rubutun Hausa ba.

Masana su riqa zama duk bayan xan lokaci (kimanin shekara 5-10) don yin gyare-gyare ga baqin abubuwan da suka shafi harshen Hausa ta fuskar rubutu, da ma sauran al'amurra da suka shafi harshen Hausa.
Kafa wata hukuma wadda za a xora wa alhakin tace wallafe-wallafen da ake yi da harshen Hausa domin hana bazuwar wallafe-wallafe da ake yin su kara zube ba tare da kula da bin qa'idojin rubutu ba.

A samu haxin kan malamai, musamman manyan masana; kada ya kasace kowa yana da ra'ayinsa wanda ya sha bamban da na sauran masana tare da zama don cimma matsaya a kan duk wani al'amari da ya shafi harshe.

Duk da yake ana qoqarin samar wa rubutun Hausa tsarin rubutu a kwafuta, da ma sauran abubuwa na zamani kamar su wayoyin sadarwa da yanar sadarwa ta 'internet' da sauran makamantansu, akwai bukatar sanya hannun masana qa'idojin rubutun Hausa don ganin cewar tun ran gini, tun ran zane, wato ba a bar bixe baya ba.

Manazarta

Abubakar A.S (2010). *Yadda za a Faxaxa Fannonin Kimiyya da Qere-qere a Jaridu da Mujallu*. www.googlesearch.com.

Abdulmumini S.A. (2010). A Further Critique of the Use of Hausa in Advetising. *FAIS Journal of Humanities*. Kano: Bayero University.

Ado L.D da Rabeh H. (2008). *Sirrin Qa'idojin Rubutu na Hausa*. Katsina: Yussan Printers.

Amfani A.H. (2004). Four Decades of Language and Linguistic Studies in Hausa (1960-2000): *The Sixth Hausa International Conference*. Kano, Center for the Study of Nigerian Languages. Bayero University, Nigeria

Adamu U.A. (2004). Hausa and Information and Communication Technologies (ICTs). *The Sixth Hausa International Conference.* Kano, Center for the Study of Nigerian Languages. Bayero University, Nigeria

Almu M. (2004). Potentials of Developing Hausa Software And Its Advantages in Inproving Data Management And Information Technology. *The Sixth Hausa International Conference.* Kano ,Center for the Study of Nigerian Languages. Bayero University, Nigeria

Vatagarawa A.G. (2005). Ambiguity in Hausa Orthography: Study on Tone and Vowel Length. *Dundaye Journal of Hausa Studies vol 1, No 2.* Department of Nigerian Languages, Usmanu Danfodiyo University, Sokoto. Kaduna: Freedom Press.

Bargery G.P. (1934). *A Hausa-English Dictionary And English-Hausa Vocabulary*. London: Oxford University Press.

Bunza A.M. (2002). *Rubutun Hausa (Yadda yake da Yadda ake yin sa) Don Masu Koyo da Koyarwa*. Lagos: Ibrish Islamic Publications Centre Ltd.

Bunza A.M. (2005). *Arashi Shi Gogi Baqauye: Nazarin Karin Maganar Arashi da ke Jikin Motoci.* Takardar da aka Gabatar a Taron qara wa Juna Sani. Sakkwato Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Xanfodiyo.

Bunza A.M. (1990). *Nahawun Rubutu (Jagoran Qa'idojin Rubutun Hausa).* Association of Nigerian Language Teachers (ANLAT)

Bunza, U.A. (2009). Samuwa da Bunqsar Jaridu da Mujallun Hausa: Taqaitaccen Tsokaci. *Himma Journal of Contemporary Hausa Studies;* Katsina, Department of Nigerian Languages, Umaru Musa 'Yar'adua University.

Xangambo A. (1985). *Qa'dojin Rubutu a Hausa: Matattakala Zuwa ga Harshen Qasa*. Nazari a Kan Harshe da Adabi da Al'adu, Littafi na Uku. Kano, Jami'ar Bayero.

Daura H.K. (2008). *Dialectical Interference in Amana, A Yau And Gaskiya Ta Fi Kwabo News Papers*. M.A Thesis Department of African Languages And Culture, Ahmadu Bello University, Zaria.

Datti Z.S. (1984). *Salon Sarrafa Harshe a Jaridun Hausa.* Taron Qara wa Juna Sani na Malamai da Xalibai. Jami'ar Bayero, Kano

Dyson M.A. (1973). *The Relationship Between Word Frequency in Written And Spoken Hausa*. M.A Thesis. Kano: Bayero University.

Furniss G. (1991). *Second Level Hausa: Grammar in Action.* The School of Oriental and African Studies (University of London), London: Thornhaugh Street, Russell Square, WC1H 0XG

Galadanci M.K.M. (1976). *An Introduction to Hausa Grammar*. Zaria: Longman;

Gidan Dabino A.A. (2004). Ta Leqo Ta Koma: Jaridu da Mujallun Hausa Ina Mafita? *The Sixth Hausa International Conference.* Kano Center for the Study of Nigerian Languages. Bayero University, Nigeria

Guibi I.I. (2006). *Modern Information Technology An Assessment Of Hausa On Internet.* M.A Thesis Department o African Languages And Culture, Ahmadu Bello University, Zaria.

Hassan B. (2010). Some Common Errors in Hausa Writing. *Himma Journal of Hausa Studies*. Katsina Hausa Department, Umaru Musa 'Yar'adua University.

Institute of Education (1979). *Karatu da Rubutu a Harshen Hausa: Jagorar Qa'idojin Rubutun Hausa;* Zaria: Ahmadu Bello University.

Jaggar, J.P. (2001). *Hausa*. Amsterdam/Philadephia: John Benjamin Publishing Company.

Muhammad M.Y (2009). *Rubutun Hausa da Qa'idojinsa.* Zaria: Ahmadu Bello University Press Ltd.

Mukhtar, A.B. (2010). *Nazarin Harshen Hausa: Sigar Hatsin Bara*. Kano: Government Press.

Musa, R. (1988). *Hatsin Bara: Tasirin Kafofin Watsa Labarai Kan Al'adun Hausawa.* M.A Thesis Department of Nigerian Languages. Kano: Bayero University..

Newman, P. (2000). *The Hausa Language: An Encyclopedic Reference Grammar.* Yale University Press. New Haven & London.

Philips, J.E. (2004). *Hausa in the Twentieth Century: An Overview*. Sudanic Africa.

Sa'id B. (2002). *Qa'idojin Rubutun Hausa. Harsunan Nijeriya*, vol. xx . Centre for the Study of Nigerian Languages, Bayero University, Kano.

Sa'id B. (2004). *Qa'idojin Rubutun Hausa: Jagora ga Marubuta.* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Sani M.A.Z. (1999). Tsarin Sauti da Nahawun Hausa. Ibadan: University Press Limited

Smirnova, M.A. (1982). *The Hausa Language: A Descriptive Grammar*. Thetford Press Ltd, Thetford, Norfolk. Great Britain

Wurma, A.G. (2005). *Daidaitacciyar Hausa da Qa'idojin Rubutunta*. Kaduna: Olatunde Rasheed Publishing Works.

Yahaya, I. Y. (1988). *Hausa A Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce a Cikin Hausa*, Zaria: Northern Nigeria Publishing Company.

Yahaya, I.Y. (1982). *Towards the Perfection of Writing Systems: Examples From Hausa and English Orthographic Convention.* Harsunan Nijeriya xii. Center for the Study of Nigerian Languages. Bayero University, Kano, Nigeria.

Zahra D.S. (1986). *Jaridun Hausa Havakarsu da Gudummawarsu Kan Harshe da Al'adun Hausawa*. M.A Thesis Department of Nigerian Languages. Kano: Bayero University.

Zarruq R.M. (1982). *Tarihin Qa'idojin Rubutun Hausa.* Studies in Hausa Language, Literature and Culture: Proceedings of the Second Hausa International Conference. Kano Center for the Study of Nigerian Languages Bayero University

_____ (no date of publication) Aron Kalmomi. Unpublished Article.

http://en.wikipedia.org/wiki/History_of_writing

http://en.wikipedia.org/wiki/List_of_writing_systems

Chinese Writing (2009), Encyclopædia Britannica.*Encyclopædia Britannica, 2009 Ultimate Reference Suite.* Chicago: Encyclopædia Britannica.

http:// www.OOHinternational.com

Jaridun da aka yi amfani da su

Aminiya ta ranar Juma'a 27 ga Janairu, 2012
Aminiya ta ranar Juma'a 22-28 ga watan Maris, 2013
Aminiya ta ranar Juma'a 28 ga Janairu, 2011

Aminiya ta ranar Juma'a 19 ga Nuwamba, 2010
At-Tatbiq fitowa ta 189 ta ranar Juma'a 13 zuwa Juma'a 27 ga Mayu, 2011
At-tatbiq, fitowa ta 227, ranar Juma'a 11 zuwa 27 ga watan Janairu, 2013
Gamzaki ta ranar 27 ga watan Octoba zuwa 4 ga watan Nuwamba, 2006
Leadership Hausa ta ranar Juma'a 9-15 ga watan Maris, 2012
Leadership Hausa ta ranar Juma'a 26 ga Afirilu zuwa 2 ga Mayu, 2013
Leadership Hausa ta ranar Juma'a 2-8 ga Maris 2012
Rariya ta ranar 9-22 ga watan Maris, 2012

Mujallun da aka yi amfani da su

Dakin Kara, Fitowa ta biyu, Maris 2009
Xakin Kara, fitowa ta 3, Mayu 2009
Fim ta Nuwamba 2010, fitowa ta 130
Fim ta Janairu 2011, fitowa ta 133
Gani Da Ido, Maganin Tambaya ta watan Mayu, 2009
Kulawa ta watan Janairu/Faburairu 2005
Kunnen Gari, (in ka ji, kowa ya ji) Fitowa ta 1 ta watan Maris, 2012
Kunnen Gari, fitowa ta 3, Mayu 2012
Magama ta Ofishin Jakadancin Amirka A Nijeriya ta watan Maris/Afrilu 2013
Magama ta Ofishin Jakadancin Amirka A Nijeriya ta watan Janairu 2004
Magama ta Ofishin Jekadancin Amirka a Nijeriya (Sifili na 17, lamba ta 2. Yuli 2011
Muryar Arewa, fitowa ta 8 ga watan, Maris 2012
Sautus Sunnah juzu'i na 2 fitowa ta 1, Mayu 2001

Hira

Dr. B.S.Y. AL-Hassan, Sashen Harsuna da Al'adun Afirika, Jami'ar Ahmadu Bello , Zaria. (24/6/2013)